💫 KYAWUNA JARABTA TA💫

✍️M SHAKUR

DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAIJINKAI.

LITTAFIN NAN NAKUDI NE BUT FOR NOW INA FREE PAGE SO U ALL CAN SHARE. subscription is 500 idan kinaso kibiya nasaki a group zaki turo 500 into 3107021073 aisha Muhammad first bank saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461 sainai adding naki a group din danake posting.

S-SQAURE FASHION AND MORE GIDANE NA HIJABAI DA HADADDUN DOGAYEN RIGUNA NA DINKAWA, KUNSAN MA MENENE TANA WANI PROMO NA FREE DELIVERY KOWANI GARI KIKE IDAN KIKASAI KAYANSU ZATA AIKOMIKI DA KAYAN KYAUTA, DON MAGANA DA ITA KO CHATTING NATA UP DAN SAYAN KAYAYYAKIN SU CLICK ON THIS LINK wa.me/+2347030037697

Free page
EPISODE1️⃣

Tudun Yola, Kano!
Baban Anguwace kuma sabuwa dan babu mutane haka sosai a anguwan, saidai irinsu uncompleted building da ake kan ginawa dakuma sababbin gidaje da ba'a dade da tarewa cikiba.

Baban gidane dayasha fenti milk color, kana ganin ginin gidan kaga ginin irin family house dinan,  tsakar gidan mai bala'in fadi, ga katuwar bishiyan mangwaro a tsakar gidan datai y'ay'a sosai dudda basu nunaba, flat biyune agidan wani babban dankareren flat saikuma wani karamin flat mai kamada boys quarters agefenshi, gidan kana ganinshi kasan bawani gidan mai bala'in kudi bane gidan rufin asiri ne dai namai karfi daidai, motoci biyune parke atsakar gidan wata bus mai kyan gaske milk color saikuma mota sienna ash da mai gadi ke wankewa ga dukkan alamu motar maigida ne sabida yanda ya kuke yana wanketa yanabin wakan sangaya dake tashi a karamin radio daya ijiye kan plastic chair.

Bude kofar karamin flat din dake kusada babban flat din akayi, wani Matashi ne baki dogo baida jiki sosai yana sanye da jallabiya brown hannunshi rikeda makullin mota yafito, takalmi yasaka sanan yasauko daga matattakalan bakin kofarsu  yadumfaro babban flat din, da sallama yabude kofa ya shiga ciki.
Babban falo dakeda girman gaske, wani Babban Magidanci ne zaune akan kujera akalla zaiyi 60years kokuma 59, kana ganinshi kaga mai gidan, bakine yanada jiki, hannunshi rikeda jarida dayake budewa yana karantawa.

gefenshi kuma wata Mata ce mai kiba Hajiya Balaraba akalla zatai 40yrs tasaka wani hadadden lace tana kurban shayi a cup, saiga yara dasuke zazzaune akasan carpet suna breakfast kowanne nashan tea da bread da soyayyan egg dinshi, Mata uku ne a tsakar falon da maza biyu wanda duk kasansu daya, Amal that is 14, sai Asiya 13yrs, sai Aneela dakenan 11, Mazan kuma Muhammad dakenan 11 sai Mudasir wanda shine autan gidan 6yrs, gabaki dayan yaran kana ganinsu kaga mahaifinsu tundaga bakin fatar da jikin dan dukansu tuluka tuluka dasu very fat gwanin ban sha'awa kana ganinsu kasan sunacin lafiyayyen abinci, dukansu suna sanyeda uniform din makaranta da alamu hadda zasu danyau sunday.

Kitchen aka bude, wata black beauty Matace dan itama ba yarinya bace akalla zatai 38yrs tafito tana sanyeda doguwan rigan atampa mai kyau da akama stonework tana rikeda tray dawasu hadaddun kwanuka ke kai, hada ido tayi da wanda ya shigo dakin dukbasu luradashi ba yasa tace "this children zasusa kayi latti for your program Ya Hamad" kiran sunan shi datayi yasa duka yaran dakowama na falo yadagokai ya kallai, atare duka yaran suka gaidashi "Ya Hamad good morning" batare daya amsasu ba yakarasa shiga falon har gaban Abba yakarasa sanan yazauna agefenshi yace "ina kwana Abba" sanan yakalli matar dake gefenshi yace "Ina kwana Mum" daidai lokacin dayan matar taja coffee table zuwa gaban mijin nasu ta dauramai tray akai tace "your food is ready Daddy Hamad" jaridan ya linke tareda mikamata, karba tayi dayan matan tadauke kai Abba kuma yatura hannu a aljihun sanan yaciro wasu kudi yamikama Hamad yace "inka kaisu kabiya musu kudin makaranta" sanan yajuya yakalli matar dake gefenshi yace "me yaran nan sukeyi asama har yanzu basusan zasu makaranta bane"? dasauri tace "kumafa su tuntuni sukai break, Nanaa, Hawwa" daga chan sama aka amsa, wasu yan mata manya masu jiki guda biyune suka sauko daga stairs, yaran zaka dauka yan biyu ne dan suna kama, irin kama na jini dinnan, Nana itace Babba 26yrs take tana final year a BUK tana karanta Mass Com, sai Hawwa 24yrs tana 300level tana karanta international relation itama a Ado Bayero, Hawwa na kama da Hamad sosai, dukansu suna sanyeda lemon green hijabi na haddan, dukansu ransu abace yake dan sun tsani zuwa hadda suna uni amman suna wani zuwa hadda shikuma Babansu yanuna babu wacce ta isa tabar hadda cikinsu kodako PHD sukeyi, tashi duka yaran sukayi sukama iyayensu bye suka fice, sanan Ya Hamad din yatashi yace "bari nakaisu Abba" gyadamai kai kawai yayi dan haka Babansu yake baifiye son magana ba, sanan yawuce yafice.
Kaman ance tadaga kanta sama taga gittawan mutum dasauri an bude  kofa anshige daki

batare da an bari sun hada ido da Mami ba. Ahankali Mami tasauke ijiyan zuciya dudda bataga fuskanba but ko amafarki aka tadata tasan waye.

Duk suna zaune afalon harya gamacin dumamen tuwon yadauki ruwa yasha, Dan gyaran murya matan dake zaune kusada shi tayi Mum tace "Alhaji nace bari namaka tuni, kaga duka duka bikin Nana bayan Babban salla da sati uku ne, gashi lokaci nata matsowa yanzu baifi wata daya bikin ba, nasan dama kariga kabada kudin kayan daki, cha kayi daman wanan satin zakaban kudin kayan kitchen, kaga idan kabani nida Zainab saimu shiga kasuwa yau muyo siyayyan koya kika gani Zainab"? Mum tama Mami dake zaune tana sauraransu magana, gyadamata kai tayi sanan tace "eh hakane Abban Hamad" ruwa yadauka a cup yakara kaiwa baki yasha sanan ya ijiye cup din, hannu yasa a aljihu yaciro bandir din yan dubu daya guda biyu yabata yace "kinemi wata kijeda ita  kasuwa, Zainab bazata iya zuwa ba itakeda girki, kuma yau lahadi ina gida" yana fadin haka yatashi yawuce sama duk suka bishi da kallo, saida taga yashiga dakinshi sanan tabata rai tace "Alhaji Alhaji bantaba ganin kafaffen mutum irin shiba wlh" tashi tayi batare data kalli Mami ba tai stairs tabude bangaren ta tashige dan saman bangare  biyune nata dana Zainab saikuma dakunan yaransu guda uku, na maza kanana dana mata kanana saikuma na yan matan suma dakinsu daban.

Ahankali Mami ta tashi ta tattare duka kwanukan takai kitchen sanan tasa Mai aikinsu Uwani tazo tashare falon ta kunna turare sanan tai sama itama bude dakin mijin nata tayi tashiga bata wani dade aciki ba sanan tafito, direct dakin yan matan tayi ahankali tabude kofar, dakin nada dan fadi gashi a gyare Kal Kal, gadaje ne guda uku irin nayan boarding jere adakin kowanne da bangaren nashi saiga wardrobe na bango da kayan kowa keciki, bin kan gadajen tayi da kallo ganin babu kowa kai yasa takarasa shigowa dakin tareda maida kofan tarufo sanan tashigo ciki takaraso tsakiyan dakin saikuma ta tsaya turus tai shiru tana kallon gaban gadon dake tsakiyan dakin, wata faran budurwan yarinyace azaune akasa tabama dakin baya tana kallon bango tadaura kanta kan kafafuwanta ta, nimai rubutu M Shakur banmasan mutum bane awurin ba saida naga Mami ta tsaya turus tana kallon wajen, wani irin silk black gashin kaman na yar India ne zube awajen yana taba tiles din kasan daki sabida yanayin zaman datayi tsabagen tsayin gashin, sai farin kafanta sol mai bala'in kyau da dogayen fararen farcenta dababu komi akai sai uban haske kaman ana wankesu da madara. "Du'a" jin ankira sunanta yasa tadago kanta daga kifen dasuke akan kafafunta dasauri batare data waigoba jin muryan Mamin ta, dan Jim Mami tayi tana binta da kallo sanan  asanyaye tace "inkin gama kukan ki tashi ki tattare gashin nan naki ki kulle kisa a hijabi kije Abban ki nakiranki yana dakin shi" tana maganan tawuce tafice daga dakin tarufo musu kofan.

Ahankali takai fararen hannuwanta tashare fuskanta sanan tamike tsaye ahankali, wani iri mahaukacin cokacola shape Allah yamata gawani irin pointed curvy ass gareta daya fito sosai cikin doguwan rigan material din dake jikinta, itama kaman sauran yaran gidan tanada dan jiki danbazaka taba kiranta da mara kiba ba amman batakai su Nana kibaba, saidai tafisu diri, ga gashin kanta dabaida banbanci dana yan India har waist dinta, juyowa tayi ahankali TSARKI YA TABBATA GA ALLAH SUBHANAHU WATA'ALA WANDA YA HALLICI SAMAI DA KASSAI DAKUMA HALITTUN DAKE CIKINTA!!!! yarinyar nan koda ace itace tayi kanta banjin zatai kanta tai kyan datake dashi yanzu hakaba dan My Lord!!! dan itace definition of tacika goma cip cip tamakai sha uku, farace Kal fuskanta babu pimple ko daya idanunta sun kumbura sunyi ja sabida kukan datayi wanda haryau takasa sabawa dan by now yakamata ace tasaba duk sanda yan uwan ta zasu makaranta boko ko islamiyya saitai kuka, tanada wani irin long pointed hanci ga pink lips, gashin idanunta dogaye kuma acike sun jikeda ruwa, ga kirjinta awani irin cike kaman wacce taje tai surgery ga flat tummy kaman bata tabacin abinci ba, Allah yamata ass amman waist dinta kona jariri albarka her waist is so tiny, ahankali take tafiya har zuwa gaban madubin dakinsu ribbon dinta dake wajen tadauka sanan ta kulle kanta da kyar sanan tashiga bayinsu wanko fuskanta tayi tafito tadauki dogon hijabin ta maroon tasaka tafito daga dakin ahankali.

Cikin wata irin siririyan cool melodious voice tai sallama gaban dakin Abban su, daga ciki taji yace "shigo" ahankali tabude kofa tashiga kanta akasa, yana zaune kan couch din dake dakin yabita da kallo tazo gabanshi tazauna tareda saukar da kanta kasa ahankali tace "Abba gani" zama ya gyara tareda bude Al Qur'ani dake kan cinyanshi sanan yace "biyomin haddanki" gyara zama tayi sanan tafara rairomai suratul Yusuf shafa'i ukun dayabiya mata last week, shi karan kanshi  idan tana biyamai hadda baiso tadena dan muryanta Allah yay mata dadi saida tagama tsaf sanan yakara mata wasu shafa'i ukun kafin yamata tajweed sanan yace "tashi kitafi" tashi tayi ahankali tai hanyar kofa yasake binta da kallo harta daura hannunta kan handle din kofa taji yakirata anatse. "Du'a" dasauri tajuyoda kanta ta kalleshi saikuma tasauke idanunta kasa tace "na'am Abba" ahankali yace "nariga nasaman miki wata sabuwar malama, daga gobe zata fara zuwa In sha Allah, ki shirya" gyadamai kai tayi sanan tajuya zata bude kofan saikuma tajuyo ahankali batare data budeba ta kalleshi hada ido sukayi hakan yasa takasa magana tajuya zata bude kofan tafice cikin muryan nan nashi nabawasa yace "mekikeso ki fada"? Dan juyowa tayi ta kalleshi saikuma tasauke kanta kasa kirjinta na bugawa fat fat tashiga wasa da yatsunta tsabagen how nervous she was tama kasa magana, dan idan Abban su yakureka da ido zamaka iya fitsari ajiki baka saniba, shifa kokadan baida wasa kuma yanada zafi sosai, gashi kaifi daya saisa duka yaranshi ke tsoron shi. Ganin takasa magana yasa yace "I'm listening" rawa sosai muryanta yafara tanama bude baki maganan yakasa fitowa saikuma tasaki hannunta ta shiga chakuda hijabinta da hannu duk yana binta da kallo hijabin tarike gamgam sanan da kyar tasamu maganan yafito ahankali tace "Ab.....ba ni......maisa ake barina agida kahanani fita kowaje, Abba ni nafison naje school kaman su Ya Nana......" saikuma tasake hadiye wani irin dry miyau hawaye yawani zubo daga idanunta suka sauka akan hijabinta cikin wata irin murya na wacce ke gabda fashewa da kuka kuma take a bala'in tsorace  tace "Ab....ba

ni maisa baka sona kaman yanda kake son su Ya Nana da Hawwa da....d....." Du'a!! taji anwani irin kirata da kakkausar murya dayasa tadaga kanta da sauri ta kalli inda taji muryan,  Mami ce tafito daga bedroom din Abba da alamu tuntuni take ciki maybe gyaramai dakin take dan taga karamin rag na goge goge a hannunta, cikin wani irin tsananin bacin rai tace "Du'a are you questioning your father? eh? mahaifin ki kika tasa agaba kina tuhuma haka?" girgixa mata kai tayi dasauri saikuma tasaki kuka dasauri tajuya tabude kofa tafita daga dakin dagudunta.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍M SHAKUR

UMMI COLLECTION is a whole world of turaruka, both na wuta dana feshi, exquisite burners na electric dana charcoal, and oils, turarukan wanka da sauran su. kunkosan kwanan nan UMMI COLLECTION na promo free delivery, hehehe banso kuyi missing this mad offer just click on this link danyin magana da ita directly.
wa.me/+2348186968736

free page
EPISODE2️⃣
Azuciye Mami ta jefar da rag din dake hannunta tace "nikema yarinyar nan magana tafice tabarni sabida batada kunya Dadyn Hamad" tataho cikeda bacin rai zatai wajen kofa tabita Abba dake kallonta tunda tafara masifan yace "ina zaki"? Turus ta tsaya tana kallonshi takasa koda motsi, anatse yanuna mata bedroom dinshi yace "koma kicigaba da abinda kikeyi" dasauri tace "but......" "no buts ki koma kicigaba da abinda kikeyi nace" yay maganan babu alamun wasa akan fuskanshi hakan yasa bata karacewa komiba tawuce takoma ciki ranta abace, jaridanshi yabude ahankali yacigaba da karantawa bazaka gane takamaimen wani yanayi yake cikiba dan fuskanshi bata nunawa.

Dakinsu tabude dagudu tashiga tafada kan gado tana kuka sosai, tayi kuka nakusan awa daya sanan bacci yay awon gabada ita akan gadon.
Hayaniya yatadata daga baccin datakeyi, bude idanunta tayi ahankali saikuma ta yunkura ta tashi zaune tana kallon dakin nasu, Nana da Hawwa ne  kecire kayan jikinsu sundawo daga hadda duk sunyi zufa, ahankali tace “Ya Nana kundawo daga makaranta” danjuyowa Nana tayi takalleta  tana kokarin daukan zanin dazata daura tashiga wanka tace “eh yanzu muka

shigo”"sannu da zuwa" tafadi ahankali sanan tajuyo da kanta Hawwa ta kalla taga Hawwa tadauke kai dasauri tana batarai, daidai lokacin aka bude kofan dakinsu, Aneela ce tashigo wacce take kanwarta, dan Du’a ce yar Mami tafarko, sai Aneela, sai Muhammad da Mudasir su Hudu Mami ta haifa, itakuma Mum itace mahaifiyar su Hammad, Nana, Hawwa, Amal, da Asiya yaranta biyar.

Ko kadan Aneel bata kama da Du’a inba ma angayamaka ba bazaka zaci uwarsu dayaba dan tafi kamadasu Nana black beauty ce itama, kyakkyawan yarinya bakutu da ita, zama tayi kan gadon takalli yayartata tace “yauma saida kika kara kuka sabida muntafi makaranta banda keko” Hawwa data zauna kan gadonta tana ciro wayanta daga jaka tana kunnawa tace “asheko xakita kuka har karshen rayuwanki dan Abba yace konan da gate bazaki taba fitaba” turo baki Aneela tayi cikeda rashin kunya ta kalli yayartata saikuma takai hannunta tadaura kan kumatunta tace “karki kara kuka kinji Duudo, kinga ko yau Malam yafassara mana wata aya yace duk wanda yadogara ga Allah to hakika Allah ya isar masa, ki dogara ga Allah and I promise you Allah will be there for you, kiyita addu’a zakiga Abba zai chanza zaice kema kifara zuwa school kaman mu kinji” gyadama kanwar tata kai tayi ahankali, Aneela tawani washe baki tai murmushi hakan yasa itama tai murmushi, Subhanallah idan tai murmushi numfashinka zai iya tsayawa sabida kyan datake karayi.

“In dauko mana abinci muci tare?” Aneela ta tambaye ta, Gyadamata kai tayi hakan yasa tasauka daga gadon tawuce tafita, itakuma ta sauka daga gadon ahankali sanan tawuce bathroom dinsu dan dauro alwala Hawwa tabita da harara wanda inda sabo tasaba tun suna yara basa shiri sabida sako da sako nesu dan daga Hawwa sai ita aka haifa agidan, itakuma Nana babu ruwanta bata shiga harkanta as per babban yaya in the house.

Fitowa tayi ta shimfida dadduma tadau hijabi tasaka ta kabbarta salla daidai lokacin Aneela tashigo ajiye musu rice da stew din tayi akan gado itama tazauna tana jiranta ta idar, itakuma Hawwa ta tashi tafita duk ranta abace yake sabida yanda tadawo Mum dinsu batanan.

Saida ta idar da sallan sanan tazauna sukaci abincin tareda Aneela batare dasunyi surutu ba sabida Nana dake waya da wanda zata aura, sosai taci abincin suka gama tass Aneela tafita da plate din takai kitchen sanan tasake dawowa dakin.

Wuraren 4 Mum tadawo daga kasuwa da mota guda na kayan kitchen yaran sai murnan ganinta suke barinma yaranta dakin da ake tarin kayanta akakai komi bayan Abba yagani sanan daga ita har Mami suka shiga kitchen sukahau girke girke sabida bakin da Abba zaiyi yan wajen aikinshi da iyalansu, yaranma duk aka kirasu kitchen banda Du'a dakenan ita kadai adaki.

Tana zaune adakinsu har magrib ita kadai, dan tun dazu aka kira Aneela da Nana da Hawwa duka batasan me akayiba but tadaiji kamshin girke girke kuma yawanci tasan ana irin girkunan nan ne idan zasuyi baki, tashi tayi ahankali ta shiga bayi wanka tayo tareda dauro alwala tafito daidai lokacin da Nana da Hawwa sun shigo dakin duksunyi zufa, dasauri tace “Ya Nana mekukeyi?” “Girki” tabata amsa atakaice tawuce tashiga bayi dan wanka itakuma Hawwa tazauna akan gado tana daukan wayanta tana dubawa ko ankirata, gaban wardrobe dinsu taje tabude bangaren kayanta, wani doguwan rigan atampa black taciro tawarware sanan tasaka dayamata kyau sosai sanan tadauki hijabi tajuyo hada ido tayida Hawwa dake kallonta suna hada ido tadauke kai tacigaba da danne dannen wayanta, saka hijabin tayi tahaukan dadduma tafara salla daidai lokacin Nana tafito daga bayin ta kalli Hawwa tace “tashi kije kiyi wanka Hawwa kinga Abba yace mu shirya dawuri suna hanya fa” tashi Hawwan tayi tashiga bayi itakuma Nana tashiga shiryawa cikin wata atampa.

Idar da sallan tayi ta tashi tazauna akan gadonta tareda cire hijabin ta ijiye agefenta tana kallon yanda duk suke shiryawa agurguje, suna makeup abin na bata sha'awa dan ita mai kadai na shafawa gareta sai body spray, batada sauran kayan kwalliyan dasuke dashi kuma bata isa ta taba abinsu ba barinma masifaffiyan Hawwa nan. Daga Hawwan har Nana saka atampopi sukayi iri daya suka shirya tsaf gwanin ban sha'awa sanan kowacce ta zauna kan gado tana danna waya, sosai take kallon wayan dasuke dannawa, duk idan taga suna tabawa saita bata shaawa kaman taje ta karba amman tasan bazama su bataba, duk suna zaune ahaka kowa nawasa da wayanshi banda ita dake kallonsu kaman tasamu film aka bude kofa dasauri duk suka daga kansu suka kalli kofan, Abba ne yasaka lafiyayyan shadda mai ruwan toka da hula akanshi yana tsaye daga bakin kofa batare daya shigoba yakalli su Nana yace “kufito kugaida Abokan aikina da matansu” yana maganan yasaki kofan yay gaba duk tashi sukayi harda ita cikeda wani irin murna koba komi yau zataga wayanda bayan gidansu ba, hijabinta tadauka tasaka sanan tabi bayansu  Nana dasukai gaba batareda sun cemata komiba suka fito Abba na tsaye kan stairs yana jiransu su fito yagansu, hada ido yayi da Du’a dake nonnoke kai, ahankali yace “ke banda ke koma daki ki zauna” wani irin murmushi Hawwa tayi ranta fess jin ankorata, Gyadama Abba kai tayi ahankali cikeda mugun sanyin jiki tajuya ahankali tashiga daki tareda maida kofan tarufo daidai lokacin Hamad yafito daga dakin Mum dinshi, hada ido Abba yayi dashi yace “let’s go tunda kafito” shida Abba suka jera yaran kuma abayanshi har zuwa kasa.

Abokanen aikinshi ne su uku da matayensu da yaransu kanana  suna ganinshi Babban cikinsu yace “what a nice family kakedashi HOD” dan murmushi Abba yayi yakaraso wajen yabasu hannu sukuma yaran suka shiga gaida kowa, Mami da Mum da Uwani suka shiga kawo abinci da kayan kwalama, ahankali Mami kebin kowa na falon da kallo saikuma tasauke ijiyan zuciya ahankali, daya daga cikinsu yace “wayan nanne kadai yaranka HOD”? Gyadamai kai yayi yace “eh” ahankali Mami dake kokarin bama matar abokinshi plate na snack tadan saci kallonshi saikuma tai murmushi tacigaba da serving while Abba yacigaba da magana yanuna Hamad yace “wanan shine first son dina Hamad he’s 30, yakaranta engineering” dasauri bakin sukace “like father like son” danshima engineering yayi yanzu shine HOD engineering department a BUK, murmushi yayi yace “yayi joining NDA yanzuma wani program yakeyi anan kano saisa

yakenan, sai Aisha” yanuna Nana yace “muna kiranta da Nana dan tanada sunan Mamana, ankusa bikinta nan da bayan salla, sai Hawwa sai Du….” Shiru yayi dasauri saiya nuna Amal yace “sai Amal, Aneela, Asiya da Muhammad da Mudasir, yarana takwas” “wow masha Allah, nice family wlh, Allah ya rayamaka su kaga aurensu” murmushi Abba yayi yace “Bismillan ku mufaracin abinci” nan aka shiga cin abinci akai shiru, ahankali Hamad yatashi yay excusing kanshi yay sama binshi da kallo mahaifiyarshi tayi babu daman kiranshi sabida bakin dake wajen.

Dakinsu Du’a yabude yashiga tareda maida kofan yarufe sanan yajuyo ya kalli gadonta, a kwance yaganta tarufa da hijabinta, ajiyan zuciya yasauke aboye sanan yashigo dakin yace “Hey Duudo look what i got for you” shiru tayi kaman tana bacci taki motsi, ahankali yasa hannunshi yakama kafafunta yadagasu sama sanan yazauna abakin gadon sanan yasaukar da kafafunta kasan gadon tareda saka hannu yaja hijabin data rufe fuskanta dashi, dasauri ta yunkura zata juya fuskanta kawai yadagota yace “come here Du’a” sata yayi ajikinshi kaman jira take ta kankameshi sosai sai kuka, ko kadan baiyi attempting hanata kukan ba, duk kanninshi babu wanda yakejin tausayinta yake kuma so kaman Du’a sabida tafi kowa rauni, he don’t care about kalaman da family su suke fadi akanta ana cewa itaba yar Abba bace, mayya ce, yar aljanu ce bla bla bla, all he knows is Mami da Abba suka haifeta and she’s his little sister kuma yanason kanwarshi sama da tunanin kowama.

Cikin kuka tace “Ya Hamad ni wlh inaso namutu” dasauri yacirota daga jikinshi yace “ke are you crazy? Karki kara fadin haka” bayan hannunta takai tana share fuskanta tace “Abba bayasona, Mami bata sona, Mum ma batasona, Kaka ma batasona, kaga ni kadai Abba ya tsana ayaranshi, yakorani nakoma daki dazu, kuma kaga yace yaranshi 8 yacireni daga cikin yaranshi, kullum ina kulle adakin nan kaman mayya, dama Kaka tace ni mayya ce ni aljana ce, sabida ni kadai aka haifa daban bana kama daku does that means am a witch ko aljana eh Ya Hamad? Ya Hamad bakacemin kananan ranan da aka haifeni ba kuma kace Mami ta haifeni maisa su Aneela dasu Muhammad da Mudasir kadai takeso eh? Ya Hamad babu asibitin dake chanza kalan fatan mutum ka kaini naje nakoma kalan yan gidan mu sabida Mami na da Abba su soni nima eh Ya……..” hannunshi yadaura akan lips dinta yace “ya isa haka listen to me all abubuwan nan dakikaga Abba da Mami nayi bawaidan basa sonki bane sunayine to protect you, Du’a tun kina primary school ansha ayi attempting ayi raping naki nasan lokacin kina yarinya ba lallai kituna ba, but kin tuna lokacin dakike JSS 2 abinda teacher ki da Abba ya kulle yamiki ko” runtse idanunta tayi dakarfi alamun ta tuna, hakan yasa ahankali yakai hannunshi yakama hannuwanta guda biyu yace “listen to me, Abba is only trying to protect you, Abba bai tsaneki ba” ahankali cikeda raunin murya tace “amman yana kunyan ya nunani amatsayin Babana” tai maganan tana kallon Ya Hamad kurii da manyan idanuwanta dayasa yakasama mata karya dan to some extend all abinda take fadi gaskiyane, ahankali kawai yajawota jikinshi ya rungumeta yakai hannunshi yashafa gashinta murya chan kasa ta yanda dagashi sai ita sukeji yace “kin tuna abinda nake yawan fadamiki” gyadamai kai tayi ahankali ajikinshi hakan

yasa yace “fada inji” murya chan kasa hawaye nabin kuncinta tace “Du’a kome kikaga yana faruwa arayuwanki Allah yasan dake, jarabawanki ne, karki kaucema Allah karki butulcemai, bake kikai kanki ba Allah ya yoki, love yourself, kiyi imani da Allah kikuma dage da addu’a watarana sai labari my beautiful little Duuudo” suka karashe maganan atare hakan yasa takara kankameshi, murmushi yayi sanan yacirota daga jikinshi, handkerchief yaciro daga aljihunshi yace “now let’s wipe those tears no more kuka okay” gyadamai kai tayi tareda murmushi yan kananun white teeth dinta suka bayyana, sharemata fuskan yayi tass sanan shima yamata murmushi yace “idan bakin nan suka tafi zan dauko miki sababbin novels din dana sayomiki kinji” gyadamai kai tasakeyi, kumatunta yaja yace “idan kika sake kuka saimun bata” dasauri tace “bazan sakeba” “kinci abincin dare?” Girgizamal kai tayi, tashi yayi yace “bari naje nakawo miki saiki bani labarin wayan nan novel din” gyadamai kai tayi yawuce yafita yana murmushi, Allah yamata brain, english novels yake sayomata dasukakai 1000+ pages cikin 2days tagama kuma tsaf zata bashi labarin novel din, abinda yataimaka mata da english ma kenan.

Bai wani dadeba yadawo dakin da bowl na hadadden pepper soup da cow head, kafinma ya iso ta tashi tsaye dasauri tace “Ya Hanad kaman pepper soup ko” bata plate din yayi yace “mayyan nama kawai” dan tana balain son nama tun tana yarinya, murmushi tayi takarba dasauri tazauna tashiga ci ya tsaya shikuma yana kallonta, she looks so happy hakan made him so happy, dan yarinya ce da dawuya kaga she’s happy saisa anytime she looks happy happiness dinta is infectious sai kawai kaji kaima ka kamu da farin ciki. Juyowa tayi takallai tana tana naman kaman wata yar baby looking so adorable ganin ita yake kallo yasa tamikamai last piece na meat din tace “zakaci” hararanta yayi yace “marowaciya sai yanzu zaki bani to banci” dan dariya tayi tace “yakuri bari naci wanan gobe saimuci tare, Ya wai yaya ake dafa nama ne”? “Har yanzu ba’a barinki ki shiga kitchen?” Gyadamai kai tayi tace “ba Kaka tahana ba” gudun karta tunakomi dan yanzun nan kuma tahau kuka tasa yace “zan sayo nama saina koyamiki a kitchen din side dina” sosai tashiga jin dadi tana tauna namanta bude kofa akayi dasauri dukansu suka waiga, Mum ce fuskarta amurtuke, wani mugun kallo tama Hamad tace “mena gayamaka? Zokabar dakin nan” tai maganan tareda nunamai kofa, tashi yayi ahankali batare dayamata gaddama ba yazo yabita gefenta yafice, shigowa dakin tayi tazo har gaban gadon Du’a data sauke kanta kasa tana rikeda bowl din pepper soup din data cinye tace “ke bazakiji da bakin jinin ki kinemi yanda zakiyi ubanki yama yarda cewa ke yarshi ce ko yadinga lissafawa dake cikin yaranshi kina nan kina nema kisama dana bakin jininki ne, sabida kinga yanda ubanku keji dashi first son dinshi ga ilimi ga kyau shine zaki biyo tanan, to ta Allah batakiba bakar mayya kawai, kijechan kiji da kanki, na tsani uwarki amman naga matsalan da haihuwanki kesata ciki wlh har tausayamata nake, wayama sani ko wani aljaninne yadura mata cikinki dan naji ance tayi aljanu datana gida da kyar namijin dare yamabarta tai aure” ahankali tashare hawayen daya zubomata sharr babu abinda ta tsana irin adinga kiranta da yar aljanu ko mayu, Mum tasake wurgamata mugun kallo tace “wawiya dakikiya kawai babu abinda tasani sai zaman daki, kannenta ma sunfita iya karatu sunfiki iya komi Babanki yamaidake gidahuma yaryar aljanu kawai” wanan karan fashewa da kuka tayi sosai takai hannunta tadaura kan fuskanta tana kuka, murya chan kasa ta yanda Baza ajiba tace “niba yar aljanu bace” da sauri Mum dake tsaye kanta tace “me kikace Du’a? Mayarmin da magana kikayi? Did you just talk

back at me eh?”.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

Don yin magana directly da M Shakur click on this link wa.me/+2347012181461
M Shakur nada group din Matan Aure wanda idan kinason kishiga is just 1k.
hakama idan kinason advert shima M Shakur duk tanayi.

free page
EPISODE3️⃣
Girgizamatakai tayi ahankali gwaninban tausayi alamun bada ita takeba, cikeda mugun tsana tace "haka zaki kare rayuwanki awanan dakin, agabanki yayyinki da kannenki duk zasuyi aure ke kina nan adakinnan har tsufa bazakiyi aureba saidai ko indaga dangin ubanki aljanune wasu zasuzo kuyi wup dake, mai bakin jini kawai mara kunya" tana maganan tawuce tafice daga dakin, sosai tafashe da kuka, har bakin suka tafi su Nana suka dawo dakin nan kuka take bata denaba, dayake sun saba bawai sabon abubane kukantaba saisaima babuma wanda yabita kanta saima shirin kwanciya dasuka shigayi suka gama Hawwa takashe wutan dakin, haka taci kukan nan har batasan sanda bacci yay awon gaba da itaba.

Yau Monday sabida taci kuka batai bacci dawuri ba sai wuraren 8 ta farka, koda ta tashi babu kowa adakin saidai sababbin novels datagani manya guda uku agefenta dasauri ta tashi zaune ta dauka tana dubawa, sunan Novel din farkon The Noisy Naigbour, na biyun sunanshi the killer tree, saina ukun Disastrous Love, wani kalan murmushi tayi sanan ahankali tace "thank you Ya Hamad" ajiyesu tayi tawuce bayi alwala tadauro sanan tafito tai sallan asuba tabude Al Qur'ani tana koya Haddan da Abba yabata, saida ta tabbatar ta haddace shafi daya darabi sanan ta tashi, dakinsu ta shiga gyara musu wanda yanzu zata iyacewa a rayuwa that's the only thing data iya gyaran daki shima da karfi da yaji takoyama kanta, ta gyaramusu gado sanan tawuce bayi tayi brush tayo wanka tafito ta shafamai sanan tasaka wani riga da skirt na atampa daya mata kyau tai parking gashinta da kyar sanan tadauki novel kaman barauniya tabude kofan dakinsu ahankali sanan tasakai taleko kadan ganin babu kowa yasa tafito duka, sanan tashiga sadadawa tafara tafiya ahankali zatai stairs. "Ina zaki"? kaman daga sama taji muryan Mami dasauri tajuyo, hada ido sukai da Mami data fito daga dakinta tana kallonta, saukar da kanta

kasa tayi tana kara kankame novel dinta ahankali tace "Mami good morning" batare data bata amsaba tace "wuce kikoma dakinku ga Uwani nan zansa takawomiki break" gyadama Mami kai tayi ahankali sanan tajuya zata koma dakinsu bintada kallo Mami tayi harta shige sanan tasauke ijiyan zuciya ahankali tawuce tasauka kasa, hada mata breakfast tayi kunun gyada da kosai, samin kanta tayi da daukan wani karamin plate tajuyemata ragowan naman da Abban su yarage sanan ta kwalama Uwani dake wanke wanke kira dasauri Uwanin tazo tray tabata tace "kaima Du'a abinci adakinsu" karba tayi tawuce sama bude kofa tayi tashiga tana kallon Du'a data bude novel tana karantawa, har gaban Du'a tazo sanan ta tsugunna ta ijiye tray din still kallon Du'a take, ahankali Du'a ta janye novel din datake karantawa daga kan fuskanta jin kaman ana kallonta hada ido sukayida Uwani, almost 2yrs Uwani na aiki a gidansu but she thinks yaune 3rd time datake ganin Uwanin hakan yasa cikin yar muryan nan nata tace "kece uhmm yama sunanki U....uuuuu...." takasa tuna sunan dasauri Uwani tawashe baki tace "Uwani sunana mai aikin gidan nan" gyadamata kai Du'a tayi sanan tasake maida fuskanta kan novel din tacigaba da karatun dan ko kadan batada surutu kusan cikin duka yaran tafi gado halin mahaifinta indai rashin surutu ne.

Sosai Uwani takasa motsi daga wajen sai wani irin kallon Du'a take dabamatasan tanayiba, bude kofa Mami tayi ahankali ganin yanda Uwani ke kallon Du'a dabamatasan tanayiba dan ita karatun novel dinta take bilhakki yasa ta dakamata tsawa. "Uwani" firgigit ta farka daga dogon tunanin datake haka itama Du'a tadan firgita jin muryan Mami hakan yasa duk suka kallo Mami, cikeda bacin rai Mami tace "kin manta kinbar aiki a kitchen ne zoki wuce kifita" dasauri ta tashi ta taho tace "yakuri Hajiya" fita tayi Mami kuma ta watsa watsama Du'a data zubama mahaifiyar nata manyan fararen idanunta harara sanan tajuya tafice, tai kasa danso take tadaura girki, kitchen ta shiga tana duba naman data saka a wuta itakuma Uwani tacigaba da wanke wanke tana tunani sai chan tajuyo ta kalli Mami da hankalin ta kekan juya naman datake dake wuta tace "Hajiya" "ya akayi Uwani"? Mami tamata tambayan batare data kalletaba, tsayarda komi Uwani tayi tace "Hajiya kunada y'a haka maisa kuke boyeta wanan yarinya taki haka aiko shugaban kasa tafi karfinshi, maisa kuke kulle ta adaki haka" tunda tafara maganan Mami takasa cigaba da juya naman datake ta tsaya chak harta gama maganan datake sanan tace "ki tsaya a huruminki Uwani inba kinaso mu sallameki mu nemo watabane" dasauri tace "yakuri Hajiya tuba nake, kawai daman abin ya tsayamin araine" juyawa Mami tayi tacigaba da aikinta bata karabi takanta ba.
*******************

Yau Friday
Sunada wata al'ada agidan ranan jumma'a kowama gidan nacin gayun Jumma'a. Su Nana tun 11 suka dawo yau sabida lectures daya kawai sukeda shi, tun safe batai wanka ba sabida Novel

din Disastrous Love datake karantawa daya daukemata hankali gabaki daya, su Nana ko harsun sake wanka sunci gayu abinsu sunfice daga dakin zuwa dakin Mum dinsu. Bude kofa akayi Mami tashigo daga bakin kofan ta tsaya binta tayida kallo sanan tace "yau bazakiyi wankan bane"? Dasauri ta ijiye novel din ta kalli Mamin ta dataci gayu cikin wata hadaddiyar bubu na shadda, tashi tayi dasauri tasauka daga kan gadon daga ita sai rigan baccin data saka iya guiwa, ahankali tasaukar da kanta kasa tana wasada yatsunta tace "yanzu zanyi Mami" tana maganan dasauri tajuya zuwa bathroom dinsu tabude kofa tashiga Mami tabita da kallo harzata bude kofa tafice saikuma ta dawo cikin dakin, gaban wardrobe din dakinsu taje budewa tayi ta tsaya tana kallon side din kayan Du'a, bangaren bras dinta ta kalla danta lura kwanan nan bata saka bra at all, daukan bra din tayi ta kalla sai lokacin tagane duk su mata kadanne saisa bata sawa kuma bazata iya fadan mataba, kwasosu tayi gabaki daya tadauki wani leda tazubasu aciki sanan tawuce tafita daga dakin, dakinta tashiga ta ijiyesu agefe sanan ta kwaso mata wasu new manyan bra masu kyau guda uku sanan tafito tadawo dakin, wardrobe din taje ta ijiye bra din sanan tazakulo mata wani lace mai bala'in kyau pink and white flowers dan tasan Du'a da hauka babu abinda ta iya kowani kalan kaya tasamu saka wa take, taciro tahada mata da sabon bra da pant tadauko ta ijiye mata kan gado, sanan tamaida wardrobe din tarufe takoma dakinta, kwalli tadauko mata sabo dawani sabon turare tadawo ta ijiye mata kan gadonta daidai lokacin tafito daga wankan daureda towel a kirji, juyowa Mami tayi takalleta daga sama har kasa, sunnar da kanta tayi kasa cikeda kunyan Mami tana gyara towel din dan bai rufe mata cinya da kyau ba kuma batasan zata sami Mami adakinba data maida rigan baccin ta, juyawa Mami tayi tafice abinta, dasauri tazo kan gadonta ta zauna, kwallin da Mami ta ijiye tafara dauka tace "laaaaa yama sunanshi irin nasu Ya Nana dasuke sawa a ido" wani irin murmushi tayi ta ijiye tadau kwalin turaren tana budewa tace "laaaa nima inada turare yanzu sunanshi Zara" budewa tayi ta ijiye cikeda farin ciki, agurguje tashare jikinta sanan tashiga shafa mai sabon bra tadauka tasaka aiko yamata cip cip lace din tasaka yamugun mugun mata kyau turaren ta tadauka ta feffesa yafi feshe goma sai murmushi take sanan tadau dan kwalinta da kwallin ta tafi gaban madubi, zama tayi tadauki comb taje gashin tayi sanan tai parking gashin da kyar sanan tadau dan kwalin duk yanda taso tadaura takasa daga karshe daurin yan kauye kawai tayi dan bata iyaba amman dudda haka tai kyau sanan ta bude kwallin taciro zata saka takai idanunta looking so excited kafin tasaka tawani tsirama idanunta ihu tayi sosai tawani zarooo hakan yasa tama tundaga idanun har zuwa gefen idanun har kunnenta bakin zanen layi, sosai ta kankame idanunta tana ihu ga radadi sai kuka batasan lokacin data mikeba tana tangadi tana ihu. "wayyo idanuna wayyo idonta" Mami da haurowanta sama kenan taji ihun ta dasauri tai hanyar dakin bude kofa tayi daidai yana shirin kuma kanta da bango tana ihu dawani irin sauri Mami ta tarota tana kokarin tallabo fuskanta tace "maiya sami idon"? Rirrike Mamin tayi cikin kuka tace "Mami idona zafi kwallin nanne ya tsiremin kwayan idanun" Mami na rikeda ita ajikinta tai bathroom dinsu da ita bude tap tayi ta tare hannunta ta debo ruwa wanke mata fuskan tayi tass sanan takashe tap din tana rikeda fuskan nata tace "bude idanun naga" ahankali tabude idanun kadan, aiko idon yayi jajir, kallon Mami tayi tanadan kyafkyafta idon tace "yadena zafi Mami" Mami na rikeda ita tafito da ita daga bayin zuwa gaban madubi zaunarda ita tayi sanan tadauki wipes din Nana data gani awajen tabude taciro kwara daya sanan takama fuskanta tagoge kwallin dayamata layi har kunnenta tagoge tass, sanan ta gyara kwallin dabama tasa a ido ba saidai kasan idanun sanan tadauki kwallin, habanta takama tace "bude

idanun nagani" budewa tayi sanan Mami ta zizara mata kwallin aduka idanun rirrike Mamin tayi tawani tura fuskanta kan cikin Mami tace "Mami idona wani iri daman haka yakeyi wayyooo" chak Mami ta tsaya tamanta the last time da hannunta yama taba jikin yarta saiyau, firgigit kaman wacce ta tuna wani abu sai kawai ta hankadeta daga jikinta batare data kalleta ba tace "dau dankwalinki ki daura" tawuce tafita daga dakin, bin Mamin tayi da kallo sanan tajuya ta kalli Madubi kwallin sunma idanunta wani irin hadadden kyau, murmushi tayi tadauki dankwalin tasake mai wanan local daurin yan kauyen nan sanan ta tashi hijabi tasaka tai sallan azahar ganin biyu tamayi sanan ta tashi tacire hijabi taje tagaban window dakinsu ta yaye kannenta tagani su Aneela da Amal a compound suna guje guje suna wasa duk sunci gayu suma, hakanan taji inama itace komawa tayi tazauna sanan tadauki novel dinta tabude zata fara karantawa saikuma kannenta datagani a compound suka kara fadomata arai jitayi she's damn tempted to go out, maida novel din tayi tarufe sanan tamike tsaye tana rikeda novel din tabude kofa taleko ganin babu kowa yasa da sauri tafito ta maida kofan ahankali ta rufe sanan tai stairs dagudunta har tana neman faduwa tasauka kasa nanma babu kowa, motsi dataji daga sama anbude kofa taji muryan Mum tanama Nana magana "kinduba zobon dayasa kimai hope yay sanyi"? wani irin kwasa tayi dagudu tashiga kitchen dinsu gabanta nafaduwa, gani tayi anama girki a kitchen din ga hadaddun kula na baki dataga an jera asaman kan fridge tana mamaki baki zasuyi yaune kuma, jin muryan su sun sauko kasa yasa da sauri tabude kofan kitchen dazai sadata da backyard tafita dasauri tamaida kofan tarufo dasauri daidai sun shigo kitchen din sanan tawani irin kwasa da gudu taidan mini garden din da Abban su yamusu awajen yawanci weekend Abba nazuwa garden din yazauna yasha iska, is very small a portable ga flowers sosai na daidai kudi ba irin na masu kudiba, ko kadan bata lurada mutumba sabida tana gudu tana waigan bayane jitayi kawai tai tuntube da mutum taiwani irin tumble tasaman kanshi tatsallako gabanshi zatai baya ta fadi yawani irin rikota gam gam hakan yasa dankwalin kanta yawani irin zamiye yafadi kasa, novel din datake rikeda shi yawani fadi shima, yanda gabanta ke faduwa dan tariga tasarai fadi zatayi yasa ta kankame idanunta gamgam cikeda tsoro tana wani irin nishi da bakinta dake fitowa afili.

Chak ya tsaya batare daya saki hannunta ba yake kallonta tundaga kan tattausan hannunta daya rike zuwa kyakkyawan fuskanta da yanda ta runtse idanunta cikeda tsoro tana nishi zuwa yanda jelan gashinta ke gogan kasan wajen. cikin wani irin murya yace "who are you beautiful lady"? jin muryan mutum wanda batasaniba dan duk azatonta da Abba taci karo danshi ke zama awurin nan danhar tasadakar yautamutu a hannunshi yasa tabude idanunta dasauridasauri sanan tawaresu sosai ta kalleshi hada ido tayi dawani kyakkyawan Matashi wanda akalla zaiyi mate din Ya Hamad dinsu yana sanye cikin wani farin yadi mai laushi sai zuba uban kamshi yake, kara zaro idanu tayi tana kallonshi batare datayi maganaba, murya chan kasa yace "who are you? what's your name Pretty Lady" kokarin fizge hannunta daga nashi tashigayi sanan tace "My name is Du'a" wani irin lumshe ido yayi yabude yana karabinta dawani irin mayen kallo yace "you have a very very, verrryyy beautiful name, keyar gidan nanne ko bakuwace ke" kokarin fizge hannunta take takasa sabida yanda yariketa gam gam tace "ni yar gidan nanne, nika sakenmini hannu intafi" ganin hankalin ta nakan hannunta dayaki saki

yasa yace "kinaso in sakenmiki hannu"? gyadamai kai tayi batare data kalleshiba ta kalli gefe daya, yace "to answer my questions saina saken miki hannu" dasauri ta gyadamai kai tana kallon gefe dan batason hada ido dashi sabida kallon dataga yanamata ahankali yana kallonta still yace "ke kanwar su Hamad ne"? dasauri ta gyadamai kai alamun eh hakan yasa yace "amman your mum is different ko?" sake gyadamaikai tayi tace "Mami ce Mum dina" yanda take magana da muryanta kaman na yara tsabagen dadi bala'in tafiya dashi yake she talks kaman yar yarinya kuma kaman ashagwabe, ahankali yace "Yaya akayi to bansanki ba?" ahankali tace "Abba baya barina infita" yanda take maganan gabaki daya taki kallonshi sai gefe take kallo yasa yasake binta dakallo tundaga gashin kanta har zuwa kirjinta da yake hango tudun boobs dinta da kyau wowwww! dan he could have a clear sight saman sabida yanayin wuyan riganta dakuma yanda tadan rankwafo ta gabanshi, tana kallon gefe still tace "dan Allah kasakeni in tafi I don't know you, idan wajen Ya Hamad kazo kaje side dinshi Abba kadai ke zama anan" murmushi yamata ganin da gaske takasa kallonshi  sai gefe taketa kallo tana magana this girl is not use to men! yay maganan aranshi sanan yace "ni wajenki nazo sonki nake" girgixa mai kai tayi dasauri tace "wlh bani bane banama fita baka sanni ba please kasakenmini hannu nakoma cikin gida ba'a san nafitoba wlh" yanda take maganan yake mugun burgeshi baisan lokacin dayace "antaba gayamiki u look beautiful whenever you talk? Is this ur natural hair"? yakai hannunshi zai taba kanta dasauri takoma baya saikuma tasaki kuka shima binta yayi tana komawa baya yana kokarin biyota zai taba mata gashin sukaji karan fadin abu dasauri dukansu suka waigo baya.

Nana ce tafito taci uban gayu sai kamshi take zubawa tadauko hadadden tray da jug din cold zobo da cups kekai dukta sakesu akasa jug din yafashe zobon nabin kasa.

💫 MY BEAUTY MY CURSE 💫

✍️M SHAKUR

Free page

EPISODE4️⃣

Ganin Nana yasa takara karfin kukan tace "Ya Nana kinga wanan mutumin ko yarikeni yaki yasakeni tundazu" juyoda kanshi yayi yana kallon yanda take magana kaman zai cinyeta yace "inda nasan akwai kyakkyawan yarinya irinki agidan nan I wouldn't have wasted my expensive time on this your sister yanuna Nana" wani irin kwalalo idanu tayi sai yanzu tagane saurayin Nana ne wanda zata aura, rawa jikinta ya shigayi tana kallon Nana tana kokarin fizge  hannunta daga nashi, ganin yanda ta daburce yasa yasaketa yana murmushi looking so damn happy, dawani irin gudu ta kwasa tama kasa komawa ta hanyar data biyo dazatazo kawai ta zagaya takoma ta compound tabude kofan falonsu ta shiga da gudu tai sama.

Binta yayi da kallo harsaida yadena hangota sanan ahankali yakalli dankwalinta dake wurin da novel dinta yadauka sanan yakai dan kwalin kan fuskanshi yana wani shakan kamshinta sanan ya janyesu daga kan fuskanshi yakalli Nana dake tsaye takasa kwakkwaran motsi yace "so kinada this beautiful sister baki taba gayamin anything about her ba, in fact you've never mentioned her to me ma" tattaro courage dinta tayi tasakinmai murmushi kobakomi akwai one thing data koyo daga wajen Mum dinta is kirsa, karasowa tayi kusada shi tazauna akan carpet din data shimfidamai cikeda salo irin na siyasa tace "ko Abban mu dudda yarshi ce baya acknowledging nata cikin yaranshi, bama Abba ba har uwarta Mamin ta data haifeta ma, bakaganta ba kaman mayya, Mamanta kafin tai aure tanada aljanu namijin dare, kafin acire mata aljannun akwai wanda ya aure ta so ance shine yamata cikin wanan yarinyar saisa gatanan daban, gabaki dayan danginmu ita kadaice fara, ita kadaice daban, kamanninta komi nata daban, Kakanmu ta tsaneta, she has been nothing but a bad luck duk inda tashiga saitai causing trouble saisa Abba yay grounding nata, ba boko ba islamiyya ko this our compound she's not allowed to come out, iya kanta daki, ko kitchen ba'a bari tashiga kartaje ta kashemu, I don't think ko hot water ma ta iya boiling, she has been grounded like this for years ba tun bayan JSS2" tunda take magananan yake kallonta don shi mugun dan gayu ne dan boko yaron dan gata dan masu kudi wani irin tabe baki yayi yace "you people are being sarcastic, young innocent preety girl zaku kulle haka agida sabida she's different kamanninta daban that's illiteracy, gatanan so pretty my lord, her body is so soft, ga gashi, just look at her snatch waist, ka auri wanan ai zaka more rayuwa da itane kasha miya kasha miya harka gaji" murmushin yake tayi tace "common Muhsin mubar maganan yar Aljanun nan" mikewa tsaye yayi yace "I'm being serious ni, wai kinzaci wasanake, wlh naganta inaso nafasa aurenki, bari naje nasanar da Dad, this ur beautiful sister nakeso wlh ita zan aura, gata so young daga gani batafi 20 ba" tashi tayi dasauri kirjinta na bugawa uku uku dan arayuwanta tana bala'in mahaukacin son Muhsin kaman zata haukace, yarone ga kudi ga gata ga kyau, dawani irin sauri takama hannunshi tarike tace "please Muhsin inma wasa kakemin this joke is way too expensive, bikinmu duka duka baifi 1month bafa saikace kafasa aurena kanwata kakeso daga ganinta yanzun nan don't you see what's going on abinda yasa ake cewa ita yar aljanune, minti nawa da ganinta har kaji kana sonta u are willing to risk our relationship damuka raina for years when we are finally about to get married, dan Allah karkamin haka, kataimakama rayuwana Muhsin kasan yanda nake sonka please Baby" fizge hannunshi yayi yace "stop talking nonsense, wlh bazan aureki ba kinjima na rantse, ni Du'a nakeso ita zan aura" yajuya zai tafi dawani irin sauri tasha gabanshi ta zube ta hanyar kneeling down tahade hannayenta tana kuka tace "please stop saying kanwata zaka aura, please stop saying that, wlh karabu dani zan iya mutuwa Allah kuwa Muhsin dan Allah karkamin haka, you know how much u mean to me eh, me zakayi da ita? babu abinda banfitaba kawai saidai ta nunamin haske" zaro ido yayi yace "what! are you crazy, karki kara comparing kanki da yarinyar nan dan wlh tafiki komi, nima daman zan aureki ne because u are full dan banson mace ramamma, kinada big boobs da ass you know that's what I like, but damn!!!! Du'a shape is bura'uba! her shape is life threatening, idan bansami yarinyar

nan namore rayuwa da itaba I can die, ke kinga ass da boobs wane naki, see maddd flat tummy, see snatched waist, I don't think kugunta yakai 10, ke abeg go gefe we are talking about Kim Kardashian anan danko Kim taga Du'a she go run go hide" dasauri tashiga hade hannayenta zatai magana hankadeta yayi yabita gefenta yawuce yace "saikuma kiyi bayan nagama rantsuwa cewa bazan aureki ba kome zakiyi saidai kuma kiyi ni kanwarki nakeso wlh, am off zanturo Dad anjima da night" yana maganan yay gaba zuwa compound dinsu yaje yashige hadaddiyar jeep dinshi mai gadi yabudemai gate yawuce yafita abinshi.

Takai morethan 15min awajen kuka take sanan wani irin zuciya yadibeta ta tashi tai ciki ta kofan kitchen tabi Mami na kitchen tana kwashe abinci amman ko kallonsu batayiba tana kuka tawuce fuuu ta tafi falo tashiga Mum dake zaune tareda Hawwa suna magana ne sukaga shigowan Nana tana kuka sosai bamata luradasuba tai hanyar stairs dasauri Mum tamike tace "Nana ke lafiya gani nan anan, menene kike kuka haka"? dawani irin sauri tajuyo tadawo batai wata wataba tafada jikin Mum tazube sai kuka, daga Mum har Hawwa rudewa sukayi, Hawwa tace "Ya Nana menene fada kukayi da Muhsin ne" cikin kuka sosai tace "Mum Muhsin yace yafasa aurena wai Du'a zai aura" chak Mami datafito rikeda kula ta ijiye kan dinning ta tsaya dubus awajen tana mamakin mekuma yakawo sunan Du'a a zancen su. Mum dama tarude sabida yanda yarinyar ke kuka tace "Du'a kuma, ta ina Muhsin yasan wata Du'a dahar zaice miki zai aureta iyye, kinsan mekike fadi kuwa"? Mum tai tambayan sounding so confuse and shocked dan batagane kan zancen yartataba, cikin kuka sosai Nana tace "Mum bayan nadauki zobo naje kaimai ajikinshi naga Du'a suna hira haryanama tabamata gashi taciremai dankwali, kuma idan karya nayi kije garden tama barmai dankwalin ta har novel dinta awajen ma" cikin wani irin mugun zuciya jikin Mum har kyarma yake tashiga kwalama Du'a kira.

"Du'a! Du'a!!! ki sauko kasan nan dakanki kafin nazo dakin nan wlh dan na lahira zai fiki jin dadi" bude kofa tayi ahankali tashiga saukowa idanunta sunyija sabida kuka tashiga saukowa daga stairs hada ido tayida Mami dake tsaye a dinning tana kallonta kaman yanda itama take kallon Mami, kasa karasa saukowa tayi Mum tace "zaman lafiyanki shine ki amsa tambayan dazan miki batare dakinmin karyaba inba hakaba yau saina kusan nakasaki wlh, kin sauka kasa ko baki sauka kasaba"? kama jikin skirt din lace dinta tayi gam gam tsabagen tsoro tana kallon Mami tsabagen tsoro sanan ta kalli Mum tace "bayan nai salla shine ta window na leka naga su Aneela nawasa a compound shine nasaci hanya ta kitchen nafita, to naji muryanku a kitchen shine na kwasa da gudu sabida kada ku ganni wlh wlh ni bansan da mutum a garden ba tuntube nayi dashi zan fadi shine yataroni" fashewa da kuka tasakeyi sosai tace "wlh wlh ni banma sanshi ba Allah kuwan Mum"

Cikin wani irin bakin zuciya Nana tai inda take a stairs wani irin finciko gaban riganta tayi ta

chakumeta tace "karya kike baki sanshi ba, kinji ina waya dashi jiya da daddare munyi zaizo yau saisa yau harda cin kwalliya haka sabida ki kwacemin wanda zan aura ko, baki sanshi ba ubanme mikikeyi ajikinshi"? Cikin kuka sosai tace "wlh Ya Nana niban shiga jikinshi ba hannuna yarike kuma inata kokarin na kwace yaki sakina, shine yazo zai tabamin gash......" wani irin kishine ya kwashi Nana tawani kaimata mugun duka abaki bata cire hannu ba sai jini bakinta tasake fashewa da kuka, kimarta Nana tashiga yi baji bagani Mum tace "yima shegiyar yar Aljanun mugun duka Nana, yimata jina jina, itada uwarta sunga kinyi miji daga gidan arziki shine aka turata tayomiki kwace tarabaki dashi, duniya inhar baka mutuba baka gama ganin abin kallo ba, kimeta da kyau kyan datake takama dashi ki chanza mata halitta" yanda Nana ke dukanta tana bubbugata da kome tasamu yasa tafara ihu tana mika hannu tana kwalama Mami kira dan bata iya fadaba bamatasan yanda zata fara dukan yartaba kwata kwata, ahankali Mami tajuya tacigaba da arranging dinning table din datake, kannensu dake wasa ihun dasukaji yasa duk suka shigo ciki suka cika falon, Aneela tafashe da kuka sosai ganin yanda ake dukan yayarta.

kahura mata iskan dakanka mana, let's help the poor girl" ko kallon Sharif baiyiba yakalli Uwani yace "sake huramata" dasauri tsohuwan tace "bawan Allah kayakuri dan Allah kataimaka mata tafarfado hankalinmu duk ya kwanta inda mahaifiyar ta na nan datakusan mutuwa dan Allah kataimakama marainiyan yarinyar nan da iyayenta basu anan" kaman ya kurma ihu yakeji amman yadai daure da kyar dan matsowa wajen kanta yayi yana kallon pink lips da dan karamin bakinta dazai daura nashi akai, kaman wanda ke tsoro yakai bakinshi gently yana kallon fuskanta yadaura kan nata ko mugun sanyin da jikinta yayine yake shiga nashi oho jiyayi jikinshi yadauki wani mugun sanyi daurewa yayi ahankali yahuramata iskan bakinshi zuwa cikin nata kaman wani magic tarrrr yaga tabude idanunta dasukai wani masifan haske sai cikin nashi suna kallon juna saikuma wani uban tari datayi white tana kallonshi duka ruwan daya taho daga bakinta sai nashi dawani irin mugun sauri yacire bakinshi daga nata yaciro kanshi yajuya yana wani irin kakarin amai babuma wanda ya lurada shi sai wani irin ihu da hamdala da duka mutane keyi na ta farfado tana uban aman ruwa aka zagayeta, ganin yakasa aman yasa ya yunkura zai tashi jiyayi an kama hannunshi gam dasauri yajuyo yakalli hannunshi gani yayi Du'a dake amai sosai tarike hannunshi gam tana kallonshi har lokacin da idanun nan nata da kaman bata hayyacinta, dasauri yajanye idanunshi dagakan hannun yakalli fuskanta idanunta kadan suka budu amman shi take kallo saikuma jikinta yafara bari tana kakkarwa, fizge hannunshi yayi daga nata dasauri yana yarfewa danjjn hannun yayi kaman ya sandare yakalli Uwani dake kanta yace "ku chanza mata kaya ku rufeta shes cold a kaita asibiti" sanan yawuce wanshi batare daya kalli Sharif ba yace "wlh nakai mota baka zona saidai kadawo gida da kafa" dawani irin gudu Sharif yatashi yabishi abaya yana kara waigen Du'a da aka zagaye, mota suka shiga Sharif yaja motan da gudu.

Agaban wani gida mai kama da mansion sukai horn bude musu akayi suka shiga, Sharif na parking yabude mota yafito yana attishawa, daidai wata kyakkyawan mata tana sanye dawani hadadden lace tafito kana ganinta kaga mamanshi sabida kamanninsu tana ganin dan nata ta tsaya turus tana kallonshi ganin yanda yay sharkap daidai nan shima Sharif yafito yana murmushi dasauri takaraso wajen tace "what on earth happen daka jike haka son" ranshi abace yace "lemme shower Ammi" yay wucewan shi, tabishi da kallo saikuma tajuyo takalli Sharif dataga yana murmushi tace "maiya faru yaji ke haka Sharif kaima jibi yanda kai daka daka kaman kai wasa a mud"? Dan dariya yayi yace "aikin Allah mukayi Ammi" aikin Allah? ta maimaita gyadamata kai yayi yace "Ammi we just saved a girl dabadan muba data mutu arijiya wlh, Asad yacirota daga rijiyan nikuma na ciro both Asad and the girl, nima bari naje nai wanka" shima yawuce yabar Ammi awajen baki bude.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️M SHAKUR

free page
EPISODE 🔟
Gban wani hadadden flat yayi ya bude kofa ahankali yashiga, kaga flat din zaka dauka a turai kake, sama yayi yabude wani daki da komi nacike kenan blue, bathroom yabude yashiga danyay wanka, koda yafito shiryawa yayi cikin 3 quarter da singlet fara,  sanan yafito anan falon sama yaga Asad zaune dagashi sai towel daya daura a waist dinshi fari, tulin gashin kanshi ajike da ruwa yana tsiyayar da ruwa, ruwan nabin fuskanshi yana diddiga akan kirjinshi gwanin ban sha'awa, dark skin dinshi nawani irin glowing dankomai bai shafaba yana fitowa daga wanka yatuna da abinda yakeyi dazu a mota yazo yazauna yacigaba, kirjinshi kaman zai fashe acike tsabagen work out gashi da uban hair akirjin dasuka kwanta sukai lub lub har wajen cibiyanshi da maranshi, hakama muscle dinshi amurtuke yadaura MacBook din akan cinya nashi yana danne danne ya mikarda kafafun shi yadaura kan wata cushion. "katashi kasa kaya Asad yanzun nan fa kabar cikin rijiya kayi wanka basaikasa kayaba" kaman ba dashi ake magana ba yamai banza dan haushin shi yakeji sabida abinda yamai dazu, tabe baki Sharif yayi yace "koba komi dai after such a long time nasa kayi taimako u just save a life today wired dude kawai" dago kanshi yayi yawani kalli Sharif din irin kallon nan na dani kake, dagamai gira daya Sharif  yayi sanan yawuce yace "am starving idan kagama come down muje ka gaida Dadda, nidai natafi wajen Ammi naci abinci" yawuce yasauka kasa abinshi batare daya karabi tanan Asad dinba tunda yaga fitina yakeji, baitaba ganin fitinannen yaro dan bala'i irin Asad ba.

Yadade yana danne danne sannan yarufe system din yatashi daidai lokacin iPhone 13pro max dinshi tahau ringing kobai kalli screen dinba yasan Ammi ce hakan yasa yadauki wayan yakara a kunne cikin muryanshi dakeda dan sanyi yace "Ammi gani nan zuwa" katse wayan yayi ya jefar kan kujera sanan yashiga wani daki, shi dakin komi off white ne ba kaman na Sharif ba, hoton dake jikin bango nashi zaisa kagane wanan dakinshine, gaban madubi ya tsaya dayacika da kayan shafa sanan yadau cream ya shafe jikinshi kafin yabude wardrobe yadauko wani 3quater maroon da white t-shirt yasaka dasukamai kyau sosai sanan yakoma gaban madubi wani man gashi yabude sanan yalukata yashafa akanshi kafin kaceme gashin su kara wani kanannadewa bakinsu na shinning kaman wani gashin jariri sanan yadau turarukanshi ya feffesa yadau yazura wani crock na maza yafito falon saman, wayanshi yadauka sanan yawuce yafice daga flat din, yana fita wani rana yadaki fuskanshi tsaki yayi yace "I hate this damn country" Babban flat din gidan yayi kofa yabude ahankali yashiga Sharif ne ke zaune afalo sai wasu yan mata guda uku Aneesa, Rahima, da Mariya duk suna zaune kusada Sharif din suna hira, suna ganinshi tsit kakeji wani irin batarai yayi kaman baitaba murmushi tunda yazo duniya yazo zai wuce tagaban su dasauri suka shiga gaidashi. "Ya Asad welcome ya hanya" da kyar ya iya bude baki ya amsa batare daya kallesu ba. "fine" that's the only thing yafadi sanan yay dinning Sharif nabinshi da kallo saikuma ya kalli Aneesa data bishi da kallo kaman zata hadiyeshi.
Zama yayi kan kujera daidai lokacin Ammi tafito daga kitchen rikeda flask tana kallon fuskanshi tace "sannu da aiki superman mai shiga rijiya, yanzun nan nagama hadamaka tea dinan

zokasha koya kori sanyin daya shiga jikinka" dan murmushi yamata daidai tamikomai cup din shayin dayaji kayan kamshi karba yayi itakuma taja kujera kusadashi tace "Ya hanya" ahankali yace "Ammi yaushe zamu koma gidanmu"? "to marason zumunci anan kano zaku cigaba da zama" dasauri yadago kanshi wata hadaddiyar mata ce kyakkyawan gaske tana sanye da bakin jallabiya kesaukowa, ahankali yace "ina yini Anty" hararan shi tayi sosai tace "kai yaron nan ina kanwar mahaifinka kana kirana da Anty, abinda kike koyamai kenan Maryama? Kaf family nan bamuda yaro mara tarbiya irin Asad" sanin halinta yasa Ammi tace "stand up and greet her properly Asad" kallon Ammi yayi yanda ta gyadamai idanu yasa yatashi ahankali yana kallon kasa  yace "ina yini M...um" washebaki tayi takaraso inda yake hannunta takai kan fuskanshi tace "ko kaifa Asad, kadawo lpy" kanshi akasa yace "lpy" murmushi tayi tace "ance kadawo kayi aikin nanne na youth start up forum ko da government sukai establishing right?" gyadamata kai yayi batare daya kalleta ba, cikeda gamsuwa tace "awani tasha zakuyi Channels television news" murya chan kasa yace "kowani TV station zasusa har nagama na 7days" gyadamai kai tayi tace "Masha Allah, Allah yataimaka, saikuma batun aure ko" shiru yayi sakinshi tayi tace "anyway nadawo mayi maganan da kyau, let's go girls" tashi matan sukayi suka bita suka fice.

Daure fuska yayi sosai yanajan cup din tea dinshi zaikai baki yace "saisa banason zuwa gidan nan I don't like her Ammi, this Anty Turai" shareshi Ammi tayi tajuya takalli Sharif dakecin abincin shi tace "you want more Sharif" "Ammi am full" kallon Asad din tayi tace "mezakaci"? kallon abincin data bubbudemai yayi sanan idanunshi suka sauka kan spaghetti da meat balls da hannu yanuna mata zubamai tayi ya karba yashiga ci ahankali bin dan nata take da kallo take, anytime taganshi mahaifinshi kawai take gani halinshi sak dana ubanshi, juyowa tayi takalli Sharif tace "baku bani labarin ciro yarinyar dakukayi daga rijiya ba" kaman jira Sharif yake yace " Ammi I was driving fa kawai wata mata tasha gabanmu tana kuka wai mutaimaketa yarinya tafada rijiya, Ammi I was begging Asad fa yaje mucirota wai bazaiyiba gashi ba maza sai tulin uban mata kaman gidan biki duk suna kuka, shine nace musu mujeni nacirota dan nasan that's the only thing dazai fitoda Asad daga cikin motan nan danni kadai nasan irin mugun halinshi, aiko ina shiga saigashi yataho ashedai yana sona yasan ban iya ruwaba fear of my death yasa yazo bawaidan he meant to save the girl ba, shine yashiga fa yacirota, Ammi kinsan menene" yay maganan yanajan kujera da sauri yana zama sanan yakalli Ammi dake kallonshi yace "Ammi nifa dasuketa yarinya I thought small girl ce fa tafada rijiyan saigashi Asad yafito da zankadediyan budurwa innalillahi Ammi kinga kyanta kuwa" Ammi dake sauraronshi tace "haba" dasauri yakalli Asad dake cin abincin anatse yana danna waya yace "Asad isn't the girl beautiful" batare daya kallesu ba yace "I don't know bankalleta ba" wani mugun tsaki yaja yace "Ammi wlh Asad dan rainin wayau ne" dan dariya Ammi tayi ganin yanda Sharif ya tunzura sosai tace "don't mind him kaji cigaba da bani labarin" murmushi yama Ammi yace "wlh Ammi tunda nake Allah Ammi harna gama yawona across the globe ni bantaba ganin kyakkyawa irin yarinyar nanba Ammi she don't even look Nigerian, hala half cast ce, Ammi she's so pretty gashinta har waist, she's so pretty I wish I can even see her again" ture plate din abincin dayagama ci Asad yayi yamike Ammi  dasauri ta kalleshi tace "harka koshi? Baka cinye ba ai" gyadamata kai yayi yace "ya isheni, natafi wajen Dadda" dasauri Sharif yatashi yace "wait for me Asad" ko kallonshi baiyiba yawuce Ammi tabisu da kallo tana murmushi, Sharif is such a

gentle man with a very very forgiven spirit, shikuma Asad is opposite na hakan, churarren mutum ne baka gane gabanshi da bayanshi ko itama sabida ita tahaifeshi ne saisa take iya fahimtan halinshi tass,.

Wani flat suka shiga kayataccen falo ne da kujera ke ciki sai lallausan carpet da aka rufe ko ina na kasan dakin dashi sabida sanyi sai wani tsohon dattijo da akalla zaikai shekara 90 ko fin haka ke zaune kan wata kujera mai ultra taushi wacce kanagani kasan musamman sabida shi akayita yana zaune gashinan tsaf tsaf sai wani bakin glasses a idanunshi hannunshi rikeda ayaba yanaci da aka yayyankamai awani clean bowl, tunda yashigo gidan this is the first time yayi kayataccen murmushi yace "Dadda" da sauri tsohon dake tauna ayaba abaki ya tsaya chak saikuma da sauri yasake gyara zaman glass dinshi a idanunshi yakalli kofa sabida haske kofa yasa baiganesu ba cikin muryanshi ta tsufa da still kuma take fitada kyau yace "amaida kofan arufe" dasauri Sharif dake hadiye dariyan shi yamaida kofan yarufe hakan yabashi daman ganinsu ahankali yanuna Asad da yatsa yace "Sharif Asad nake gani" dawani irin sauri Asad yaje bowl din jikinshi yacire ya ijiye agefe sanan yawani rungume kakanshi tsam tsam yace "Dadda kai kadai nayi missing wlh, kaga Sharif tunda na shigo garin nan yake batamin rai Dadda" washe bakinshi da hakora sun fiffita yayi yace "to wlh su kiyayeni aina gayamusu duk wanda yataba Asad toni yataba kona mutu bazan yafemai ba" dariya sukayi duka Sharif yazo yace "Dadda kai bazakamai fadaba mugun halinshi yay yawa" hannu yamika ya kamo hannun Sharif yace "banace ku hada kanku ba kome yayi kamai hakuri, shi hali zanen dutse ne ko mutum zai rabu dashi saidai da kadan kadan, halin mahaifinshi Abdullahi yagado sak" kankameshi sosai Asad yayi yace "i love you Dadda na"

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

wa.me/+2347012181461

Free page
EPISODE1️⃣1️⃣
Da taimakon Matan dake compound din aka kwasheta akai falonsu da ita jikinta na mugun barin sanyi daidai lokacin motarsu Abba tai parking akofar gida wani irin azababben gudu sukayi dayake Hamad shiya tukasu da Mami da Abba ne kadai sauran duk sun barsu awajen Kaka achan Ikara, dawani irin gudu Mami tashigo gidan idanunta sunyi jajir, this is the first time data iya cire koma meke sata yima yarta wani kala tanuna tsantsan damuwa da so akan yartata

tadubi matan tace "ancirota ancirota daga rijiyan? jama'a kufadamin ina y'ata Du'a, ina take"? Tai maganan tana kama kirjinta dataji yana wani irin bugawa tsabagen fargaba, daki matan gidan suka nunamata sukace "tana daki, yanzun nan aka shiga da ita ciki" dawani irin gudu Mami tai flat dinsu Abba ma dayashigo yabita dasauri Hamad shima dagudu yabisu da shine last na shigowa sabida parking mota dayake, tana shiga falo taga some few mata akan Du'a dahar lokacin take ajike akasa tana wani irin rawan sanyi hakoranta na karkar kar kaman ana hada kacha ana gwarasu, wani irin ihu Mami tayi. "Du'a! Du'a" yanda Mami tayi baya kaman zata sume yasa dasauri Abba yatareta yace "calm down" juyawa Matan dakin sukayi suka fice ganin maigida, daidai Uwani tasauko kasa dawasu kaya da bargo daban daban a hannunta, tashi tayi daga jikin Abba dasauri takarasa wajen Uwani, karban kayan hannunta tayi sanan takoma inda take, dagota tayi dasauri takalli Hamad tace "Hamad bani wuka" dagudu yay kitchen wuka yadauko yafito yaga rigan jikinta Mami tayi Abba da Hamad duk suka juyar dakai chanza mata kayan Mami tayi agurguje sanan tawani irin rungume yarinyar dasauri tarufeta da bargo tana kuka. "I am sorry Du'a sorry" matsowa wajen Abba yayi hannunshi yakai yadaura kan wuyanta jin sanyi yasa yakalli Uwani yace "jeki hado garwashi" sanan yaciro hannun Du'a daya yana murza tafi hannun dasauri Hamad shima yazo yakama dayan hannunta yana murzawa duk tana jikin Mami data kankameta sosai, ba'a wani dauki lokaci ba saiga Uwani da uban rushi a kasko dan makota taje tasamo, ajiye wa sukai agabanta still suna murza hannunta ahaka suka samu kadan kadan tarage rawan sanyin hartazo tada ina gabaki daya kallon fuskanta tayi yanda idanunta ke a lumshe shafa fuskanta Mami tayi ahankali takira sunanta.

"Du'a" bude idanunta kadan tayi saikuma tabudesu gabaki daya tana kallon fuskan Mami, dasauri Hamad yataso kansu yana kallonta yace "Du'a taya kika fada rijiya"?zubamishi idanu tayi shima tana kallonshi saikuma ahankali tamaida idanun kan Mami tana kallonta asanyaye, Mami hakanan taji jikinta yay sanyi sabida yanda yarinyar ke kallonta, hawaye taga sun zulalo ta gefen idanunta kafin ahankali tabude bakinta cikin muryanta dabata fita sosai tace "maisa aka cironi daga rijiyan eh? Mami inaso namutu kowa yahuta saisa kodana fada saidai nadinga lumawa cikin ruwan ko tsoro daya banji ba saima kwanciyan hankali danaji domin ajalina yazo, Mami naso namutu sabida kihuta hankalinki ya kwanta kince tundaga randa kika haifeni baki karasamin kwanciyan hankali ba, yau dana fada rijiya all I could thought of was yanzu zaki fara samin kwanciyan hankali, bazan kara jawo matsala agidan nanba, bazan kara saki ko Abba a matsalan Kaka ba, Ya Nana zata auri Muhsin dinta, bazan kara zamema kowa matsala ba, Abba bazai kara wahalan boyeni ba dan nariga namutu" yanda take maganan tana kuka mara sauti sai hawaye kobakada imani sai zuciyanka ta sosu, ahankali tace "Mami akwai wata tambaya dana dade inaso namuku keda Abba" taidan shiru saikuma ahankali tace "bayan kun haifeni maisa tun a asibiti dakuka ganni daban bakusan yanda kukai dani ba maybe ko kuce baku sona a kaini gidan marayu kokuma kuce a chanza muku yarinya bani kuka haifa ba, maisa kuka daukeni still kuka raineni maisa kukamin haka, wanan kalan rayuwan dakukasa inayi kullum zaban mutuwa nakeyi akanta dan tafimin alkhairi I just want to die nahuta, dan Allah kubarni na mutu" tafashe da kuka sosai dayasa daga Abba Mami da Hamad were damn speechless itako Uwani dake gefe kuka tadingayi, tadade tana kuka ajikin Mami babu wanda

yay attempting hanata ahaka bacci yay awon gaba da ita, ahankali suka kwantar da ita akan kujera suka lullubeta sanan Mami tazauna gaban kujeran tana kallon fuskanta, Tashi Hamad yayi yakalli Abba da Mami yace "Abba I want to see you both" yay sama tashi Mami tayo takalli Uwani da jajayen idanunta tace "ki zauna da ita" gyadamata kai Uwani tayi Mami tawuce sama itama, Abba yadade tsaye awajen sanan yawuce yay sama, dakinshi Hamad yabude ya shiga Mami tashigo Abba dashine na karshe shima yashigo yasami waje yazauna, kallon Abba Hamad yayi yace "Abba what are you going to do? Yaya zakayi da maganan Kaka?" kallon Hamad yayi yama kasa magana saikuma chan yace "all I know is bazan taba iya koran y'ata daga gidan nan ba" dasauri Hamad yace "Abba yazakayi da bakin Kaka, tace inhar yarinyar nan batabar gidan nan ba bata yafemaka ba, itaba mahaifiyarka bace kaza kaza kaza, Abba Kaka ta tsufa and we all know yanda tsofaffi sukai believing akan all this superstition, Du'a tazaman ma gidan nan da family mu gabaki daya matsala, jibi duka su Baffa dazu sunce duk akoreta ni I think inhar hakane zan dauki Du'a natafi da ita chan Jaji tai zamanta a apartment dina" dasauri Mami tace "Hamad duk randa mahaifiyar ka tasan kaika tafi da Du’a abin bazai muku kyau ba, kuma Du'a mace ce bazaiyi kyau tayi rayuwa dakai kai kadaiba dama kanada mata ne, ni kaina ayanzu all I want is peace, tunda Du'a ce matsalan afitarda ita daga gidan saisa na yanke shawaran kaita wajen Mama na achan Abuja" kallon Abba tayi ahankali tace "Dadyn Hamad" kallonta yayi yay shiru batare dayace komiba, ahankali tazo kusadashi zama tayi sanan takama hannunshi tarike tace "I know tunanin dakake da abinda ke ranka, mu dinan bamuke kula da Du'a ba wlh Allah ne, so it's high time we free this girl mu mikama Allah komi and I assure u idan tana hannun Mama she's safe nasan Mama na, I don't want u to be stubborn, u are a family man, ba Du'a ce kadai yarka ba, sauran ma dole ka kalli yanda rayuwan su zata cigaba da gudana, sabida Du'a kar peace da family ka ya wargaje just look at what Nana is going through now itama ai yarka ce, the way u look out for Du'a itama haka kake looking out for her, kayakuri kaduba lamarin kaji" tunda take maganan yake kallonta harta gama, ajiyan zuciya yasauke sanan yace "I will think about it, kubani waje yanzu" gyadamai kai kawai Mami tayi ta tashi tawuce tafice, yakalli Hamad yace "ka kira Dr na yazo yadubata tashi katafi" tashi yayi ahankali yafice shikuma Abba ya kishin gida da kujera ya lumshe idanu Allah kadai yasan meke going azuciyanshi.

Wuraren magrib likita abokin Abba wanda shine likitanta tun tana yar karama yazo yadubata allura yamata sanan yabata magunguna Abba ya sallameshi yatafi.

"she's alive! she's alive I can feel her pulse" sama sama takejin maganganun nan kaman a eco saikuma chan tabude idanunta sukai clocking da nashi......tarrrr tabude idanunta daga baccin datake tanabin inda take da ko'ina na dakin da kallo, ganin tana dakinsu kan gadonta ne an lullubeta da bargo, mafarki take kenan, mutumin data bude ido tagani dazu yacirota daga cikin rijiya tagani yanzun nan amafarki, ahankali ta yunkura ta tashi zaune ta jingina da bango tana kallon ko'ina ganin gari yama soma wayewa, saukowa tayi daga gado sai alokacin taga wani jibgegiyan akwati da batasan daga ina yazo ba baka kwara daya atsaye gaban wardrobe dinsu, bathroom dinsu tawuce tashiga wanka tayi da ruwan zafi sosai tana karajin karfi ajikinta sanan

tafito daga wankan daidai lokacin Mami nabude kofan dakinsu tana shigowa hada ido sukayi da Mami ahankali ta sunnarda kanta kasa tana tuna all maganganun data gayama Mami jiya suna dawomata fresh a memory dinta kasa motsi tayi itama Mami tadauke kai tawuce wardrobe wasu kaya taciro mata tajuyo ta ijiyesu kan gado tace "ki shirya kiyi salla bari naje nakawo miki breakfast".

Fita Mami tayi daga dakin itakuma tashiga shiryawa agurguje sanan tahau kan dadduma tai salollin dake kanta saida tai azkar sanan ta tashi ta cire hijabin tazauna akan gado, bude kofa Mami tayi tashigo dauke da tray na abinci sanan takaraso cikin dakin ajiye abincin tayi kan side drawer gadonsu sanan tadawo tazauna ahankali kan gadon kusada Du'a da kanta ke kasa har lokacin dan wani irin kunyan Mami taji tanaji, murya chan kasa tace "Mami ina kwana" shiru Mami tayi tana kallonta batare data amsa ba saikuma gently takai hannunta kan fuskarta ta tallabo habarta hakan yasa tadago idanunta ahankali takalli Mami, murya chan kasa Mami tace "Du'a" ahankali tace "Mami I'm sorry Kinji" murmushi Mami tayi tace "shiiii I want you to listen to me" gyadama Mami kai tayi, Mami tadan numfasa tace "all abubuwan dakikaga nida mahaifinki namiki badan mun tsaneki bane saidan we are all trying to protect you Du'a, Du'a nasan kinsan wanan abin dan nasan kinsha jin yan uwan Abban ku nafadi, dana haifoki babu kalan maganan da ba'a fadiba akanki, ance ke ba yar Abba bace, naje na nemi ubanki nahadaki dashi, ke mayya ce ke yar ruwace" shiru Mami tayi tana sauke ijiyan zuciya sanan tace "Du'a akwai many things which u don't know kuma banmason kisani, I fought mahaifinki, we fought hard muka samu yan uwanshi da Maman shi suka barki kika zauna agidan nan left to them koranki sukaso ayi" Mami tasakeyin shiru sanan ahankali takai hannunta tadaura kan kumatun Du'a dake kallonta ahankali tace "Du'a you are special! tun ranan damuka haifeki mukasan hakan, you are special saisa kikaga muna boyeki, Du'a ke dabance! muna boyeki ne cus munyi tunani ta hakan zamu iya kareki and protect you, but u got it all wrong kin zaci mun tsaneki ne amman bamu tsaneki ba, kintuna abinda yafaru dake a JSS2 dayasa Abba yahanaki fita at all kinaso yakara faruwa dakene" girgixa ma Mami kai tayi dasauri hawaye nacika mata idanu. Ahankali Mami tasauke ijiyan zuciya tace "nakira Mama, Grandma dinki tariga tasan komi dama, yanzu da safen nan Hamad zai kaiki chan wurin ta a Abuja harsai komi nagidan nan ya daidaita, I think kema is best for u, your childhood has been terrible, kin taso cikin kyaran kowa is high time kije inda nasan u will receive d best care batare da an kyareki ko an ware ki ba, kinason kije wajen Mama na ko" ahankali ta gyadama Mami kai hawaye na zubomata, hannu Mami takai tashare mata hawayen tace "nasan namiki laifi, I've wronged you in so many ways just to please yan gidan nan but bazan karaba, nina daukeki na raineki for 9 months I can never hate you, abinda nakeso dake is take very good care of yourself, kizama yarinya mai wayau da basira, know when u are in danger and when u are not, kidage da addu'a, ki rike Allah danshi kadai ya isarmiki, I want you to be a good girl, karki sake kima grandma dinki ko any of your uncles rashin kunya kinji Du'a, I know u are in a good hands this is the first time dazaakije wani wuri da hankalina ya mugun natsu, now eat your food saiki fito ki gaida Abban ki kuyi sallama bari nakai jakan I waje" gyadama Mami kai tayi Mami ta tashi jakan taja tawuce tafita daga dakin, shiru Du'a tayi Allah ma yasan har cikin ranta tana farin ciki zatabar gidan nan sabida tasan yanda

Maman Mami kesonta lokacin tana yarinya idan sukaje gidan kaman zata cinyeta, koba komi bazata kara ganin Muhsin ba, mugun mutum, koba komi idan baiganta ba zai hakura ya auri ya Nana, Hawwa zata huta da hararanta kullum Mum ma tahuta babu wanda zai kara kiranta yar aljanu, and at the same time yau saitaji wanan bakin cikin da kunci na haushin Mami dayakeji dukya fita daga zuciyanta sabida fir the first time Mami ta zaunar da ita tamata bayanin abinda bata taba mataba kenan. hannu tamika tadauki tray abincin ta abincin taci bama tawani ci sosai ba ta ture ta ijiye, shigowa dakin Mami tayi takalleta tace "tasoto muje kiyi sallama da mahaifinki" gyadama Mami kai tayi gabanta nafaduwa hijabinta tasaka sanan tabi bayan Mami suka fito, Abba na zaune akasa yana karanta jarida hangita yasa ya tsayar da karatun yana kallonta harta karaso, dan nesada shi ta tsugunna ahankali tace "ina kwana Abba" "ya jikinki akwai abinda ke miki ciwo"? Abba yamata tambayan bayabo ba fallasa wanda idan tasabo tasaba dan Abba naturally he's not that kind of a friendly father dake wasa da yaranshi, gyadamai kai tayi ahankali tace "babu ko'ina Abba" gyadakai yayi cikeda gamsuwa yana kallonta, batare data dagokai ba tace "Abba kayakuri bazan kara abinda nayiba" ahankali yace "I know" dagokai tayi ta kalleshi, hannu yasa a aljihu yaciro bandir nayan 200 20k yace "zo" tashi tayi ahankali takarasa gabanshi karba tayi ahankali tace "nagode Abba" "Allah kiyaye hanya, jeki Hamad na jiranki a mota ta" hakanan batasan mesaba kawai taji kuka yazo mata dasauri tajuya tana daura hijabinta kan fuska Abba kuma yabita da kallo, fita tayi daga falon, Mami ta biyota abaya rikeda hadadden kula na abinci.

Hamad na tsaye gaban motan sienna Abba yaga fitowanta yana kuka, murmushi yayi yabude mata gaban motan tana karasowa tashiga ta zauna, karasowa itama Mami tayi tana murmushi tace "bazakama kanwarka magana tarage kuka ba tadauka yarinya ce ita" murmushi yama Mami baice komiba, Mami ta ijiye mata kulan akan cinyanta tace "ga abinci inkinji yunwa kici naga baki waniyi break da kyau ba and stop crying" gyadama Mami kai tayi, tashi tayi takalli Hamad tace "kutafi Allah kiyaye hanya" rufe kofan yayi sanan yazagaya yashiga yatada motan yaja Mami namusu bye bye suka fice daga Gate din. ajiyan zuciya Mami tasauke ahankali tace "Allah ya azurtaki da farin cikin rayuwa Du'a, I love you so much y'ata, zan dinga miki addu'a kinji Du'a"

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️M SHAKUR

Free page
EPISODE 12
Sosai Hamad ke zuba gudu akan titi, har cikin ranshi he is happy for Du'a na barin gidansu datayi, bini bini yake kallonta yanda saibin hanya da komi take da kallo kana gani kasan bata saba fitowa ba, dan juyowa yayi yakalleta ganin yanda take kalle kalle yasa yay dan murmushi yace "iyye basaban ba yau anfito waje" juyoda kanta tayi takalleshi washemai baki tayi tana murmushin nan mai tafiyar da imanin mutum tace "Ya Hamad rabon dana fito waje wlh harna manta nafi shekaru" murmushi yamata yace "this is a chance da Allah yabaki, remember abinda nafada miki duk wanda yadogara ga Allah to Allah ya isar masa, cikin sauki tashi daya Allah yacireki daga kuncin gidan mu, so babu abinda yagagari Allah muddin ki kayi imani, just always thank Allah kinji and be a good girl" gyadamaikai tayi kaman mai tunani tace "Ya Hamad nifa nama manta kamannin Maman Mami fa Grandma, tun ina karama da Mami ta taba zuwa dani ban kara zuwa ba, saidai muyi magana awaya, su Aneela ne suka santa" dan murmushi yayi hankalinshi nakan hanya yace "grandma dinki is one of the nicest person I know in this world, tanada kirki gatada son mutane, duk naje Abuja sainaje na gaidata, you are so lucky to have her as grandmother" shiru Du'a tayi kaman tana tunanin maganan shi saikuma chan ta kalleshi tace "Ya Hamad maisa kai u are different agidan mu? baka biyema su Mum da Ya Nana, kafisu kirki duka" yana kallon hanya still yace "let's say sabida ni namiji ne I see life differently daga yanda mata keganin life, and Abba yabani tarbiyan da nakan iya banbance right from wrong" murmushi tayi takalli kulan kan cinyarta tashiga budewa name ne soyayye da Irish da plantain. "bani nama naci" turo baki tayi tadauko nama daya takai tasamai akan hannunshi dayake bata, murmushi yayi ya wurga abaki yana taunawa yace "wow girkin Mami always taste different" nama daya itama ta dauka tamaida kulan tarufe sanan tahauci tanamai hira kadan kadan harta cinye sai bacci, kallonta yayi ganin yanda take bacci yasa yay murmushi gabgarawa gefen hanya yayi yay parking Sana yadan taso yasaukar mata da kujeran sanan yakoma mazaunin shi yatada motan yana bata wuta.

Wuraren 1 suka kai Abuja, tadata yayi ta hanyar kiran sunanta. "Du'a, Du'a" bude idanunta tayi kadan, hararanta yayi yace "duk uban baccin dakikayi jiya bai isheki ba yarinya saison bacci" tashi tayi yace "gyara kujeran" gyara kujeran tayi yataso sanan takalli hanya yace "kinga yanda Abuja keda kyau kalli titi ba irin na Kanon Kuba" murmushi tayi tace "mun kuwa kaiwa gidan" gyadamata kai yayi yace "takirani yafi sau uku duk kina bacci" shiru tayi tana kallon ko'ina kaman zata hadiye garin da idanunta saiwani irin sanyi da shauki takeji har sukakai wani estate mai suna Presidential Estate. zaro ido tayi tana kara kallon ko'ina ganin gidaje masu suna gidaje ba muna gidaje ba, tasha ji idan su Mum na gulman su tana yawan cewa ai Abba sabida ya rainata yar gidan masu kudi yaje ya auro mata, itama yarinyar kaman mayya itace kawai ta auri talaka mahaifiyarta tabarta ne sabida ita kadaice yarta mace, ita bazata iya tuna gidan dasuke zuwa a dan memory dinta na Grandma sonta lokacin tana yarinya akazo kuma aka dena zuwa da ita saidai su Aneela da Muhammad da Mudasir.

Shiga Estate din yayi yana tafiya ahankali ganin yanda Du'a is enjoying the view din, agaban wani lafiyayyen gida Hamad yay horn, wani security yafito ganin Hamad yasa yace "barka da zuwa yallabai Hajiya ta sanar dani zuwanka" gyadamai mai kai Hamad yayi yana murmushi shikuma yakoma ciki yabude musu Gate din, Jan motar ciki yayi Du'a ta kwalalo idanu tace "nan ne gidan Grandma Ya Hamad" murmushi kawai yamata yana karasa parking motansu acikin jerin motocin dakenan gidan wanda babu mate din seinna su, bude motan yayi yafito sanan yamata alamu data fito gyadamai kai tayi daidai security yagama kulle gate yazo yace "akwai akwati ne Yallabai" "oh yeah" Hamad yafadi yana budemai booth daidai lokacin Du'a takaraso wajen tsayawa chak security yayi yana kallonta ganin haka yasa Hamad yace "ga akwatin" dasauri yajuyo yakalli Hamad hannu yasa yadauki akwatin yawuce Hamad kuma yarufe booth din yajuyo daidai lokacin wata hadaddiyar mata wacce kana ganinta kasan ba yarinya bace dan ta ijiye jikoki tafito, tana sanye da bubun atampa ajikinta gatanan black beauty da akalla zatakai 70.

"oyoyo oyoyo, su maigida an iso" jin muryanta yasa dasauri Hamad yajuya washe baki yayi yace "Hajiya wanan kwalliya haka, bazaki barma yara ba" dakuwa tamai tace "kaci gidanku, yanzu dani dasu idan akaje gasan kyau basai akwasheni sau dari baza'a kwashe suba" karasawa yayi har inda take sanan cikeda girmamawa yadan runtsuna yace "ina yini Hajiya" hannu tasa tashafa kanshi tace "kasha hanya Soja na maigida, jekai wanka kahuta kaida komawa kano sai gobe" tai maganan tana kallon Du'a dake bayan Hamad kanta akasa tana wasa da hijabinta kunya yahanata dago kai. "Du'a" matar takirata ahankali, ahankali Du'a kaman wacce ke tsoro tadago kanta takalli kakanta fess tagane ta danga kamanninta da Mami nan, black beauty abinta yar gayu, ganin takasa magana yasa dasauri tabude mata hannu tace "zonan zoki rungumeni, taho taho" ahankali Du'a taje dasauri tashige jikinta takankameta kankameta Hajiya tayi tace "Alhamdulillah Alhamdulillah, Du'a sannu, sannu kinji, akwai abinda ke miki ciwo"?girgizamai kakan nata kai tayi, dagota Hajiya tayi tasa hannu tai cupping face nata tana kallonta kaman yanda Du'a me kallonta ahankali rasama mezatama yarinyar tayi hakan yasa ta manna mata kiss a goshi sanan takama hannunta tarike tace "muje nakaiki dakinki kiyi wanka"

Ciki tashiga da Du'a falon wani irin hadadden gaske gashinan Duplex sai yan aiki guda biyu dataga suna gyara dinning suna ganin Du'a duk suka bitada kallo suna gaidata. "welcome Du'a" murmushi Hajiya tayi tace "kingan su suke tayani aikace aikacen gida, wanan sunanta Shema'u, dayan kuma sunanta Razika, duk sun sanki, jeki musu sallama" gabansu taje ahankali sai kallonta suke kaman basu taba ganin mutum ba, hannu tamika musu cikin muryanta mai dadi tace "Assalamu Alaykum, nice to meet you" dasauri suka karbi hannunta suna murmushi Razika tace "you are so beautiful" tsayawa tayi turus tana kallonsu Hajiya dake kallonsu tace "tell them thank u sunce kinada kyau" ahankali tace "thank u" sakinta sukayi itakuma Hajiya tasauke ijiyan zuciya sanan tace "taho mutafi" dasauri tajuyo kaman jira take dama stairs sukayi sukai sama saitaga ashema kasan baida kyau wani daki tabude dakin mai kyau sosai saiga hoton ta datana

yarinya tana rarrafe kusada Hajiyan dasauri tashiga dakin tana kallon hoton, murmushi Hajiya tayi tace "lokacin kina yar tatsitsiya keda Mamanki kunzl ganin gida, little Du'a, jeki yi wanka kizo kici abinci zan baki labarin anjima" gyadamata kai tayi sanan tacire hijabi ahankali tawuce zuwa kofan datagani wanda ta tabbata bathroom ne saida tashiga sanan Hajiya tafita daga dakin.

Saida tayi wanka sanan tafito daure da towel,
akwatin ta dataga anshigo dashi tabude tadauki wata doguwan riga wanda yawanci kayanta dogayen riguna ne daidaikune riga da skirt, saka rigan tayi sky blue ce mai kyau sanan tasaka hijabi salla tayi sanan tazauna tana tunanin maganan Hajiya datace tasauko, tashi tayi ahankali tacire hijabinta ta ijiye  sanan tabude kofa tafito, ahankali take sauka daga stairs tana karabin gidan da kallo, daga sama sama takejin maganan Hajiya da Hamad saikuma takarasa suna ganinta sukai shiru. "kin idar tahonan" tauna mata kusada ita akan dinning hakan yasa ta taho zama tayi wajen Hajiya tace "debi abincin ki kici" dasauri Hamad yace "kafin namanta banfada mikiba kuran nama tazo gidan nan ba" turo baki tayi Hajiya ta harareshi tace "karkaga kana maigida kanemi samin jika kuka sama zamu hau nidakai, ci abinci ki kinji kome kikeso" gyadama Hajiya kai tayi sanan tadebi rice da stew da plantain da fish tanaci, bini bini Hajiya ke kallonta hartaci rabin abincin sanan tasha ruwa haka

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️M SHAKUR

EPISODE1️⃣3️⃣
Har dare hira suke Hajiya da Hamad, kagansu zaka dauka Hamad jikan ta ne, Hajiya wata irin mace da idan kana tareda ita you have no reason or what so ever to hate her ne, kodan sabida yaranta biyu kachal aduniya saisa takeda son mutane haka oho, danta na farko yaranshi uku dukansu Maza kuma kanana dan Mami tariga shi aure yana UK achan yake aiki sai Mami dakeda yara hudu tana aure a kano, Bayan Mami ta haifi wata tarasu, Hajiya is very very educated, lawyer ce babban gaske amman yanzu tai retire saidai she's still an advocate na Human right, batun yauba taso tadauki Du'a, akwai lokacin data kusan kulle Maman Abba wato Kaka, sabida kukan da Mami tamata ne tana rokonta yasa tahakura daga lokacin tai fushi da Mami ta shareta, saisa koda wasa bata taba taka kafarta agidan Abba ba dan batada daukan nonsense and zasuga yanda zata maida yarinyar nan, Du'a tariga tabar gidan nan kenan har abada saidai in bata raye.

Ganin Du'a na gyangyadi akan kujera yasa ta tadata. "Du'a Du'a tashi kije ki kwanta adaki" ahankali ta tashi murya chan kasa tace "saida safe Grandma" murmushi tamata tace "kiyi

alwala sanan kiyi addu'a kafin ki kwanta kinji" gyadamata kai tayi sanan tawuce, dakinta tabude tashiga tamaida kofan tarufe, bayi tashiga tadauro alwala kaman yanda aka umurceta sanan tafito, fadawa kan gadon tayi tana karanto addu'an bacci sanan taja bargo ta lulluba tana rufe ido fuskan mutumin nan tagani yay flashing a idanunta dasauri tabude idanunta tana yaye bargon tafito da kanta waje tanabin dakin da kallo, mutumin daya ciro ta daga rijiya she just saw fuskanshi, lumshe ido tayi ahankali still tana ganinshi saikuma ta girgixa kanta kaman tana kokarin koran abin dan bataso tana ganinshi, ahaka bacci yay awon gaba da ita......

Hajiya tashigo dakin da asuba ganin wutan dakin A kunne, karasawa gaban gadon tayi, zama tayi atabaki bakin gadon tana kallon fuskanta, Du'a is just different! ahankali takai hannunta ta kwashe gashin daya sauka a gefen fuskanta, shafa gefen fuskanta tayi tana kiranta ahankali. "Du'a, Du'a atashi daga bacci asuba tayi" bude idanunta tayi ganin kakanta yasa taji kunya murmushi tayi dasauri Hajiya tace "na tabbata yau zata yalwatu da ni'ima a gareni, wanan kayataccen murmushi dakika gaisheni dashi Du'a, Masha Allah jikata is very beautiful, barakallahu fiki, tashi kiyi alwala kizo kiyi salla kifito kuyi sallama da Hamad yashirya zai tafi" gyadamata kai tayi Sanna tasauka daga gadon ahankali bathroom tashiga itakuma Hajiya tawuce tafita.

Saida tai salla sanan tafito sanye da hijabi, a falo tagansu suna zaune Hamad na rike da mug yanashan coffee, karasowa tayi ta tsugunna ahankali tace "ina kwana Grandma" "kintashi lpy Du'a ya kwanan Abuja" murmushi tayi tace "I love here Grandma, Ya Hamad good morning" "morning dama ke nake jira zantafi" yatashi bayan ya ijiye cup dinshi, Hajiya tace "sa takalmin ki kiraka yayanki" tashi tayi tasaka slippers din da Hajiya ke nuna mata sanan tabi bayan Hamad suka fita daga falon sauka suke daga matattakala kaman daga sama yace "ya akayi kika fada rijiya Du'a" dawani irin sauri takalleshi ta tsaya batare data cigaba da tafiya ba hakan yasa shima ya tsaya yana kallonta yace "answer me" murya chan kasa tace "Muhsin din Ya Nana ne yazo" dawani irin sauri cikeda mamaki yace "Muhsin"gyadamai kai tayi tabashi labarin komi iya wanda tasani, shiru yayi saikawai yay kwafa yace "muje" binshi tayi harwajen mota, sanan ya tsaya yace "be a good girl kinji, kinga yanda rayuwanki take kasancewa awajena maza so be careful kinji" gyadamai kai tayi shafa gefen fuskanta yayi yace "wuce ki koma ciki bye" waving hannu tamai tawuce shikuma yashiga mota yatada yabar gidan bayan security yabudemai gate.

Ahankali da sallama tabude falonsu tashiga, Hajiya na zaune kan kujera tanacin fruits dake cikin bowl akan cinyanta, ganin Du'a ta shigo yasa tanuna mata gefenta tace "zoki zauna anan Du'a" murmushi tayi takaraso wajen tazauna, bowl din tanuna mata tace "zaki sha fruits"? gizgiza mata kai tayi tace "na koshi" murmushi tamata tace "karki damu nariga namiki friends sunje kano ne but maybe tsakanin yau ko gobe zasu dawo zaki gansu yanmata kaman ke zadan su girma miki but I'm sure u will like them" murmushi tayi tace "thank you Grandma"

murmushi tamata sanan tace "yanzu abinda ke mind dina is school, banso kishiga secondary school dan kinyi girma saidai lessons, koda wasa bazakiyi rayuwan kullen nan dakikayi agidan ubanki ba, don't worry I will think of what to do akanki, yanzu dai zansa driver na yadauke ki Razika zata biki kije saloon ama gashin nan lafiyayyen gyara ko amiki kalba ko kitso duk wanda kikeso, sanan amiki gyaran farce right" gyadamai mata kai tayi tana murmushi, Murmushi itama Hajiya tayi tace "answer da naki stop nodding head be acting like a big girl okay" murmushi tayi sosai wanan karan tace "okay Grandma" "good girl, jeki shirya kiduba wardrobe dinki akwai kaya awajen kisa daga nan" harzata gyadamata kai saida sauri tace "Tom" wuce wa sama tayi Grandma tabita da kallo harta bace mata.

Wardrobe din dakin tabude hadaddun karyane wanda mostly abaya ne, dogayen riguna kala kala daban daban, ahankali tadaura hannunta kan wani baki fitodashi tayi daga leda tana kallon rigan kaman Grandma ta aunata shiryawa tayi cikin rigan saikuma dagudu tai wajen madubi tana kallon kanta yanda taga tayi kyau ko Nana su bata taba ganin tasaka doguwan riga mai tsada nan ba, murmushi tayi tadaura dan kwalin saman tadauki hijabinta akai tasaka tafito tasauko kasa Hajiya na ganinta tace "ina gyalen abayan Du'a" dasauri tace "nadaura akai Grandma" dan dariya Hajiya tayi saikuma ta mike tace "zokiga" karasowa gabanta tayi Hajiya ta yaye hijabin dan kwalin ta warware sanan ta gyaramata parking gashin, takalli Razika dake wajen tace "he daukomata handbag a dakinta Razika" da sauri tai sama, taimata rolling gyalen saitai kaman wata balarabiya, saukowa Razika tayi da jaka mai kyau, Hajiya ya karba tabata tace "perfect oya kutafi to driver na waje yana jiranku" takalli Razika tace "stay by her side, saikun dawo, bye Du'a" juyowa Du'a tayi tamata waving hannu alamun bye sanan suka wuce suka fita sai murna take basabamba, mota suka shiga direban yajasu.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

Free page
EPISODE1️⃣4️⃣
Bini bini direban Hajiya dake sanye da uniform ke kallonta tamadubi, hakan yasa Razika takalleta, ganin yanda take kalle kallen hanya tana murmushin nan dake karamata wani kalan kyau nadaban yasa Razika tace "is this ur first time a Abuja Du'a?" juyowa tayi tazubama Razika mayun idanunta dakesa mutum yaji wani kwanciyan hankali harzata gyadamata kai ta tuna maganan Hajiya hakan yasa tace "eh" murmushi sosai Razika tayi tace "Abuja ai nada

kyau, nima Hajiya tadaukoni daga kauyen mu takawo ni nan, sanan akwai lesson teacher dake zuwa mana karatu duk asabar da lahadi, Hajiya nason yara, kinga tunda nake a Abuja bantaba ganin yarinya mai kyau kaman keba" dan murmushi tayi saikuma tadauke kanta tamaidashi kan titi tana kallon motoci dan kunya takeji taji ance tanada kyau bamataso adinga cemata haka, ahankali tace "thank you" "yauwa munkawo" Razika tafadi ganin driver yay kwana yashiga wani babban Plaza, parking yayi hakan yasa Razika tace "sauka muje" bude kofa tayi ahankali tafito tana kallon wajen yanda akwai mutane kowa na shiga da fita abinshi, ko yanda takebin mutanen datake gani da kallo ne yasa taga suna kallonta itama oho dasauri tarike hannun Razika gam data fito tace "muje" tana rikeda hannun Razika suka wuce suka shiga wani hadadden saloon dake nan first floor, ma'aikatan suka taso suna gaidasu kafin Razika tamusu bayanin me za'amata nan aka shiga yi mata gyaran gashin.

"inje insiyomana ice cream a wanchan shagon Du'a" ta tambayi Du'a da ake wankema gashi, murya chan kasa tace "eh" tashi Razika tayi tafice daga saloon din daidai angama wanke ma Du'a tulin gashin aka nannade mata gashin da towel matar tace "tashi muje dryer" tashi tsaye tayi tawuce taje tazauna ana sliding kofan saloon din aka shigo, juyowa tayida sauri tazaci Razika ce, wani Alhaji tagani yaci babban riga milk na shadda dake kyalli da akalla zaikai 60yrs baki dashi mai kyau ga gemu kadan tareda wata mata kana ganinta kaga yar duniya ga hujin hanci akan hancinta guda uku tana rikeda jaka tana taunan cingum tana sanye dawasu kaya dabasu da maraba da babu ajikinta, suna shigowa masu aikin suka taresu. "welcome Alhaji, welcome Hajiya" gyadamusu kai yayi yanabin matan saloon din da kallo one by one, zama matar dake taredashi tayi kan kujera tawani kamo hannunshi ganin ba ita yake kalloba da sauri yajuyo yakalleta jinta kamamai hannu, kashemaai idanu tayi tace "Baby kagaya musu style din da za'a min" washe baki yayi yace "kai wlh mata kun iya rigima yanzu style ne sai an tambayani, ninasan kan style ne" kallon yar aikin dake gabansu yayi wacce ke jiran bayanin su kafin sufara aiki yadan lashe baki sanan yace "okay bari muga" juyawa yayi yacigaba da kallon yan shagon, Du'a yanuna da akema rolling gashinta a roller za'a sata a dryer yace "how about that fine baby style, Zinariya kinason style din"? yamata tambayan still yana kallon Du'a da akema gyaran gashi wacce ko kallonsu ma batayiba madubi take kallo tana kallon abinda ake mata akai wanda is new to her tabama kofa baya, ganin inda yake kallo yasa Zinariya tace "katafi meeting din dakake dashi Sweet, idan kagama saika biyo kadaukeni" tai maganan tana shafamai hannunshi still datake rikedashi, dan juyowa yayi yakalleta kaman wanda ya manta da abinda ke gabanshi yace "ohh meeting dinan, to,to bari inje, saina dawo" yay maganan yana juyawa bude kofan yayi harzai fita saikuma yadawo dasauri yawuce wajen kujeran Du'a ya tsaya tagaban wajen yana facing nata directly yakare madubin datake kallo yana murmushi yana kallonta kaman yanda takedan kallonshi atsorace yace "nace nawane kudin gyaran kan Zinariya"? Ya tambayi mai gyaran kan Du'a yana kallon Du'a kaman wani tsohon maye wanda baitaba ganin mace ba sai akan Du'a, Mai gyaran gashin Du'a dake kallonshi ne itama cikeda girmamawa tace "all payments are done to Christy Alhaji gatachan the cashier" tanunamai wacce ketare da Zinariyan shi data daure fuska tana kallonshi, yana kallon Du'a still yace "in that case ba matsala, by the way young lady ur hair is beautiful" yama Du'a magana yana wani kalan kallonta, sai alokacin Du'a tadago kanta ta kallai da kyau wanan sa"an Abban tabe hakan

yasa tamai shiru, wani irin hadiye yawu yayi yana lashe baki murya chan kasa yace "bala'i Allah yayi mace anan" rasa yanda zaiyi yasa yawuce yawayance yana kallon Zinariya yace "natafi Baby" yawuce yafita ya shiga hadaddiyar jeep din da aka kawosu ciki daidai lokacin Razika na shigowa rikeda ice cream guda biyu tazo inda Du'a take tamika mata tace "gashi" hannu tasa takarba tana murmushi tace "thank u" gajeren tsaki Zinariya tasaki tadauke idanunta dagakan Du'a kishi nawani irin turnuketa kaman taje tashake yarinyar takeji tadai daure dantafi karfin karaman yarinya haka.
*********

Kano!
Tundaga nesa yake hango yanayin Ammin shi dake tsaye achan baya, jiyayi ranshi yabaci sosai, ahankali yakalli Sharif dake tsaye gaban kantar Max Airline yace "collect the ticket" sanan yawuce yana tafiya daidai kaman dan Sarki, yau yana sanye da native kaya dasukamai kyau ba kadan ba, farin yadi yasaka anmai dinki jumper daya zauna ajikinshi chass, kafanshi yasa wani takalmin Dior mai kyau black dakeda igiya, gashin kanshi dinan as usual looking so coily and black, idanunshi yasaka bakin shade dan baison kallo sosai sai kamshi yake zubawa, wucesu Aneesa yayi batare daya kallesu ba yakarasa inda Ammi ke tsaye tana daddanna wayanta tasanya wani hadadden abaya mai tsadan gaske, dayake tabashi baya ko kadan bataji zuwan shi ba dan hankalinta ma yayi nisa dan tunani take, zuba hannunshi yayi a aljihun wandonshi yana kallon screen din wayanta dan yafita tsawo ganin number datake kira da akai saving da Maigidana yasa murya chan kasa yace "Ammi" firgigit tadan waigo ta kalleshi saukar da wayan tayi dasauri gudun kar yaga number datake kira tace "is it time for boarding already son" shiru yayi yana kallonta, saikuma ahankali yakai hannunshi yacire glasses din idanunshi yace "Ammi baki gaji da kiran mutumin nan ba eh?" dan murmushi tayi dakana ganin murmushin kasan na damuwa ne tace "inaso na sanar dashi zamu dawo Abuja ne dama, kaga yakamata yazo yaduba mahaifinshi baida lafiya fa" cikin dan bacin rai yace " Ammi yafiki sanin mahaifinshi baida lafiya idan baizoba ki shareshi shiya sani, Ammi kidena sa kanki a damuwa, what if u fall sick eh? ina zansa kaina" tunda take maganan take kallonshi, ganin ranshi yabaci na damuwa yasa tai murmushi tace "wayagaya maka ina cikin damuwa eh, I'm fine kawai dama sabida Dadda kane nadamu, oya maida glasses dinka kafo kyau ahaka, mata sukaga this ur no nonsense eyes bazasuyi approaching dana sunce suna sonshi ba" dan murmushi yamata daya karamai wani irin kyau saka glasses din tayi tace "oya muje to, come here lemme hold ur hand asan nine maman this handsome boy" turobaki yayi yace "Ammi kindaiga akwai yara anan ko karkisa su rainani" yay maganan yawuce dasauri kafin tarikeshi zuwa wajen Sharif dakechan, binshi da kallo tayi saikuma takarasa inda su Aneesa suke tace "let's go girls gobe sai makaranta" duk dariya sukayi, Aneesa tace "Ammi kince zakicema Ya Asad ya chanza min waya in munkai" gyadamata kai Mami tayi tace "eh dukanku zansa ya chanza muku" ganin Sharif namusu waving hannu yasa Ammi tace "kumuje" wucewa sukayi saba ko 3min basuyiba sukai boarding jirginsu zuwa Abuja.

Suna sauka airport motoci biyu sukazo dukansu, shiga sukayi yayi Ammi takalli Asad dake kusada ita tace "gobe zaka fara shirye shiryen aiki ko" gyadamata kai yayi yace "eh gobe ne, illustrator dinmu Ammi yasami accident a hannunshi I don't know how am gonna start looking for new one, gawanan TV program dinan dazan fara dukshi yabatamin schedule" ahankali tace "don't worry komi zai daidaita I trust my son" harsuka karasa anguwansu, wani hadadden gida aka bude musu shiga sukayi gidan ya bala'in hadu, sassakowa sukayi Security gidan nashiga da kayansu ciki shikuma yay hanyar flat dinsu, binshi da kallo Aneesa data fito daga motansu tayi, fitowa Mariya tayi tace "yarinya kin debo ruwan dafa kanki" juyowa tayi takalli Mariyan cikeda tsiwa tace "mekike nufi?" Ammi dahartai gaba tajuyo ta kallesu tace "to bismillah tsiya zata fara ne" dasauri Aneesa tace "Ammi Mariya ke tsokana na fa" murmushi Ammi tayi tace "barta kinji Aneesa zomuje" dasauri Aneesa tabita tanama Mariyan gwalo itakuma tai dariya zata mata gwalo Rahima ta ture mata meya tace "dalla wuce mutafi"  wucewa tayi tana turo mata baki sukai flat dinsu.

Hadadden Babban falo ne dayaji komi na duniya, stairs sukayi, sukai dakinsu daya hadu sosai irin dakin mata Ammi tashiga dakinta, ahankali ta ijiye handbag dinta tazauna kan gado tai shiru saikuma tamika hannunta tadauko wayanta dake cikin handbag din tai dialing number datai saving da my husband, har wayan tai ringing ta katse ba'a dagaba, sake dialing number tayi wayan na gabda tsinkewa aka dauka dasauri tace "Alhaji wanan wani kalan haline kakeyi? children are all at home, Asad is back yau kusan 5days kenan ina kiranka baka dauka what is all this Alhaji bazaka zo kaduba iyalanka ba? Eh?" muryan mace taji tawanija tsaki mtswwww..... cikin muryanta dayakedan shake da alamu bacci suke tace "dalla Malama karki sake kiran number nan kinwani hana mutane bacci, yabaki kudi yasaki gida mai kyau, aikinki shine zaman gida u are a house wife, ki kulada gidanshi da yaran kanninshi daya mutu that's ur work and leave him alone, yana nan ina kula dashi, ki ganshi nan ma bakinshi kan tsayayyun nonuwana yana tsotsa yana bacci ba irin naki ba daya koma kaman silipas" wani irin tari Ammi tashigayi batasan lokacin data yarda wayan akasa ba yafadi kuka taji tanaji but batason yaranta suji tana kuka ko su ganta jitayi duniyan tamata zafi dasauri ta tashi bude kofan dakin tayi tafita sauka kasa tayi tafice compound security na ganinta yabude mata kofa murmushi dole tamai tace "idan yarana na nemana tell them nashiga wajen Hajiya, Mamana" Gyadamata kai yayi yace "yes ma" fita daga Gate din tayi, ko tafiyan kafa goma batayiba ta tsaya gaban gate din gidan dake gaban nasu, knocking tayi security gidan yabude kofa yana ganinta yace "welcome back Ma" murmushi tayi tace "is Hajiya around" "yes she is" dasauri tashiga gidan direct kofa tabude tashiga Hajiya na zaune kan kujera tana duba wani magazine idanunta da glass sai yar aikinta dake goge TV stand, jin sallama yasa tadago kanta takalli Ammi datai sallaman, fadada murmushin fuskanta tace "Walida" ahankali muryanta narawa sosai tace "Haj.....iya" tashi Hajiya tayi dasauri ahankali takaraso gaban kofan tana kallon fuskan Ammi ganin yanda idanunta suka cicciko da hawaye yasa takama hannunta tace "muje sama" tana rikeda ita sukai sama har zuwa dakin Hajiya, shigarda ita ciki tayi sanan tamaida kofan tarufe kafin ahankali takama hannunta ta zaunar da ita kan gadonta tace "ya isa Walida ya isa" wani irin rungume Hajiya tayi gam, duk duniyan nan batada wacce tarike amatsayin uwa sai Hajiya, saisa babu abinda take boyemata, Hajiya bata hanata kukan ba saidai bubbuga mata batada takeyi ahankali tace "it's

okay ya isa" tadade ahaka sanan tadago kanta, tissue Hajiya tabata fuskanta tashiga sharewa tace "Hajiya babu narasa Yaya zanyi da Baban Asad, gabaki daya baida lokacin iyalinshi, har muje kano munyi sati mudawo mutumin nan baizo yaduba mahaifinshi ba, yana nan Abuja fa amman yakauracewa gidanshi, kullum ina cikin yima yara karyane yay tafiya wanan kasan yay tafiya wanchan kasan, Hajiya Asad danshi ya tsani mahaifinshi sama da komi, kinsan bakin halin Asad koyaya naso nawanke mahaifinshi bayama yarda bama ya saurarena, nasan Asad kadai na haifa wlh Hajiya ke shaida ce anan falon ki ranan nace na yarda ya karo aure ba hanashi kara aure ba, Hajiya yaki sai bin matan banza, kince idan naje kano nabada sanarwa masallatai asashi a addu'a wlh duk nayi, baya daukan wayana yanzun nan nakirashi wata karuwanshi ce tadauka, I don't know what to do Hajiya, ina zansa raina inji dadi eh? Baban Asad yana girma yanakara tambarewa shekaranshi 60 fa yanzu".

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️M SHAKUR

Free Page
EPISODE1️⃣5️⃣
Hannu Hajiya tasa cikeda tausayinta tace "stop crying, dena kuka, ya isa" tasata ajikinta tana bubbuga bayanta tana gayamata kalamai masu sa natsuwa hartai shiru, saida ta natsu sanan Hajiya tace "bari nakawo miki abinci kici nasan is being long bakisa abinci acikin nan naki ba" batama tsaya sauraronta ba tawuce tafita, lafiyayyen tuwo takawo mata da miyan kubewa busassa da kifi da man shanu, bude kofa tayi tashigo dakin tana kallonta, maida kofan tayi tarufe takaraso ijiye tray tayi akan carpet tace "wayyo jikin tsufa, sako kici kinga kinsani aiki" murmushi tayi ahankali sanan tasauko tasan halin Hajiya hakan yasa batai gaddama ba tashiga cin tuwon sosai taci tuwon ta koshi sanan taje tawanko hannunta anayi tafito carpet din Hajiya tanuna mata hakan yasa tazo tazauna kusada ita, ahankali Hajiya tace "Walida, ke yanzu ba yarinya bace, inda ace Asad yayi aure da yanzu kinada jikoki dozen ma halan" dan murmushi tayi Hajiya tace "my point is indai rayuwan zaman aure ne you've come a long way saidai kibama wasu shawara, kunada yaro dakeda shekaru 33 aduniya aiko littafi aka baki zaki iya rubutawa kan zaman aure, Baban Asad wanan halin nashi bayau ko jiya yafara ba, kinyi kuka kinyi kuka Walida, kukan jini ne kawai yarage bakiyiba, kinsan yanayin lafiyanki, amatasayina na mahaifiya agareki dudda bani na haifeki ba abinda nafadi miki kafin kutafi kano shizan kara gayamiki ki manta da batun mijinki and concentrate akan yaranki, fi fawwalama Allah lamarin Baban Asad kidinga mishi addu'a idan yanada rabon shiriya wlh zai shiryu, kinsan yanda Asad

ke sonki sama da rayuwanshi ko ciwon kai yaron nan yaga kinayi lamarin shi saiya tabarbare yaron dayakeda TV show dazai fara nan da kwana biyu, I think, kinason ya susuce ne"? Dasauri Ammi tace "a'a Hajiya" "then dole ki jajirce ki kauda komi, Alhamdulillah baihanaki ci ba baihanaki shaba, ke kodama yahanaki danki Allah ya horemai mezai dameki, ki share batun shi yanda yasa kafafunshi yafita dakanshi zaisasu kuma yadawo gidan kinji" harcikin ranta taji wani sanyi wani zubin takance inama ita yar Hajiya ce, dan Hajiya tayi arayuwa, tadauketa tamkar yar cikinta, haka tadauki yaranta tundaga su Asad da Sharif harzuwa kansu Aneesa kaman jikokinta, babu abinda abinda take iyayi bata sanar da itaba, murmushi tayi ahankali tace "Hajiya nagode, Dadda da Turai sunce na gaisheki" haba Hajiya takama tace "wanan rigimammen tsohon yanzu bai biyoku yadawo nan Abuja yadinga ganin specialist bako" dariya tayi kaman ba itane tasha kuka ba tace "ai yace shi kano yakeso, Turai natare dashi dakuma Nurse dinshi, ya samu lafiya sosai kafin mudawo ma" Hajiya tace "Masha Allah".

"Grandmaaa" Du'a data shigo falon takira Hajiya ganin bata falo, shigowa Razika dake biyeda ita tayi tace "tana sama, muje kinuna mata kalban da aka miki" dasauri Du'a tai stairs tana murmushi sosai dan kitson da aka mata yamata kyau dan ba'a taba yimata kalanshi ba, tana kaiwa falon sama takara kiranta. "Grandma" dasauri Hajiya take tareda Ammi tace "jikata tazo bangayamiki ba, Du'a gani nan adaki shigo" bude kofan dakin Grandma ahankali tayi tashigo Razika biyeda ita, ganin wata babbar mace baka tareda Grandma yasa ta tsaya batare data karaso ba, saukar da kanta tayi kasa ahankali ta gaida matar  tace "ina yini" murmushi Hajiya tayi takalli Ammi tace "ana gaidake" wani kayataccen murmushi Ammi tayi tace "Masha Allah, sabida kin ganni kikaki karasowa ciki wajen Grandma dinki" dan murmushi Du'a tayi cikeda kunya ta girgixa kai saikuma tajuya dasauri tace "bye Grandma" sanan tabi ta gefen Razika tafice dasauri, dan dariya Hajiya tayi tace "kinganta haka take akwai kunya" takalli Razika tace "anmata kitson" gyadamata kai tayi tace "anyi kalba akayi, yayi kyau sosai" "haka nakeso, jeki bata abinci taci" ficewa Razika tayi, Ammi tace "Hajiya yar Muktar din UK ne" dariyan manya Hajiya tayi tace "yar Zainab din kano ce, Du'a, wacce nake baki labarinta" murmushi Ammi tayi tace "Allah sarki Yarinyar ga kyau ga natsuwa"

Saida tai wanka sanan ta chanza kaya zuwa wani gown data dauka daga wardrobe red iya guiwa ya tsaya mata yamata kyau, bata daura dankwali ba tasaki kalaban dayake nan har waist dinta kaman ansaka mata attachment tabude kofa tafito da saurinta ta sauko dan itada Razika sun biya wani super market tadauki drawing book babba da HB Pencils da eraser da colors, dakin kasa wanda shine dakin Razika da Amina ta shiga suna zaune sunacin abinci duk suka bitada kallo ganinta adakinsu, Razika ta kalla tace "ina drawing book dina"? Dan ware ido Razika tayi sanan tace "inama nasa ohh natuna suna dinning" dasaurinta harda dan gudunta tawuce tafita a dinning ta tsaya ganin komi yasa tasaki wani murmushi she's so happy and excited bayan reading novels wanda technically Ya Hamad ne yakoya mata the only thing datasan ta iya shine zane, babu abinda bata iya zanawa ba saida yawanci abinda tafi zanawa

yanzu shine takalma tana bala'in son zama takalma sabida batada takalma agida dayawa dan bata fita saisa hakanan idan tazauna saita dinga zama dream shoes dinta.

fitowa tayi tazauna akan falon, bude komi tayi, tai sharpening pencil dinta sanan tabude hadadden drawing book din da Razika tasiya mata ta shiga zane, yanda take zanen kadai saika tsaya kana kallon hannunta sabida wani kalan burgewa datake yi kafin good 3min tagama zama wani tsantsararren takalmi hill na mata, murmushi tayi tadauki drawing book din tana kallon takalmin saikuma chan ta hura iska sabida all particles na eraser dakekai yafita sanan tace "to yanzu wani suna zansa maka kai takalmin nan kaga nadade banyi drawing ba tunda drawing book dina na gida yacika Ya Hamad baikara sayomin ba" shiru tayi tana tunani kawai saita sauke drawing book din akano saitama zanen tittle Du'aXAbuja, kallon rubutun tayi dayay kyau, kawai saita bude wani page tashiga zana wani daban.

Ahankali Ammi datai sallama da Hajiya ke tafiya kan stairs Hajiya bata rakota ba sabida wani office related call da aka mata, tundaga stairs take kallon Du'a, dudda batasan metake zanawa ba but ganin drawing book yasan tasan zane take, kitson kan yarinyar tabi da kallo da yanda take zane ita kadai saita daga ta kalla tai murmushi tasauke tacigaba, hakanan Allah mai daurama mutum so da ki kawai taji Du'a na burgeta tanason yarinyar, karasa saukowa tayi Du'a ma bataji saukowanta ba sabida yanda hankalinta yay nisa, karasawa cikin falon Ammi tayi ta tsaya tana kallon takalmin da Du'a ke zanawa batasan lokacin datace. "Masha Allah, you are gifted Du'a" dasauri Du'a tadago kanta ta kalli Ammi, murmushi tayi sosai tace "Mum yayi kyau"? Hakanan Ammi batasan mesa ba but kiranta da yarinyar tayida Mum yasa son datake mata ma yay double da sauri tazauna kan kujeran dake gefen Du'a tamika mata hannu tace "bani drawing book din naga" da sauri Du'a tadauki drawing book din tamika mata sanan ta matso kusada kafan Ammi ta daura hannayenta kan cinyan Ammi batare datama sani ba tana kara leka drawing din itama, gyara zama Ammi tayi jin yanda yarinyar ta dagata tafara duba drawing din daga farko tace "wow, haka kika iya zane Du'a, this is talent wlh" murmushi tayi sosai dan batasaba ayabeta ba agidansu Ya Hamad ne kawai yake cewa zanen ta yay kyau, murmushi takara yi tace "Ya Hamad ne kadai yataba cewa inada talent sai ke Mum" takarashe maganan looking damn happy dayasa Ammi taji suka matsalolinta ma sukau, hannunta takai tashafa kan Du'a tace "you are very very talented Du'a, kinsan nawa ake biyan wayanda suka iya zama abu haka" girgixa mata kai Du'a tayi tana kallon Ammi saikuma tace "Mum ni ai baza'a biyani ba, kinga banyi school ba a JSS2 na tsaya, wanda yay karatu ne ai ake bashi aiki ko"? tunda take maganan Ammi ke kallon yarinyar, idan tana magana sosai zakaga rashin wayau da yarinta aciki wanda yarinyar dakeda shekarunta bai kamata ace hakan yasameta ba, murmushi Ammi tayi tace "ko ina talent yake yanada kyau ayi acknowledge nashi, and it doesn't matter sabida kin tsaya da karatu a JSS2, with this" Ammi tanuna mata drawing book din tace "with this zaki iya samin aiki a companies da dama that are into shoes kuma abiyaki" wani irin kyalkyacewa da dariya Du'a tayi tawani kife kanta akan kafan Ammi tanajin dadi sosai data kasa boyewa dayasa Ammi takarajin tashiga ranta, Hajiya data dade a stairs tana jinsu takaraso tazauna kan kujera tace "ke karki karya ma mata cinya inba so kike Asad yashigo yay yaki dani

ba kirufamin asiri yaron nan son maman shi yake kaman me" dariya sosai Ammi tayi tace "kundai fi kusa kedashi Hajiya" tashi Du'a tayi tana murmushi itama, Ammi tace "how about natafi da wanan drawing book din sabida nasaman miki aiki dashi" dawani irin sauri ta gyadamata kai tace "eh Mum kutafi dashi" tawani washe baki tajuya tana kallon Hajiya dake kallonsu itama tana murmushi tace  "iyye Du'an baaa, tobazakima Mum din naki godiya ba za'a neman miki aiki kinata washe baki" cikeda farin ciki takalli Ammi tace "Mum nagode Allah amfana" tashi Ammi tayi rikeda drawing book din tace "bari nashiga gida" Takalli Du'a tace "yaushe to zakizo ki gaidani agida inada yammata nima kinga saikiyi sababbin kawaye ko" juyawa tayi takalli Hajiya dake kallonta tace "yo jama'a kome aka tambayi yarinya sai tajuyo takalleni, Razika da Shemau sa rakota suzo gobe" "shikenan, Hajiya sai munyi waya" "tom Walida ki gaidamin da Sharif dasu Aneesa, shikuma gogan kice nace Allah yataroshi" dariya Ammi tayi tana bude kofa tace "yau dai munjiku arana kuda ba'a shiga tsakanin ku" Jan kofan tayi tarufe tafice.

Hajiya ta kalli Du'a daketa murna tace "zansa driver yasayo miki wani sabon drawing book, kinci abinci"? girgizamatakai tayi tace "a'a" dasauri tana hararanta tace "tashi kije kici abinci banson kina wasa dacin abinci, anjima idan zasuyi girkin dare saiki bisu kidinga ganin yanda sukeyi ko" murmushi tayi looking so happy tace "tom grandma" sanan ta tashi tayi dinning dasauri Grandma tabita da kallo daga zuwanta harta fara murmurewa kwanan nan zatai kiba tai kyau abinta.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE 1️⃣6️⃣

Koda Ammi ta shiga gidan Sharif kawai tagani zaune a dinning yanacin spaghetti da Rahima tadafa, yana ganinta yace "Ammi ina kikaje" zama tayi akan dinning tace "daga wajen Hajiya nake" takalli Rahima data fito daga kitchen tace "iyye yammata na angirma harkinyi girki" murmushi tayi tazauna kusada Ammi ashagwabe tace "Ammi please sai next Monday zamu resuming school this week muhuta muyi shopping kinji Ammi" Sharif dakecin abinci ne yahararеta yace "why mesa yaran this generation basason school saison kula samari" murmushi Ammi tayi takalleta tace "bazakuyi lectures bane" ahankali tace "first week lectures baya serious sosai Ammi fa"gyadamata kai Ammi tayi cikeda gamsuwa tace "okay I will think

about it inasu Aneesa da Mariya"? tabe baki tayi tanajan plate tace "sunyi bacci" kallon Sharif dayagama cin abinci Ammi tayi tace "ina Asad" ajiye cup din dayake shan ruwan dashi yayi yace "dazun nan yafita, bansan inda yajeba"  "Ammi wai yaushe Daddy zai dawo" Rahima dake kusada Ammi tamata tambayan, murmushi  Ammi ta kakalo tace "this week ko next week, bari kiga naje na kwanta" ta tashi tawuce sama Sharif yabita da kallo.

Wani dankareren building wanda nan a offices din senators na Nigeria suke ya dumfara cikin mad ride dinshi na Benz, tsayarda shi sojojin dake guiding building din sukayi, ahankali yasaukar da glass din motar, ganin wanda keciki yasa suka shiga gaidashi, Jan motar yayi ciki har zuwa inda ake parking yay parking sanan ya kashe motar yafito, wanan karan yana sanye cikin wani classic 3quater wanda dakadan yawuce gwuiwanshi dark blue color, sai wata white t shirt mai V neck dayasaka  data kara fitar da kyawunshi kana iya hango kwantaccen gashin kirjinshi ta wuyan rigan sabida shape din dayake dashi na V, kafanshi Sanye cikin flat slippers na Gucci, kanshi ya sanya p cap na Gucci, lips dinan nashi yay pink yir looking damn moist and fluffy, sai black eye glasses na Gucci a idanunshi, hannunshi ya daura agogo da bracelet na Rolex akai sai zuba uban kamshi yake, kana ganin shi kaga irin yaran masu kudin nan yan gayu looking casual sabida yau Sunday, maida kofan motan yayi yarufe sanan yafara tafiya ahankali yashiga cikin premises din babu kowa ciki sai security personnel dake gadin wajen wanda dazaran sunganshi gaidashi suke dan sunsan koshi waye, elevator ya shiga zuwa 5 floor, wanda yasadashi dawani mahaukacin building dazaki dauka ataurai ne, ga kujeru na ma'aikata amman sabida yau Sunday babu kowa, cigaba yayi da tafiya zuwa gaban wani hadadden kofa wanda da finger print ake bude kofan, baiyi yatsanshi yasa abin yayi magana Authorize Mr Asad,  kama handle din kofan yayi yatura kofan yashiga tashi daya, wani irin zabura mutumin yayi yasauka dagakan yarinyar dayakekai dataji uban attachment ja akai yanajan boxer dinshi dayadan sauke kasa kadan dama dagudu yana rufe abin datai wani automatic kwanciya jikinshi na mugun bari yakalli yarinyar da babu kaya ajikinta yana mata ihu. "leave this office, I said leave" Ahankali yaja kafanshi baya kadan bazaka taba iya tantance wani yanayi yakeba sabida glasses din dake kan idanunshi, dasauri mutumin daya rude yace "Asad look is not what u are think......" awani irin zuciya Asad yajuya fuuuuu, dagudu mutumin yashiga laluban kayanshi yana sakawa batare dayabi takan karuwanshi dake sa kayanta arude ba yasa riganshi baima tsaya saka malum malum ba yazura slippers din office yafice dagudu, sauka kasa yayi gudun da yakeyi yasa yacimmai shan gabanshi yayi yace "Asad listen to me listen to me son please" tsayawa yayi chak yana kallon mahaifin nashi dat so much disgust him now, ahankali yakai hannunshi yacire glasses din dake kan idanun nashi yace "wanan ne US din dakaje ko Dad? Almost 2month babu wanda yasaka a ido kana garin nan Dad" juyawa mutumin yayi yana kalle kalle ganin babu mutane inda suke yasa cikin muryan lallashi yace "listen to me Asad wlh naje US ba karya nayi ba kawaidai dana dawo banje gida bane" wani irin kallon mahaifin nashi yake kallon bakin ciki da tsantsan tsana, Dan murmushi mahaifin nashi yayi irin na marasa gaskiya, cikeda lallashi yace "how are you my boy? Your Mum told me kadawo kaima kaje kano gaida Dadda ka, sanan zakai hosting show ma Youth a TV station, I am so proud of you Asad dina, you are really my son" sosai idanunshi sukai ja ruwa yacika a idanunshi fall ahankali yace "why

are you doing this to Ammi? After all the sacrifice da Ammi tamaka why are you treating her this way, why are you maltreating my Mum Dad eh"? kana ganin yanda yayi maganan kasan zuciyanshi namai zafi da daci, ganin yanayinshi yasa Baban yadan sosakai yace "listen Asad, inamaka kallon yaro but I think u are not more a little boy anymore, I love you morethan anything in this world, in fact ma darajan kane ma yasa nai deciding I will leave tareda mamanka har karshen rayuwa but banason mamanka Asad, ko kadan bani sonta, auren hadi akamana nida ita, ur Mum was never my choice, choice din Daddan kane, yar maigadin shine dayarasu dagashi har matanshi lokacin sunje gida kauye suna dawowa suka sami hatsari suka rasu, shine sabida how the gateman was good to Daddan ka yasa yadauki maman ka shida Mamana Allah yajikanta suka raini mamanka aka sata a makaranta aka hadani aure da ita dudda na nuna banso..." yanda idanun Asad sukaija zaka dauka zai makance ne, cikin wata irin murya datai rauni bama ta fita sosai tsabagen bakin ciki da kunci yace "is that the reason why kakebin all kind of useless matan banzan Abuja nan Dad" Dasauri yace "banason aure aure, da mata daya zan iya rayuwa since uwarka ce d lucky one saisa I am stuck with her,  look son I don't wanna go into details with you now, nan gaba u will understand after all kai d'ana ne, my blood runs through ur veins, you are just like me" cikin wani irin huge voice yace "I will never be like you, bazan taba zama mutum irin ka ba, I despise you Dad, u are nothing but a shame to my name, wlh da ana chanza uba dana chanza ka cus u don't deserve a son like me much less a good wife kaman Ammi na" yana maganan yawuce yabude motan shi yashiga yana kokarin tadawa Dad yazo wajen. "Asad, Asad, come here son calm down nasan ranka abace yake, but yakakeson nayi eh ur Mum is such an old school babu abinda ta iya sai kunya, Asad" wani irin jan motanshi Asad yayi yabar wajen ubanshi na kwalamai kira. "Asad, Asad" tsaki yaja yadafa kanshi yace "yaro sai bakin zuciya, nima maiya kaini zuwa office yau" tsaki yayi shi kadai yace "to nasan zaizone yaron da fushi yake dani kona kirashi baya dauka" tsaki yasakeyi dukya bala'in damu yace "daka tsaya kajira Zinariyan ka daganan ma kona sami contact din kyakkyawan yarinyar nan dayafimin, yanzu look what I cause yanzu, shiit yanzu sai nakoma wajen wanan matar nan da nonuwan kirjinta sunfi silifas tsawo abu har cinya, dan Allah dai jibi nonon wanan cinyare dinan atsaye, na Zinariya ma haka, amman ace yaro yakasa ganewa uwarshi ba gaba ba baya gatanan ne gabaki dayanta zero ce" yaja tsaki yawuce yana tafiya zuwa ciki ranshi fall da damuwa.

Allah da ikonsa ne kawai yakawoshi gida lafiya, ko parking din kirki bai iya yayi ba yafito daga motan dawani irin gudu security su yace "subhanallah" ganin motan na tafiya yashiga yay parking da kyau shikuma Asad yay wucewan shi batare dayama juyoba, ko katon Sharif dake zaune a garden dake kusada flat dinsu baiyiba yawani irin buga kofa yashiga ciki, binshi da kallo Sharif yayi saikuma ahankali yasauke ijiyan zuciya yacigaba da aikin dayake yi akan system, karan zubarda abu dayaji yasa yatashi da sauri ya ijiye system dinshi awajen, bude kofa yayi yashiga falonsu sanan yamaida kofan yarufe yay kitchen dinsu da sauri tsayawa yayi awajen kofa yana kallon yanda Asad ke zubarda komi na kitchen din yana rotsasu akasa kaman wanda yazare, cikeda damuwa Sharif yace "what's wrong with u Asad"? Wani irin daga kafa Asad yayi yadaki fridge din kitchen din cikin zafin harshe yace "it's none of your business leave

me alone Sharif" shiru Sharif yayi yana kallonshi yanda yake haukanshi shi kadai wanda is not new to him, kowa yasan Asad da zafin zuciya haka Ammi ta haifoshi da halin nan.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

Freepage

EPISODE1️⃣7️⃣

Yagama barinshi duk basu isheshi ba ganin yafara punching kofa da hannunshi yasa dasauri Sharif yashiga kitchen din wani irin kamashi Sharif yayi yasashi ajikinshi ya rungume tsam yace "calm down Asad ba Ammi tace idan ranka yabaci kadinga salati ba, calm down please" kokarin fizge kanshi yake yana ihu. "I said leave me alone Sharif, stay out of this" kankameshi sosai Sharif yayi with all the power he got yace "Ya isa Asad I am here for u, I am here, we gonna be brothers forever okay, ina kaje? what happen? Giran da kayi dazu ina kaje?" shiru yayi yakasa magana ahankali Sharif yace "you went to see Dad ko"?Murya chan kasa yace "I guess kaima kasan babu wani US din dayaje" shiru Sharif yayi sai chan yace "before muje kano lokacin kana UK I saw how worried Ammi is yasa naje office naduba shi, I saw him though shi baiganni ba baisan naganshi ba" shiru Asad yayi saikuma gently yatashi daga jikin Sharif zama yayi akasa ahankali yajingina da cabinet din kitchen din idanunshi sunyi jajir, zama shima Sharif yayi kusadashi yana kallon kasan wajen, ahankali Asad yace "I don't know why Dad choose this life he's 60 but jin kanshi yake kaman dan 20, that Oldman is lost Sharif completely, can u believe niyake gayawa I am just like him eh Sharif" yay dan shiru idanunshi sunyi ja yace "I  can never be like that man, bazan taba neman matan banza ba, wlh bazan tababa cus I hate them kyama ma suke bani, I hate that I am his son, wlh da ana chanza uba da na chanza nawa, I hate that man Sharif" kallonshi Sharif yake bakaramin tausayi yabashi ba matsawa yayi kusada shi ya jingina da cabinet shima yace "bazaka taba zama kaman shiba that I am sure of Asad but we gonna do something right now" yay maganan ahankali yace "inaso ka share batun Dad for now dan is affecting u physically and mentally bayan kasan u need to be at ur best gobe zaka fara TV show dinka eh Asad, this whole mess will affect ur productivity as well as ur performance, I cannot be managing everything for u eh, u need to be at ur best mugama this TV program in the next 7days sabida kasamu muyi concentrating a office we need to release new collection eh Asad, banda ma haka kanason Ammi taganka ahaka ne kaga how I am better than u kenan, tunkafin mutafi kano nasan Dad na garin nan amman koda wasa ban nunama Ammi ba sabida I need her happy, kaiko look at u now bayan kasan mu Ammi ke gani taji dadi common be a man for Ammi, let's keep pretending we don't know what Dad has been up to koma yana gari" Ahankali yasaki dan murmushi saiya kalli Sharif din yace "kasami wanan illustrator din?" girgizamai kai yayi yace "no he's on his summer break wai, kaima I don't get u Asad why don't u wanna give Nigerians dinmu a chance" "cus they can't give me what I want" hararanshi Sharif yayi yace "shikenan haka zan zuba idanu inta kallonka wlh idan ka shiga tight corner kaida

kanka zaka dinga neman su" tashi yayi ahankali yace "don't worry I will get one" fita yayi daga kitchen din Sharif yabishi da kallo cikeda so dakuma tausayin dan uwan nashi yasan wani zubin Allah kan jarabci yara da iyayensu and that's Asad da dukansu ma a family nan biggest test, Dad gashinan ne kawai living one kind of useless life kaman yaro, imagine Babba dashi he is willing yayi karya yabar gidanshi da sunan yatafi UK just dan yatafi wajen matan banzan shi, tsohon mahaifinshi baida lpy he don't care yaje yaduba shi saidai yayta tura kudin magungunan shi, ayanzu kuma shi kadai ne dandan Dadda namiji, dan dama Dad ne Babba sai mahaifinsu daya rasu, sai Anty Turai mahaifiyar Aneesa, Mahaifinsu daya rasu ne kawai ya haifi yara dayawa a family Shine first born sai Rahima sai Mariya, itakuma Aneesa ita kadaice yar Mamanta Turai, da mijinta yasakota tadaukota suka dawo gidan Dadda dazama kafin tabama Ammi ita aka zo da ita Abuja tafara school gudun kar mijin ya kwace ta dan Anty Turai yar rigima ce fitinanniya saisa ma takasa zaman gidan miji.
Banda haka Ammi is just the best woman aduniyan nan, sosai take tarbiyan yaran batare data nuna gazawanta ko gajiyanta ba, hasalima bala'in son yaran take suma haka suke sonta dan wajen Ammi yafi musu ko'ina.

Mikewa Sharif yayi ahankali yanabin kitchen din da kallo, kwashe abubuwan dabasu wani baci sosai ba yayi sanan yawuce yafita, sama yayi ahankali yabude kofar dakin Asad din, akan gadonshi ya ganshi yana bacci, ajiyan zuciya yasauke sanan yaja kofan yarufe yasauko kasa, masu gyaran gidansu yakira yasasu gyara kitchen din sanan yakoma falon sama yazauna tunawa ma yayi da system dinshi awaje dasauri yatashi yawuce waje.

Dayake tanada yammata hakan yasa Ammi bata dauki yan aiki ba, su take sawa girki, duk tana kitchen taredasu suna aiki takalli Aneesa dake wanke rice tace "namuku kawa fa" dasauri duka yaran suka tsaya suna kallonta, Aneesa ce tace "Ammi a ina"? murmushi Ammi tayi tana maida marfin tukunyan data bude tana rufewa tace "jikan Hajiya ce, sunanta Du'a, she will be ur mate Aneesa keda Mariya" tanuna Mariya da itama ta tsayar da peeling Irish din datake tana kallon Ammi, tafi Aneesa tayi da Mariya tace "yi sauri Mari mugama girki muje gidan Hajiya" murmushi Ammi tayi takalli Rahima data cigaba da aikinta tace "Anty Rahima kinyi shiru" wani irin murmushi tayi tace "Ammi bakina Ya Asad maganan wayoyin muba" dasauri sauran sukace eh Ammi, hararansu tayi tace "wai mesa kuke tsoron yayan ku haka, aiko babu wanda zai kara aikena wajenshi cikinku kuje kusameshi dakanku kokuma kuma Sharif magana yasaimuku" dasauri Mariya ashagwabe tace "Ammi wlh Ya Sharif mugune yace wai babu wanda zaici kudinshi cikinmu wai tara kudin aure yake, duk wanan wahalan inda Dad na nan muna gayamai zai sai mana wlh" shiru Ammi tayi tace "kugama girki kuje ku sami Asad to baruwana kudena sani a lamarin ku" nariga nahada muku komi ku karasa kuyi setting dinning up tai maganan tana fita daga dakin.

Wuraren 5 suka gama girkin tass sukai setting dinning dakinsu sukayi kowa yay wanka, Aneesa data gama shiryawa cikin wata yar rigan zaman gida half gown mai spaghetti hand ya tsaya mata a knee ta kallesu tace "kumuje wajen Ya Asad" kwalalo ido daga Mari har Rahima sukayi atare sukace "kidawo Ipy nidai bazani ba" hararan su tayi tace "wlh naje nawa kadai zan fadamai" tawuce fuuu tafice tana tafiya ahankali gabanta nafaduwa, tsayawa tayi takalli kanta a madubin dake bangon falonsu tayi kyau sosai ga kitson kanta yamata kyau abunku da faran yarinya dan gidan Asad ne kawai black cikin yaran, bude kofa tayi tai flat dinsu Asad, tsayawa tayi abakin kofan tai knocking, jin ba'a amsaba yasa ta danna door bell har sau biyu, sake knocking tayi cikin wata irin isasshiyar murya akace. "waye"? faduwa gabanta yayi muryanta har rawa yake tace "Ya Asad is me, Aneesa" shiru aka sakeyi takai kusan 3min atsaye awurin sanan akace "come in" dasauri tabude kofan ta shiga yana zaune a falo dagashi sai towel daya daura a waist dinshi ya zaunar akan kujera ya mikarda kafa yadaura kan enter table yadaura MacBook akan cinyanshi yana aiki ruwan coily gashinshi nabin fuskanshi.

Kallo daya tamai tasaukar da kanta kasa dasauri, tunda take bata taba ganinshi ba rigaba sai yau, wani irin hadiye miyau tayi gabanta na dukan uku uku, tashiga wasa da yatsunta takasa magana, batare daya kalleta ba hankalinshi nakan aikin dayake yi akan system yace "why are you here"? Yanda kirjinta ke dukan uku uku yasa muryanta yama fara rawa tace "Y.....a As...ad, dama....dama...." saita karayin shiru tadan dagokai ta kalleshi aikinshi yakeyi comfortably a MacBook dinshi kaman baimasan tana wajenba, kirjinshi tabida kallo jitayi jikinta yadau rawa da sauri ta maida kanta kasa tadage tace "Ya Asad I want a new phone Ammi tace zata gayama shine yanzu wai muje musameka da kanmu, ahhmm kuma da shopping da resuming school, I want new school bags, pairs of shoes sai Abaya dakuma and kuma pads dinmu yakare duka" saida takai nan tai shiru kirjinta na bugawa fat fat fat bata taba sanin zata iyama Asad magana ba saiyau, juyoda kanshi yayi yakalleta for the first time tunda tashigo dakin, ahankali kaman baison yay maganan yace "what happen to your phone" dagokanta tayi ta kalleshi yanda yake kallonta yasa takasa mai karya langabar da murya tayi tace "babu abinda yasame shi I just wanted a new one" still kallonta yake babu alamun wasa kowani yanayi akan fuskanshi yace "and the other things nawa zai isheki kisaya" wani irin murmushi tamai cikeda jin dadi tace "150k zai isheni Ya Asad" Su Rahima da tuntuni suke gaban dakin suna jiran suji yanda zata kaya jin yana tambayanta nawa yasa suka turo kofan suka shigo suna sallama, duk atare suka gaidashi muryansu narawa. "Ya Asad good evening" dasauri Aneesa tace "Ya Asad kaga saida nace musu fa suzo muje tare sukaki wai tsoro sukeji sai yanzu dasukaji zaka bani kuma wlh ni bazan raba kudina daku na nawa kadai nafadi" dasauri Rahima tadan kyafta mata ido takalli Asad din tace "Ya Asad sorry" Mari ma ahankali tace "Ya Asad sorry ni wlh tsoro ya hanani ma biyota" duk tsayawa yayi yana kallonsu yanda duk suke trembling, ahankali yasaki dan murmushi, wani kalan dadi ne yakashe su dasauri Rahima tace "Ya Asad nima I want new phone" dasauri Mariya tace "Ya Asad nima" ganin suna neman samai ciwon kai yasa yakalli Aneesa yace "go to my room, check the left sidebed drawer bring all the money that is there" wani irin dadi taji tace "tom Ya Asad" dasauri tawuce stairs tai sama dakinshi tabude ta shiga wani kamshi ne yamata sallama, drawer taje ta kwaso duka kudin wrappers na yan dubu dubu ne guda 10, kwaso su tayi tasauko, Su Rahima na ganinta suka shiga murmushi, gabanshi tazo zata bashi kudin gefenshi ya nuna mata hakan yasa ta ijiye kudaden awajen, hannu yasa

yadauki rapa biyu yabata dasauri takarba tawani washemai baki tama kasa godiya, "Rahima" "na'am Ya Asad" dasauri tazo dauka biyu yayi yabata dagudu Mari tazo itama yabata biyu dukansu yabasu 200k each, ahankali yace "u will get the phones tommorow" wani irin ihu sukayi sukahau tsalle awurin suna rungume juna. "Ya Asad thank u, yaaayyyy, Ya Asad u are the best wallahi" ihunsu yatada Sharif dake bacci hakan yasa yasauko ganin kudi a hannunshi suna rawa suna nunamai yasa cikeda wasa yace "yanzu sabida ku yan bakin ciki ne Asad na rabon kudi shine bazaku tasoni nazo na amshi nawaba " dasauri Rahima tace "bayan kahanamu damuka maka magana" hararanta yayi yaje gaban Asad dake aikinshi yana kallon ragowan 4 raps na kudin yace "Ya Asad nima abani nawa"? Dan hararanshi Asad yayi saikuma kaman bashiba yakalli su Aneesa yace "abashi" atare sukace "nooo Ya Asad" wani irin biyo su dagudu Sharif yayi aiko suka kwasa dagudu suka fita daga dakin yace "shegu yan bakin cikin yara kawai" murmushi Asad yayi sosai yace "kasai musu waya" juyowa yayi yaharari Asad yace " marasa kunyan yaran nanne zasuci kudina, ashe zasu mutu bawaya, Tara kudin aure nake" tabe baki Asad yayi yace "says wanda baida girlfriend" hararanshi Sharif yayi yace "Malam ya isheka fa kaita daga harkata tunda dai kahanani kudi".
wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE1️⃣8️⃣
Tashi Asad yayi ya rufe system din ya ijiye sanan ya kwashe ragowan kudinshi yawuce wanshi sama, baiwani dade ba yasauko cikin jallabiya sabida sallan magrib da aka kira sai baza kamshi yake bayin falo shima Sharif ya shiga ya dauro alwala sanan yafito suka fice tare zuwa masallaci.

Ana Magrib suka shigo gidan, dinning direct sukayi, zama sukayi Ammi na fitowa, Sharif yace "Ammi ina yaran nan wai nisukema dariya" dan hararanshi Ammi tayi tace "toba dole suyimaka ba nan nan yaran nan suka rokeka kudi kahanasu, anyway suntafi wajen Hajiya, kasan jikan Hajiya tazo shine ita sukaje gani nace musu nai musu kawa age mate dinsu ce wai zasu cemata ta shirya suje shopping tareda ita gobe" tsaki Sharif yayi yace "Ammi bani abinci na naci nima naje naga jikan Hajiyan muga ko za'ayi ta gida ne, Ammi tanada kyau"? Hararanshi Ammi tayi tace "inkaje ka gano da idanunka" tai maganan tana bashi plate na biryani rice, karba yayi yafara ci sanan ta zubama Asad dake daddanna wayanshi kaman bashi awurin. Biryani ta

zubamai sanan ta turamai gabanshi tace "ina kaje dazu Asad" dagokai yayi yakalleta spoon yadauka zai faracin abincin yace "naje nasha iska ne kawai Ammi" ture abincin Sharif yayi yamike yace "Ammi natafi" wanan karan dariya Ammi tayi tabishi da kallo fita yayi abinshi, tashi itama Ammi tayi tai sama bata wani dade ba tafito rikeda drawing book din Du'a  samin shi tayi zaune inda tabarshi yanacin abinci, kujeran kusada shi taja tazauna sanan ta ijiyemai drawing book din agabanshi, Ammi yabi da kallo saikuma ya ijiye spoon din dayakecin abinci dashi yadauki drawing book din yabude yana dubawa, ahankali yakalli Ammi yace "Ammi who drew this"? murmushi Ammi tayi tace "zanen yayi kyau" dasauri yana kallon drawing din yace "this is classic, I mean the hands behind this drawings is a genius, Ammi wow, idan yanzu nabada wayan nan zanen akai bringing this shoe to life my company zai zama number show brand company in the whole Africa" murmushi sosai Ammi tayi tace "zaka bama mai zanen aiki kenan"? sai alokacin ya kalli Ammi yace "who drew it Ammi" ahankali Ammi tace "zan gayamaka, but my zanen is very dear to me nai alkawari zaka bama mai zanen aiki dudda batai makaranta ba" dasauri yace "Ammi u mean mace ce tai zanen!" gyadamai kai tayi tace "yes mace ce, but batai school ba sabida some matsaloli irin na rayuwa, but she's talented, inason kabata aiki sanan kabiyata tsakani ga Allah yanda kake biyan illustrators dinka" yatsine fuska yayi yace "Ammi kinsan qualifications din illustrators dina kuwa, how can I pay wacce bada da credentials haka is not possible ma" fizge drawing book din Ammi tayi tace "then forget it" dasauri yace "okay naji Ammi kawo" ya karbi drawing book din yana kara dubawa, Ammi tace "yanzu yaushe zata fara aiki" ahankali yace "gobe Monday, for now Sharif will handle everything dan sai next week zan koma"

wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️M SHAKUR

Free page
EPISODE1️⃣9️⃣
Gyadamai kai Ammi tayi cikeda jin dadi tace "Allah maka albarka Asad dina" murmushi yayi yace "Ameen Ammi, but who is the girl"? kaman bazata fadamai ba tace "jikan Hajiya ce, she's 21" yatsine fuska yayi yace "Ammi ni all those children banson raini fa" hararanshi Ammi tayi tace "to Uncle Asad, ya za'ayi ma tamaka raini, jikan Hajiya ai she's just like ur sister su Mariya idan tayi badaidai ba ka gyaramata, kuma batada raini ko kadan that I know" yatsine fuska yayi irin baimasan maganan nan ahankali yace "Ammi I want coffee" tashi Ammi tayi tace "bari nahado ma tunda yaran nan duka sun gudu gidan Hajiya sun barni nikadai" kitchen tawuce tashiga....

Yau idan kaga bakin Du'a har kunne, har Rahima dake feeling tagirme su bazata iya zama friend din Du'a ba jitayi tanason Du'a sabida yarinyar akwai kyau dudda sun lura duk sun fita wayewa basu wani damuba kafin kice me cika falon Hajiya sukayi da hayaniya, suka tasa Hajiya agaba sai tabama Du'a itama kudin shopping gobe duk suka tafi tare, itama 200k tadauko tabata daman tanason takai yarinyar shopping but bata sami lokaci ba waya ma tace "gobe idan zata dawo zata taho mata da waya" duk suna cikin uban hanayinan Sharif yay sallama, dasauri Rahima tace "kinga Du'a we have two brothers, wicked and harsh, yanzu zakiga weekend one din shike mana murmushi da wasa amman shine ba'acin kwandalan shi" Hajiya dake kallonsu tace "Au haka kikace Sharif shigo kaji yanda kannenka kebata maka suna" turo kofan yayi yashigo hakan yasa Du'a itama tadaga kanta dantaga wanda ake batawa, wani kyakkyawan gayene dogo mai tsayi gashinan fari fat kaman su Rahima, tana ganinshi taga kamanninshi da Rahima da Mariya, baida kiba ko kadan, sai uban kyau ga sajenshi baki sidik dasuke nan akwance, gashin baida tarin gashi irin na Asad amman akwai gashi kadan da lowcut yakeyi ko kadan bata ganeshi ba hakan yasa kawai ta tsaya tana kallonshi daga inda take zaune kusada Hajiya dasu Rahima.

Dauke kai yayi daga kallon Du'a ganin kannenshi da kowa na wajen yace "Hajiya yanzu har gidanki suka tattaro sukazo suna gulmana yaran nan, aiko wlh zan baku kashi" yay maganan yana dunfaro su, ihu sukayi duk suka tashi suka kankame Hajiya Du'a ko sai dariya dasauri Hajiya tace "jama'a na shiga uku, wani yamikomin wayata yaga wlh Ammin ku zan kira tazo ta kwashi yaranta kutafi gida tunda neman kasheni kuke kai kuma wlh bazaka taba yaran nan agidan nan na ko kazo kazauna kokuma kawice katafi idan mugunta kazo yi nagayamaka kukuma ku dagani" Da sauri suka dagata shikuma yazo gefenta yazauna kusa da ita yay folding hannu yace "Hajiya jikanki batada kunya ita batasan yayanta yazo tagaidani ba wlh idan tace zata biyema marasa kunyan yaran nan nida ita bazamu shirya ba" yay maganan yana hararan Du'a, sosai Du'a ke murmushi ganin yanda Sharif keda ban dariya, ahankali cikin yar muryanta tace "Ya Sharif ina yini" hararanta yayi yace "lpy lau" Mariya dake gefenta tace "Ya Sharif kaga harda ita zamuje shopping din gobe tunda Ya Asad yabamu namu kai kabata nata ai itama kanwarka ne yanzu" dasauri Hajiya tace "ohh ni yasu Mari ke Mariya yaushe kika dawo scammer eh, Sharif yaran nan damfaran ka zasuyi ba yanzun nan nabama Du'a nata 200k dinba" dan sosakai Sharif yayi yace "Hajiya ni bansan ko yaran nan basuso nai aure bane, kudin aure fa nake tarawa" saikuma ya kalli Du'a yace "nasan sun riga sunce miki banda kirki I will prove them wrong, kinga ban shigo da kudi ba, but zanbama Mari gobe tabaki okay" gyadamai kai tayi tana kallonshi irin kaman bata yarda ba dinan dan ita Grandma tariga tabata kudin ta, kaman Hajiya ta lurada hakan ne yasa tace "baki cema Yayanki kingode ba" murmushi tayi ahankali tace "nagode Ya Sharif" nan fa dakin ya kachame da hira, shi Sharif baida girman kai yana shiga kannenshi yayi hira dasu sosai iyayensu dasuka rasu yasa yafara haka dan he is all dasuke dashi couple with the fact Asad baida wasa, saisa yake hira dasu yasasu dariya yasasu bakin ciki komi ba, daga karshema zamewa Du'a tayi tai bacci shoulder ta nakan jikin

Rahima, sai wuraren 11 Sharif ya tarkatasu sukama Hajiya sallama suka tafi kaman karsu tafi, itakuma ta tada Du'a tawuce taje ta kwanta.

Flat dinsu ya shiga yana maida kofa yarufe sanan yashigo ciki Asad yagani zaune afalo yana kallon wani horror movie a smart TV dake falonsu, tsaki Sharif yayi danya tsani horror movie zama yayi yace "kafara kallon film din aljannun nan naka ko" dagamai gira daya Asad yayi sanan yadauki drawing book din da Ammi tabashi ya jefama Sharif din, dasauri ya chapke yace "what is this" yay maganan yana budewa, ganin wasu hadaddun zanen takalma yasa yamike tsaye yacigaba da kallon su one by one. "woooooo Asad who drew this??? Wow Wow, waye yay zanen nan eh, we need this talent a company mu wlh, who drew this Asad" dan batarai yayi yace "Ammi takawomin wai I should hire wacce tai zanen a company mu" dasauri Sharif yace "of course Asad you should hire this talent karfi all those competing companies su gano mai zanen su rigaka hiring nashi, but waye mai zanen a ina Ammi tasamo maka" tabe baki yayi yace "tace wai jikan Ammi ce mai zanen, she's a small girl 21, kuma karatun ta a JSS2 ta tsaya due to some reasons best known to them, how can someone dabaida qualification zaimin aiki eh" dasauri Sharif yace "in this case don't look at qualification look at the talent, Asad ko bature illustrator dinka baitaba zana takalma masu kalan kyau dinan ba, this is masterpiece wlh, mukai takalman nan trust me all celebrities across the globe will be rocking ur brand, yarinyar nan tun wuri without second thought kadauketa" yatsine fuska yayi yace "Ammi tariga tasa nadauketa gobe zata fara aiki" dasauri Sharif yace "gobe" dan yasan gobe zasuje shopping, gyadamai kai Asad yayi yace "yes, inaso you should handle everything, interview her kasata a office na illustrator din let her get to work, guide her, before nagama this TV program in yaso once am back sai afara work on production" gyadamai kai Sharif yayi yace "okay Asad, bari naje na kwanta, kaine night owl" yay maganan yana stairs yana murmushi da gangan yaki fadamai wacece jikan Ammi yanaso yaga reaction dinshi ranan dazaiga wacce yace to daga rijiya ce jikan Hajiya ita yabama aiki.

Wuraren 5:30 Hajiya tashigo dakinta, tadata tayi ahankali tabude idanunta tashi tayi ahankali tazauna Hajiya dake kallonta tace "guess what" bude idanunta tayi tarr tana kallon Hajiya, murmushi Hajiya tayi tace "kinsami aikin" wani irin murmushi tayi tawashe fararen hakoranta, Hajiya tace "amma ance yau zaki fara aiki, danhaka tashi kiyi salla kiyi wanka ki shirya yarinya na is now a working class young lady, my lucky jika" murmushi sosai tayi ahankali cikin muryan baccinta tace "Grandma shopping dinmu dasu Rahima fa" murmushi tayi tashafa gefen fuskanta tace "don't worry about that karfe 4 zaki tashi daga office idan kindawo sai kuje, yanzu tashi kije kiyi salla" gyadamata kai tayi ta tashi dasauri tai bayi alwala tayi tafito tai salla saida tai karatun Al Qur'ani tai addu'a Allah ya sanyama aikinta albarka sannan takoma bayi tayo wanka tafito mata shafa ta shirya cikin riga da skirt na atampa sanan tafito falo, tunda take saukowa Hajiya ke kallonta ganin yanda mahaukacin shape dinta yafito akayan yasa taji bata natsu ba, ko aikin

ma data bari tayi sabida tasan Ammi da yaranta ne tasan yanda sukeda natsuwa kuma tasan zasu sa ido akan Du'a, saisa ta natsu da bata bartaba, sanan kuma tanason yarinyar takara girma tai wayau tasan ya rayuwa take outside home, kujeran dinning Hajiya taja mata hakan yasa ta zauna tace "grandma cikina namin wani iri idan natuna zani aiki" dan dariya Hajiya tayi tana zuba mata tea da Irish tace "kina feeling butterflies a ciki, it's normal, yanzu ci abinci karki latti fa, 8 ake zuwa aiki" dasauri tashiga cin bata wani ci sosai ba dan bata iyacin abinci sanan ta tashi, Hajiya tace "anya bazan sayo miki Vitamin B complex ba kuwa Du'a baki iyacin abinci, oya tashi muje sama kiga" tashi tayi sukai sama, dakinta suka shiga Hajiya tabude wardrobe dinta, wani sabon abaya taciro mata black mai mahaukacin kyau ta ijiye kan gado tace "inaso ki zama very wise girl, kinga kalan jikin da Allah yabaki dan haka bazaki dinga saka atampa haka kina zuwa aiki ba, zan karo miki hadaddun abaya masu kyau su zaki dinga sawa kina zuwa office okay, inaso idan kikaje ki natsu ba ruwanki da gulma ko surutun office respect ur senior idan kikai laifi aka miki fada take ur correction, karkiga sabida kinga Sharif ko Asad sabida kin sansu suna kaman matsayin yarana ne kidinga musu magana anyhow ko rashin kunya no, a office is strictly work and formal communication okay, ki natsu kafin ki zauna akan kujeran aikin ki da za'a baki kiyi addu'a, kullum idan kika shiga office dinki kafin kifara aiki kiyi addu'a hakan zaisa kidinga samin cigaba Allah na Buda miki, ki zama mace mai kamunkai, abinda yasa nama barki kiyi aiki sabida inaso ki sami experience ne kisan menene rayuwa dan bakisan komi kan rayuwa ba Du'a, be very smart okay, karki damu yau zan sau miki wata" gyadama Hajiya kai tayi tace "thank u Grandma" ajiye mata kayan tayi tace "oya shirya nima bari naje na shirya zan shiga office yau saina saukeki a company ku" wucewa tayi tafice, shiryawa tayi cikin doguwan rigan ita kanta saida ta kallo kanta saboda yanda tai wani kalan kyau, parking kalabanta tayi sanan tazauna kan kujeran tadau gyalen abayan tana kokarin rolling bata iyaba aka turo dakin aka shigo, Hajiya ce ta shirya cikin ubansun gown din lace rikeda waya tamikama Du'a tace "ga Mamin Ki" karba tayi takai kunnenta ahankali tace "ina kwana Mami" ajiyan zuciya taji Mamin ta tasauke tace "Du'a ya kike" murya chan kasa tace "lpy lau" murmushi Mami tayi tace "ance kinsami aiki Allah ya sanya alheri ki kulada kanki kinji" murya chan kasa tace "to" "OK bye" bye tace Mami ta katse wayan karban wayan Hajiya tayi tace "bani gyalen kiga namiki rolling" rolling Hajiya tamata tsaf, saita juya tana kallon gaban mirror hannu tasa tadauko wani pink janbaki da kwallin saka mata kwallin tayi sanan ta shafa mata Jan bakin kadan daya saje da lips dinta, kafin tadau turaruka ta fesa mata sanan tadauko wata jaka tace "idan mace zata fita most especially office haka makesure kinada pad kwata daya aciki incase of period yazo miki, sai wipes, sai lip balm, sai dan karamin turare haka dayar hoda ko madubi, pen da dankaramin jotter haka" tai maganan tana daukan komi tana samata ajakan sanan tabata jakan, karba tayi tana murmushi Hajiya tawuce tafita tace "sa takalmi ki sako" takalmi tasaka sanan tajuya takalli kanta a mirror wlh kaganta bazaka iya tantanceta da balarabiyaba tai wani irin kyau akayan, hakanan saitaga tama kanta girma tadawo wata babba kaman yar mai kudi jin Grandma ta kwalama ta kira yasa tajuya da gudu tafice.

don magana dani M Shakur chat me up by clicking on this link wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

Free page
EPISODE 2️⃣0️⃣
Razika da Shemau tagani a falo tsaye duk suna kallonta suna murmushi sabida tsabagen yanda tai kyau, sake washe musu baki tayi tace "natafi office" kwashe wa sa dariya sukayi sukace "adawo Ipy Du'a, Allah yabada sa'a" Ameen ta amsa sanan tawuce tafita waje tana musu bye, tsakar gida tayi tana tafiya ahankali ita kanta Hajiya tsayawa tayi tana kallon Du'a to some extend bata wani cika blaming Kaka ba data dage cewa Du'a ba jikan ta bane dan wlh Du'a bata da banbanci da balarabiya ga kyau ga diri ance mutum tara yake baicika goma ba Du'a tamafi ashirin, fararen kafafunta Hajiya tabi da kallo dake kara haske bakin abayan data saka karasowa wajen tayi tace "muje grandma" murmushi tamata ta rungumo kafadan ta tace "kinyi kyau jikalle, yau kukaje shopping ki zabo takalma masu kyau da hills ba chan chan ba kinji, good shoes takes a woman to good places, takalman Du'a dina should be epic kaman cendarella koba hakaba" "hakane Grandma" tai maganan tana shiga mad jeep din Grandma, Grandma ma tashiga driver ta yajasu, hira Hajiya keta mata ganin she's a bit nervous daurewa kawai take wayaga sabon shiga, cikin wani ubansu glass building taga sun shiga mai tsawo wanda daga gani kasan akwai elevator dan sabida yanayin tsayinshi sunan company EPIC & COs LTD, parking direban Grandma yayi takalleta ganin yanda take kalle kalle tace "this is company dazaki dinga aiki aciki wuce kitafi" kallon Hajiya tayi idanunta sukai zuru zuru kaman zatai kuka tace "Grandma mezance" dariyan da Grandmaa keji ta hadiye tace "just go this is beginning of new phase, anriga an baki aikin so amsan da zuwanki idan kikaje akwai receptionist awajen ki gayamata sunanki she will tell u what to do, come here" Hajiya tama goshinta peck tace "Allah bada sa'a don't forget abubuwan dana fadamiki" gyadamata kai tayi gabanta nafaduwa sanan tabude kofan ta fita, direban grandma yajata suka wuce suka tafi suka barta tsaye awajen, haduwan ginin kadai yasa taji she's having change of mind ita daketa murna zatai aiki ita ko kadan batai picturing something like this ba irin wanan big organization dinne Ammi zata saman mata aiki ba, takai kusan 5min tsaye awajen sanan ta dage tafara tafiya towards the entrance door da kofan yay kala da kofan bank, taga yanda mutanen dake wucewa ke shiga hakan yasa itama taje, security dake wajen ne dake bada hand sanitizer ne yabita da kallo sanan yace "ur hand Miss" muka hannunta tayi aka zuba mata ta shafa yace "u can go in" shiga kofan tayi nan kawai taga glass yarufe ta ihu tayi tashiga buga glass din. "wayyooo Allah na innailaihi Grandm......" bata karasa kiranta ba taga kofan ya budu ga mutane dayawa awajen kowa na harkan gabanshi bama a lurada ita ba yasa tashare hawayen daya zubomata da sauri tashiga tana kalle kalle still ganin desk da counter da aka rubuta reception yasa tai wajen, wata hadaddiyar chic ce awajen kafinma Du'a ta isa wajen yarinyar ke kallon

Du'a kaman zata hadiyeta tace "how can I help u Miss" ahankali Du'a tace "my name is Du'a Muhammad" dasauri receptionist din tace "the new illustrator, please come with me Miss Du'a" Receptionist din ta tashi tai hanyar elevator Du'a biyeda ita suka shiga, 4th floor ta danna da elevator yafara tafiya runtse ido tayi danji tayi hanjinta na neman fitowa, wani complete new section tagansu aciki saiga wata secretary dake zaune gaban system ga kujeru zaman mutane awajen, nunama Du'a kujera tayi tace "have a sir Miss Du'a" sanan takalli secretary dake kallon Du'a tace "she's the new illustrator, u take it from here" gyadamata kai tayi tawuce itakuma Du'a ta zauna tana kallon office din dake gabanta dakenan arufe jikin kofan anrubuta M.D Mr Sharif Alameen Kitse, takai kusan 1hr azaune awajen sanan aka bude kofan wasu manyan baki dake sanye da suit turawa suka fito tareda Sharif dake sanye da suit yayi wani irin kyau, binta yayi da kallo sai baice komiba yawuce yataka bakin har zuwa wajen elevator sanan suka shiga yadawo ya tsaya gaban secretary din cikeda fushi yace "tun yaushe Miss Du'a ke zaune anan Miss Amal"? dasauri matan tace "about an hour ago" "and u couldn't take her to her office" yafadi ranshi abace, tashi Miss Amal tayi tace "sorry sir I thought zaka fara ganinta ne tukunna saisa na bartaka sallami baki tukunna" cikeda takai takaici yawuce gaban Du'a yace "I apologize for that Miss Du'a, shall we" tashi tayi tana gyadamai kai yabude office dinshi yashiga tana biyeda shi sai kallon office din take yanda office din yahadu kujera yanuna mata ta zauna sanan shima yawuce ya zauna yakalleta da murmushi a fuskanshi yace "you want coffee kona kaiki cafeteria kici abinci"? Gizgizamai kai tayi ahankali cikin muryan nan nata mai bala'in dadi tace "I had breakfast thank you" cikeda gamsuwa yana kallonta yace "it's fine, anyway welcome to EPIC & COs LTD, company ne that is into creating and inventing all kind of shoes dakika sani da different materials, starting from animal skins har zuwa leather shoes, munada lots of investors da abubuwa da yawa which I believe since kina nan yanzu u will understand everything, Today is all about introduction babu abinda zakiyi gobe ne zaki fara aiki officially, that aside. My name is Sharif Al Ameen Kitse, nine MD wato managing director of this company, sorry bazaki sami daman ganin CEO dinmu ba dan he's officially on leave sai next week zai dawo, I will give u a tour around the company har zuwa warehouse dinmu dake kasa inda ake hada takalman da ire irenki ke zana mana, zan kaiki HR department zaki miki small abu za'a dauki hotonshi da some biometric dan za'a miki ID card na aiki, we have mosque we have church, rest room cafeteria duk acikin nan, and if u are having any difficulty with anything feel free to give me a call okay I'm ur brother banda haka Hajiya tace nakulan mata da jikan ta inba hakaba saitaci kaniyana" yay maganan cikeda wasa yana kallonta dan murmushi tayi itama dan sosai yanada kirki, ahankali yace "are you ready for ur tour ko kina bukatan wani abu, water juice ko cingum ko sweet kinsan mata da kwadayi remember I have sister nasanku, nabaki sweet"? yay maganan yana jawo wata yar locker shi yanuna mata, uban sweet ne na chocolate da sauransu aciki yana kallonta, kasa cemishi a'a tayi ahankali yasa ahankali tace "eh" ciko chocolate da sweet yayi a hannunshi yamika mata hannu tasa takarba ahankali tace "thank you" jakanta tabude ta zuba sanan tadauki daya tabude tasa abaki, murmushi yamata yace "let's go" gyadamai kai tayi tabishi suka fito tana biyedashi suka shiga elevator, ya danna 5th floor yace "let's start with 5th floor nanne floor na Oganmu duka, CEO anan kuma office din illustrator company yake dan haka anan office dinki yake" jin shiru yasa yajuyo yakalleta gani yayi ta kankame idanunta lips dinta na motsi, dan murmushi yayi yace "scared of elevator"? Gyadamai kai tayi ahankali daidai kofan nabudewa yafice ahankali tafito itama idanunta har sunyi ja sabida tsoro, tazaci 4th floor

nada kyau dasukazo fifth floor dinnan saitaga wane 4th, ga mutane sai aikinsu suke sai gaida Sharif ake ana bin Du'a da kallo dashi kanshi Sharif saida ya lura, gaban wani office yaje dake kusada CEO dan tazaran ba yawa taga an rubuta illustration, bude kofan yay ya shiga yajuyo ya kalleta yace "come in" shigowa tayi tana bin office din dakallo table ne hadadden gaske da laptop ke kai ga kujera dake juyawa, ga dogon couch, sai frames a bango na zanen takalma masu kyau, sa shelf dawasu irin hadadden drawing book dabata taba ganinsu arayuwanta ba suke ganin su take kallo yasa, Sharif yadauko daya yace "anan zaki dinga zanen it's digital drawing book, kome kike zanawa is connection to this MacBook" yanuna mata laptop din dake kan kujeranta, yace "we can't wait for xanenki, you can keep ur bag dan nanne official office dinki" gyadamai kai tayi ahankali ta ijiye jakanta kan table sanan yakalleta yace "mucigaba kokin gaji" murmushi tamai ahankali tace "mucigaba" fita yayi tabishi wanan karan saitaga baibida ita elevator ba sun dauki stairs hakan bakaramin dadi yamata ba harsaida ya lura dansai murmushi takemai, suka tafi kowani floor yana nuna mata komi, sukaje Cafeteria company babban gaske all employees dinsu are entitle to lunch kaje za'a baka free lunch, dasafe kuma kowa is entitle to either coffee ko lip tea saisa kowa nan yake fara tsayawa dasafe ya karbi tea sanan kowa yawuce office, yakaita mosque incase tanaso tazo tai salla, yakaita warehouse, yakaita HR yana tsaye akai taking biometrics dinta aka mata passports saida tagama komi sanan suka taho abin har mamaki yadinga basu wanan tour din dayake bata ba aikinshi bane, sake komar da ita Cafeteria yayi yakalleta yace "tea or coffee"? murmushi tayi kaman mai tsoro tace "tea" sawa yayi aka hada tea a coffee aka kawo musu a disposable cup mai marfi yabata nata yana rikeda nah I yace "muje" sakebin bene yayi da ita suka tafi har 5th floor, office dinta yakaita yace "now sit round relax do anything dakikeso, if u want anything just dial my number awanan landline Din" yanuna mata telephone din wajen yace "dial 444 zaiyi connecting naki to me" gyadamai kai tayi, waving mata hannu yayi yace "bye" ahankali tace "bye" harya wuce saikuma yaleko yace "drink our tea kiji da dadi kafin yahuce" gyadamai kai tasake yi tana murmushi, wucewa yayi yatafi abinshi, zama tayi kan kujeran ta da tuntuni yake shigan mata idanu tahau wasa akai tana juye juye saikuma tamika hannu tadauki cup din tashiga shan tea aiko dadi hakan yasa tacigaba dasha tana murmushi ita kadai.

wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

free page
EPISODE 2️⃣1️⃣

Sosai takebin office din da kallo kaman wacce bata taba ganin office ba arayuwanta, ga katoton TV dake makale a bangon office din, gawani camera Ata sama amakalle shima dabata san koname ba, ahaka tana zaune ita kadai har lokacin azahar tayi, knocking office dinta akayi saikuma aka budo kofan, Sharif ne murmushi lullube kan fuskanshi yana kallonta batare daya shigo cikin office dinba, dan murmushi tasakinmai itama dan wani irin kunyanshi takeji ganin yanada kirki sosai, ahankali yace "is time for zuhur u wanna join me?" Gyadamai kai tayi da sauri dan tuntuni takejin fitsari dama amman kunyan tafita ita kadai takeji taje, tashi tayi ahankali tafito duk yana kallon ta sanan taja kofan office din suka wuce tare har mosque yanuna mata side din mata ta tafi, wucewa tayi bayinsu sai kallonta matan dake wajen suke itadai babu wanda take cema uppan besides ma kanta akasa dan kunyan yanda suke kallonta takeji, fitsari tayi tayo alwala sanan tashigo masallacin ganin cupboard dake cike da hijabai yasa tadauki hijabi tasaka tai salla abinta, tana idarwa ta zauna tana kokarin rolling gyalenta babu yanda batayiba takasa hakan yasa takama gyalen ta wajen wuyanta gamgam tamike tafito, jigine da bango masallacin taga Sharif yay folding hannunshi akirji da alamu ita yake jira, ganinta yasa ya yunkura yataho inda take yana kallonta yace "maiya sami gyalen"? Ahankali tace "ban iya yanda Grandma tamini ba" Dan murmushi yayi yace "then u have to learn dagayau, let's go have lunch" yay maganan yana hawa stairs yay hanyar canteen dinsu tana biyeda shi, shiga sukayi ga few employees dinsu dake wajen suna cin abinci cikeda girmamawa suka shiga gaidashi amsasu yayi batare daya kallesu ba sanan yaja kujera yanuna mata alamun ta zauna zama tayi ahankali tana kallonshi ganin yanda yake wani kulada ita kaman yar kanwarshi, shima zama yayi yakalli yarinyar datazo cikeda girmamawa tace "mezan kawo muku sir" batare daya kalleta ba yace "I want pasta da salad, mezakici Du'a" yay maganan ahankali yana kallonta, kallon yarinyar tayi sanan tace "jallof rice" juyawa yarinyar tayi ta tafi itakuma tasauke kanta kasa tana wasa da yatsunta Sharif sai kallonta yake kaman yamata magana saikuma yay shiru shima ahaka har aka kawo musu abincin, cin abincin shi yafara hakan yasa yace "bazaki ci ba" Dan dagokai tayi ta kalleshi ahankali tadau spoon tafara cin abincin, bini bini yake satan kallonta, ta bala'in yima kyau, komi nata daban ne, harya gamacin abincin shi batai rabin nata ba hakan yasa yacigaba da jiranta, kadan takara akai ta ture hakan yasa yace "u okay" gyadamai kai tayi tasha ruwa sanan ta tashi alamun su tafi tafiya sukayi har office yasake rakata sanan yawuce nashi office din, wuraren 4 tana zaune a office dinta telephone din wajen yahau kara dasauri ta dauka, muryan wani security taji.

"Miss Du'a your driver is here to pick u up" dawani irin sauri ta tashi tana hada yan tarkacenta ajaka ta kosa ta ganta agida sanan tafito tana tafiya ahankali tasauka kasa zatai hanyar kofa taji magana a bayanta. "so you're living without saying goodbye" dawani irin sauri tajuyo ganin Sharif ne yana rikeda waya a kunnenshi da alamun ma waya yake but still saida yamata magana yasa adan kunyace tamai waving hannunta tace "bye" gyadamata kai yayi yacigaba da magana. "yes I can hear u Asad" waje tafita ta shiga motan Grandma dinta driver yatafi da ita, Allah Allah take takai gida, suna kaiwa gida tafito daga motan dasauri harda dan gudun ta tai falonsu tana budewa taga su Rahima Mariya da Aneesa duk sunci gayu sosai suna zaune afalon Hajiya atare sukace. "surprise" suka tashi suna rungumeta, wani irin murmushi tayi ta

kallesu tace "yaushe kukazo sorry" dasauri Aneesa tace "bakomi Hajiya da Ammi daman sun gayamana kinji aiki, jekiyi wanka kizo kici abinci mutafi" gyadama musu kai tayi takalli Grandma dinta dake zaune tana kallonsu tana murmushi, wajenta taje ahankali tace "Grandma ina yini" fuskanta tashafa tace "Du'a dina sannu da zuwa, yi sauri kije ki shirya kunga tuntuni su Aneesa ke jiranki" wucewa sama tayi da saurinta dakinta ta shiga, wanka tayo tafito, tunawa da abinda Grandma tafadi mata yasa tasake dauko wata gown wanan is simple dan ba designers bane irin na dazu data sakaba milk color, saka shi tayi sanan tadauki mayafinshi ta feffesa turare tafito kasa, duk juyowa sukayi suna kallonta Aneesa tace "mena rike dankwali a hannu kiyafa mana" karasowa falon tayi tace "ban iya bane grandma zatamin" tabama grandma dan kwalin, dasauri Mari tace "Hajiya bari mu mata sabida ta iya" tana maganan ta karbi veil din daga hannun Hajiya sanan ta wani irin yafama Du'a akai gaban kanta daya cika da kwantaccen gashi yawani fito, Rahima tace "wow wlh kinyi kyau Du'a mutafi to, Aneesa ina kudinta da Ya Sharif yace mubata" dasauri Aneesa tashiga bude handbag dinta wani kudi taciro a envelope sanan tamikama Du'a din tace "ga kudinki, tundazu dasafe kafin yatafi office yabamu mubaki" dasauri Du'a takalli Hajiya danharga Allah batasan mezatayi ba, murmushi Hajiya tayi tace "karba Allah ne ya ciyar dake kafin aci kudin Sharif saidai idan Allah ya tsaga da rabonki ne" kwashewa da dariya yaran dukansu sukayi sukace "wlh kuwa Hajiya Ya Sharif kare bayacin kashinshi, karba muje" Ahankali tasa hannu takarba tace "thank u" sanan tasa ajaka, sallama sukama Hajiya sukai tafi direba ya kwashe su, sosai sukema Du'a hira a mota ita abin mamaki yake bata yanda suke sonta daga ganinta jiya dan har labarin samarin su suke bata, Aneesa data zauna agaban mota ne tajuyo ta leko takalli Du'a tace "ke baki bamu labarin saurayinki ba" Dan zaro idanu tayi tanuna kanta tace "ni"? dasauri Mariya dake gefenta tadan bugi kafadanta tace "common on don't be shy, tell us about the lucky guy" dan murmushi tayi saikuma tadauke kai dan tambayan tabata kunya ahankali tace "ni banda saurayi ko daya wlh" wani irin bude baki sukayi suna kallonta sabida mamaki, Rahima dake gefen Mariya tace "Du'a wasa kike ko" girgixa kai tayi tace "wlh ba wasa nake ba" shiru duk sukayi yanda yarinyar nan keda kyau ace bata da saurayi basu wani karyata ta sosai ba sabida sunga ko wayama batada shi, share maganan sukayi suka shiga wata hiran har sukakai mango dazasu, nan Du'a taga yanda ake shopping ita bama tasan mezata dauka ba hakan yasa kome suka dauka itama saisun daukan mata anata cart din, tundaga kan Bra da tuni suka gwadata suka shiga zakulo mata sizes dinta zuwa pants, pads kayan makeup, duk suna tura cart dinsu kowa na diban abinda akeso TV super market din dake makale asama na aiki Channels television news inda ake program REINVENTING THE NIGERIAN YOUTH....

Suna tsaye bangaren English wears Rahima ta amshi tape tana kokarin ana waist din Du'a dan asan size din jeans dinta itama ta dauka kaman daga sama wani kyakkyawan eloquent voice yadaki dodon kunnuwan Du'a da hakanan taji kaman tasan muryan, dawani irin sauri tadaga kanta sama takalli TV, chak ta tsaya ko motsi kirki tasaka, idanunta ne suka sauka kan fuskan da kusan kullum saitaga fuskan, wanda yacetota daga rijiya, yana sanye cikin wasu classic suit dark blue, ga necktie awuyanshi, yana zaune kan wata hadaddiyar kujera yayi crossing legs dinshi in a stylish way, yadaura hannunshi biyu kan cinyanshi wrist dinshi na daure da agogon

Rolex, idanunshi fari kalll wanan karan babu bakin glasses akan su, lips dinshi sunyi wani masifaffen pink kaman ya shafa janbaki pin akai, gashin kanshi dake da yawa sunyi wani kalan extraordinary coils, yana magana da english da accent dinshi na bristish, kaman acikin mafarki taji ana Du'a, Du'a, Du'a, tabatan da akayi yasa tai firgigit tafarka ta kallesu da sauri dan sai alokacin ma tasan ashe tayi nizan tunani ne, neck dinta Rahima takai hannunta ta taba tace "baki da lafiya ne? Tunanin me kike haka kin tsare TV da ido eh harmun gama siyan kaya" binsu tayida kallo ganin yanda suke kallonta kaman sun damu yasa takakalo murmushi tace "tunanin abubuwan dazan saya fa nake" murmushi dukansu suka mata, Rahima tace "mungama da wanan shop din next stop is abaya store, mutafi mubiya mufice yamma nayi" gyadamusu kai tayi tabisu zuwa wajen cashier tana kara waigowa tana satan kallon TV da Asad har lokacin ke magana, kowa kudinshi yabiya sanan aka musu parking kayan a leda sanan suka wuce suka fita still saida takara waigowa takalli TV, sanan suka fice, ranan basu suka dawo gida ba sai 8 nadare kasa bude kayan tayi salla ta lallaba tayi sai bacci tashinta grandma tayi saida ta tasa ta agaba taci abinci sanan tabarta takara komawa bacci da tagaji bata saba fita ko wahala hakaba, all abinda tasani is wanka kwanciya da cin abinci shikenan saisa tai bacci awahale.

DAN MAGANA DANI M SHAKUR CHAT ME UP BY CLICKING ON THIS LINK
wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE 2️⃣2️⃣
Kaman an tsikareta wuraren 4 na asuba tafarka da kanta batare da an tadataba, TV dake bangon dakinta ta tsaya chak tana kallo kaman mai tunanin wani abu, dasauri ta yaye bargon data lulluba dashi tasauka daga kan gadon, kunna switch din bangon tayi nan TV da decoder na DSTV duk suka kunna komawa tayi tazauna kan gadon tana sosa idanunta dake cikeda bacci, tadauki remote tashiga neman channels television news, da kyar ta iya ganoshi ta saka da sauri tana gyara zama kaman akwai abinda take shiri ta kalla, ganin ba abinda take nema sukeyi ba yasa tashiga wasu channels din tana skipping amman duka bataci karo da abinda take nema ba yarda remote din tayi akan gado sanan ta tashi tashiga bayi tai duk abinda zatayi sanan tafito dadduma ta shimfida tai nafila sanan tadauki Al Qur'ani tashiga karantawa har aka tada salla hakan yasa tarufe tai salla tana idar wa tai azkar ta tashi sanan tawuce tafito ko kadan batajin dadi, gaban dakin Hajiya tayi knocking tayi sanan tabude kofan ta shiga kan dadduma taga Hajiya zaune tana lazimi, ahankali tace "ina kwana Grandma" murmushi tamata tace "Du'a jiya angaji anyi bacci dawuri, tashi ga wayanki chan na samiki a chaji ina ganinma

yacika" dasauri takalli inda ake nuna mata hadadden waya ne a bango dawani irin sauri tafada Jikin Hajiya batasan meyafaru ba kawai saita saki kuka sosai tunda tazo gidan nan she has been so happy, babu mai takura mata ko matsa mata ko kyaranta, ba'a taba bata matarai ba, ba'a hanata zuwa ko'ina, she's truly happy, jin yanda take kuka yasa grandma ta kankameta itama ahankali tace "I promise you Du'a inhar inada rai adoron kasan nan u will never be sad again, wlh wanan karan ko uban waye kulleshi zanyi akanki, abinda kika going through agidan mahaifinki u will never go through that again kinji, kina tare dani anan har aurenki, I will take care of you, malamin islamiyya da boko ma na saman miki zai dinga zuwa Saturday da Sunday, u will excel kinji, forget komi dayasameki abaya kaddara ce, kyaune Allah yabaki amman hakan bazaisa ki karake rayuwanki a kulle adaki ba dan haka u will learn how to live with ur beauty kinji Du'a dina" gyadamata kai tayi ajikinta ahankali, dagota Grandma tayi takai hannunta kan fuskanta tana share mata hawaye tace "ba'a kuka agidan Hajiya, now tashi kidauki wayanki kije falo ki kwaso kayan shopping dinki ki jera komi a inda yakamata adakinki, idan aikin yamiki yawa ki kira su Razika su tayaki" gyadamata kai tayi ta tashi daga kan jikinta wayan tawuce tadauka tana kallo, iPhone mai kyau 11 pro max Grandma dinta tasai mata ga Sim din MTN aciki, fita tayi daga dakin taje falo ta kwaso kayayyakinta tadawo dakinta, ta shiga jera kayayyakin, harda bags da shoes hadaddu, masu tudu da flat, ga kayan kwalliya, saida tagama tsaf sanan tashiga bayi tayo wanka tafito, shiryawa tayi cikin hadadden abaya again kaman yanda Hajiya tafadi mai ruwan kasa, tai rolling gyalen da kanta dan jiya sauka su Rahima suka koyanata a shagon abaya sunma sai mata pins na kama gyalen tasa pin din, sanan tadauki wayanta tasa a jaka tasaka wani takalmi baki mai dan tudu kadan dayama farin kafanta kyau sosai sanan tafito, a falo taga Hajiya zaune tana shan ruwan bunu kusada ita tazauna tace "grandma bazaki je office yauba" murmushi tamata tace "nariga nai retire, idan kinga naje office ko akwai wani important meeting ne, kokuma naje supervision, tashi kiyi break direba na jiranki zai dinga kaiki yana zuwa ya daukoki kullum, banda latti koni bana tolerating late coming dan tahaka ake discipline na employees, go and eat" tashi tayi tawuce yau tayi breakfast kadan saita shiga kitchen wani karamin roba tadauko mai marfi ta zuba pepper meat aciki duk Hajiya na kallonta sanan ta taho tasa ajaka tana murmushi ganin Hajiya na kallonta, dan hararanta tayi tace "da yanda kikecin nama haka kikecin abinci danaji dadi kura kawai" dariya tayi tarataya jakan a shoulder tace "Grandma Byeeee" Bye Du'a ayi addu'a, gyadamata kai tayi tafice Hajiya na kallonta tundaga kan kafafunta kafanta badai kyau ba ya ilahi, tana ganin zatamai fara sakata sa Safa, mota ta shiga direba yajata zuwa office.

Yau tana shiga batai kauyencin datayi jiya awajen kofa ba, glass din na budewa ta shiga ciki, mutane sai kallonta suke maza da mata, saukar da kanta kasa tayi tana tafiya ahankali kafafunta na neman hardewa sabida yanda ake kallonta, dukfa sun tsayar da aikin dasuke kallonta ake, this is the first time data shiga waje kowa ya tsayarda abinda yakeyi yana kallonta, wani irin rawa jikinta yafara kafanta na hardewa daidai tazo stairs tahau kafanta yaturgude baya tayi zata fadi, jitayi antareta ta baya an daura hannaye biyu akan kafadunta murya chan kasa taji ance. "careful" dawani irin sauri tajuyo ta kalleshi, Sharif ne yana sanye cikin suit black yay wani irin kyau, hannayenshi dakekan shoulder dinta ya kalla sanan yajanye su ahankali murya

chan kasa yace "sorry about that" sanan yajuya daga inda yake yakalli ma'aikatan su da ganinshi yasa kowa yafara aikin gabanshi kaman da gaske dan kwafa yayi sanan yajuya yakalleta yace "let's go kinada aiki yau" yay maganan yana gaba ahankali tabiyoshi abaya, Cafeteria dinsu yaje yakarbi cup biyu yajuyo na tea yabata sanan yarike na coffee sukai stairs yana tafiya yace "omg, at this points knees dina sun kusan cirewa kuma duk kece Du'a, mezan fadama future wife dina idan suka cire" dan murmushi kadan tayi tana binshi abaya batare datace komiba hakan yasa yajuyo yakalleta, boye murmushin tayi dan zaro idanu yayi cikeda wasa yace "did u just smile knees dina na aching" ahankali tace "sorry" juyawa yayi yacigaba da tafiya yace "zan gayama future wife dina it's one gurl called Du'a tasani nake bin stairs zuwa 5th floor fa sabida tana tsoron elevator" murmushi tasakeyi batace komiba har sukakai office dinta, shiga sukayi ta ijiye komi kan table ta tsaya agefe, juyowa yayi ya kalleta yace "me kikeyi abayana sit akan kujeran ki nabaki aikin ki natafi" gyadamai kai tayi tazo ta gabanshi tawuce tazauna kan kujeranta ahankali kaman mai tsoro, wani karamin mini pad yamika mata yace "the CEO sent this, yanaso kiyi zanensu next week idan yashigo aikinsu za'a fara, 5 design na hills, 5 na loafers, 5 different design na croc and unhooked sandals" ganin yanda take kallon pad din yasa yace "it's a whole lot of work ko, don't worry take ur time zaki iya kadan yau kiyi sauran gobe" gyadamai kai tayi ahankali hakan yasa yajuya yace "in that case bari natafi" haryakai kofa ta dago kanta ahankali tace "ummmm" juyowa yayida sauri yakalleta yace "da wani abu ne"? gizgiza mai kai tayi tace "thank you, su Rahima gave me the money, Allah amfana Ya Sharif" tunda take maganan harta gama yake kallonta, dauke kai yayi yace "you are welcome" sanan yawuce yafita daga office din.

Ranan haka tawuce zane take a E-board dinan, bakaramin burgeshi zanenta Sharif sukayi ba, kafin 4 tagama gabaki daya ma dan she's so fast da zanen tawuce ta tafi direba yadauketa.

Tana shiga gida tafito tawuce ciki, Razika da Shemau tagani zaune a falo suna kallo TV tabi da kallo ganin film suke kallo yasa tace "ina Grandma" Razika dake kallonta tace "tana sama kaman ta kwanta bata dade da shigowa ba" sama tayi ahankali tabude kofan dakin Hajiya ganinta kan gado tana bacci yasa tawuce dakinta, kaya tacire tawuce bathroom wanka tayo tafito daure da towel tayi gaban wardrobe wani simple short gown tadauka tasaka, jin anyi knocking kofar ta yasa tace "shigo" shigowa Razika tayi dauke da tray na abinci tace "abinci nahado miki nasan kin gaji" wani irin murmushi tayi Razika nada kirki karban tray tayi tace "nagode Razika" gyadamata kai tayi tawuce tafita zama tayi kan gadon ahankali rikeda tray din tana kallon sinasir dake cikin plate, ga lafiyayyen miyan taushe dayaji naman kan Rago, dago kanta tayi sai kawai tacire tray kan jikinta ta ijiye agefe tamike tsaye da sauri switch din TV ta kunna tadau remote takoma kan gado ta zauna, gama booting yayi hakan yasa ta kunna tashar Channels Television News, daidai an nuno wani  daga cikin audience ya daga hannu, hoster tace "go ahead" mikewa tsaye yace "My name is Samuel Madina Chris, My question to Mr Asad Abdullahi Kitse is you see we all know you come from a wealthy home/family, so setting up a business starting a company can not be a problem for you cus ur family are buoyant enough to

support you with startup capital, mu yanzu that come from not so financially strong family how can we source for start up capital dan bamu da yan uwan dazasu taimaka mana"?
Nuno Asad akayi, yau yanacikin wani hadadden suit ash color dark ash da yamai bala'in kyau, yay crossing leg as usual, looking so elegant and classic, gashin kanshi sun kanannade suna wani irin kyalli, lips dinshi sunyi pink yirrrr....... Ahankali Du'a tawani irin sauke ijiyan zuciya idanunta kur akan TV akanshi gabanta nafaduwa dum dum dum.......

Gyara zamanshi yayi yay adjusting mic din dake gabanshi wani dan karamin cute smile yasaki dako hakoranshi basu bayyana ba cikin husky melodious voice dinshi yace "I appreciate this question Mr Samuel you know why" yadanyi shiru kafin yadan ciki lebe kadan yace "sabida mutane dayawa nada wanan misconception din, suna tunanin all mutanen dasuke business are from wealthy homes, lemme tell you all something, mahaifina nada companies, yanada kudi, but kunsan 1naira na mahaifina kona family na banyi amfani dashi a business dina ba, I strive for my business with my hard earn money" wani irin tafi hall din yadauka hakan yasa yay shiru yana jiran sugama yace "akwai lots of organizations that ayanzu the youth can reach out to dan su sami kudi and establish business dinsu ko expanding business dinsu, CBN, SMEDAN, BOI, and so much more, listen business is not for the lazy ones dayay depending on his families, and is not for the ones that doesn't have the zeal to strive hard and hard and hard to achieve his goals, business is for people that doesn't believe in impossible, don't tell ur self is impossible to establish a business because my parents are poor I don't have any source of income..." wani irin tafi aka fara a hall din kowa na having goosebumps sabida yanda yake maganan yana penetrating a zukatan audience din, saida sukai dan shiru sanan yace "business na mutane ne that believe in their self, people that have vision and are ambitious, people that are vasitile and strong hearted, we'll ladies and gentlemen I think we've reached the end of today's program saikuma gobe, thank you" wani irin tafi aka fara a hall din kowa yamike tsaye anamai tafi shikuma yawuce yana tafiyan nan kaman zaki looking damn elegant, classic and sexy yawuce yafita daga hall din, tashi itama Du'a tayi ahankali tama rasa mezatayi kawai saita koma ta kwanta kan gadon ahankali tana kallon TV da har anfara another program.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️M SHAKUR

Free page
EPISODE2️⃣3️⃣
Lumshe ido kawai tayi looking so somehow da bazaka tabace ga asalin yanayin datake ciki ba, ahaka bacci yay awon gaba da ita saida Hajiya tashigo ne ta tadata taje tai salla sanan ta sata agaba aka kawo mata wani abincin aka tafi danada dan bataci ba sanan tabarta ta kwanta dan akwai baccin sosai a idanunta.

******

Ahaka tai good five days a company from Monday to Friday Sharif has always been there for her, yanada kirki mara misultuwa, he's very nice and generous kaman ba boss dinta ba at all, yamaida ta kaman wata sister dinshi hakan yasa itama tadaukeshi kaman wanta Ya Hamad, itadasu Rahima kuma kaman sunsan juna tuni suka koya mata watsapp suka sakata group dinsu na yammata inda ake hiran samari da heart break ita saidai ta karanta taita mamaki, kullum 4 nayi take fitowa driver Hajiya ya dauketa tana dawowa gida zata gudu dakinta tasaka channels television news but kodaa yaushe ending din program din Asad take samu wani zubinma bata samin takalla kafin takai gida an gama barin ma ranakun da holdup yakamasu, har kasan ranta she wish zata iya ganinshi tace mai thank u for saving life dinta dan ko kadan takasa manta da fuskanshi da idanunshi dasune tagani da kyau danhar kasan zuciyanta takasa mantasu.

Yau Saturday su Rahima sunso sujata yawo Grandma tahanasu dan malamin ta zaizo, wuraren 10 malamin bayerabe yazo, Hijab tasaka har kasa tafito karatu yamata both na boko da islamiyya dan irin genius ustazan malaman nanne, karfe one suka gama yatafi, dakinta takoma ta kwanta yau kawai she's so happy koba komi tana gida zata kalli program dinan daga farko har karshe yau, salla ta tashi tayi jin ankira sanan takoma ta kwanta sai bacci, wuraren 3 Hajiya tashigo dakin tadata tayi. "ke Du'a oya tashi" bude ido tayi ahankali ganin Hajiya yasa ashagwabe ta daura kanta kan cinyarta murya chan kasa tace "Grandmaaa nagaji" smooth kumatunta Hajiya tashafa tai murmushi tace "oya tashi sonake ki shiga kitchen tareda su Razika kema kisoma iya girki, tuwon shinkafa zakuyi da miyan taushe sai farfesun kifi" ahankali tabude idanunta dahar sunyi dan ja sabida baccin datayi takalleta, tashi tayi zaune sanan tamike tsaye tace "grandma dakaina zanyi girkin ni kawai su nunamin yanda zan dinga yi" gyadamata kai Hajiya tayi tana murmushi tace "to gimbiya Du'a hakan za'ayi" wani kalan murmushi tayi cikeda murna tawuce tafita daga dakin dan tafi kowa so ta iya girki dan girki na burgeta, shiga kitchen sukayi aiko su Razika sun sha dariya dan targen tuwo bata iyaba haka suka dinga koyanata suna dariya gabaki daya ta manta da abinda takeso tayi, saida suka gama tuwon sanan ta kalli agogo dake manne abandon kitchen din, dawani irin gudu tafita daga dakin ta sama dakinta tashiga, TV kawai ta kunna dan decoder a kunne yake dama tana kan channels din, ganin angama program din yasa taji wani abu yatokare mata wuya, wata matace ta bayyana agaban TV tace "to jama'a ni karan kaina bakin cikin sanar daku nake cewa a yau ne wanan program din da gwamnatin Nigeria takawo muku sabida tallafawa Matasan kasa wanda wanan shahararen matashin nan dan kasuwan nan wato business Mr Asad Abdullahi Kitse ya gabatar muku yazo karshe, ku saurara kuji" matan tayi murmushi tace "channels television news tasami sakonni da dama kan shafukansu na sada zumunta da emails kan Mr Asad cewa mutane naso sugana dashi, toga wata sanarwa, gwamnatin Nigeria tashirya kyakkyawan liyafa wato dinner nagama wanan program din agobe karfe 4 na rana inda star dinku Mr Asad zai hallata, ana gayyatan marasa su fito duk kuzo dan Mr Asad zai sake bayarda jawabi wato speech awajen

dazai taimakawa marasa wajen fara tasu sana'ar, za'ayi wanan taro ne ababban hall din transcop hotel, a huta Ipy" daidai nan suka shiga talla kuma, zama tayi ahankali kan gado tai shiru, kwala mata kiran da akayi yasa ta tashi tafita daga dakin da sauri suka daura miya, suna gamawa ta debi nata tafito ta tafi dakin Grandma dinta dake waya hakan yasa tai zamanta tanacin tuwon. Gama wayan Hajiya tayi tace "iyye manyan mata anyi mana girki yau" washe baki tayi tace "grandma abincin nan dadi wlh sosai" hararanta Hajiya tayi tace "nidai tashi kikai plate dinan kitchen ki wuce kije kiyi wanka, haka akeso mace tadinga yi idan tagama aikace aikacen gida ko girki, wuce daganan sai kiyi salla" tashi tayi tadau kwanon tafito saida taje ta ijiye a kitchen sanan takoma dakin ta wanka tayi tanajin dan ciwo ciwon ciki kaman MP dinta zaizo, fitowa tayi ta tsaya gaban madubi ta kalli kanta tawani kara haske fatar jikinta na kyalli sabida man da Hajiya tasaimata mai bala'in kyau ne, tamadanyi kiba, wanan kumburin kukan da idanunta keyi a gidansu duk babu yanzu, gama shafa man tayi batabi takan kalaban kanta dake lilo ba dan batai parking nasu ba tawuce wardrobe dinta wani dogon riga tadauka na kanti mai kyau pitch color ne tasaka kawai ajiki batare datasaka bra ba sanan tasa hijabi tai salla, tana zaune kan dadduma tana biya karatun da aka mata aka kira isha'i tashi tayi tayi sanan tamike tsaye cire hijabin tayi ta ijiye  kan kujera tadauki wayanta dake gaban madubi tawuce tafito, kasa ta sauka, ganin babu kowa a falo yasa tawuce dakin su Razika dake nan akasa, zaune suke su biyun suna assignment dinsu dan malamin su yabasu assignment, suna ganinta duk suna dagokai suna kallonta, murmushi tayi tace "kuma anbaku assignment" dukansu gyadamata kai sukayi, fadawa kan gadonsu tayi tace "to kugama bari nai chatting dasu Aneesa" saida suka gama sanan Razika tarufe book din ta ijiye tana kallon gashinta tace "yaushe zaki kwance kannan gashinan harya soma kwance kanshi sabida gashibki nada santsi" yatsine fuska tayi tace "ni bazan kara zuwa saloon dinan ba suncika kallon mutane wlh" dariya daga Razika har Shemau sukayi dan yanda tai maganan zaka dauka yarinyar ce harda dan turo baki She looks so cute, matsowa gaban gadon Shemau tayi tace "ai sabida kinada kyau ne saisa ake kallonki Du'a mu ana kallonmu ne Razika"? Girgizakai Razika tayi alamun a'a, yatsine fuska Du'a tayi tace "wlh ko bansan kyan nan, uhm, bari naje na kwanta" tai maganan tana tashi daga kan gadon tamike tsaye, hannunta tasa tadauki wayanta sanan ta musu murmushi ganin yanda suke kallonta tace "saida safe" "Allah tashemu Ipy, Du'a gobe kezaki break" bude kofan tayi tajuyo cikeda murna tace "dagaske?" gyadamata kai Razika tayi tace " eh" fita tayi tana murna, Shemau ta kalli Razika tace "Razika daman haka takeda nono ni wlh nadauka breziya ce ke sa nononta yay girma a riga irin push up dinan sai yanzu naganta da ba breziya ajikinta" tashi Razika tayi tana gyara gadonta tace "haka takeda su harda bombom ma kaman ita tai kanta, wlh inason yarinyar sosai Shemau mugun burgeni take, dan she's so simple, batada wani ji da kanta sabida tanada kyau kaman yanda masu kyau keyi dinan kiga suna daddaukema mutane kai sabida sunga sunada kyau, Du'a ga kyau ga kamun kai ga natsuwa bakiga ko saurayi batada shi ba" Gyadamata kai Shemau tayi cikeda  gamsuwa tace "hakane, Allah yabata miji kyakkyawa irinta, ni wlh daurewa kawai nake dabana tsareta da idanu dan wlh bangajiya da kallonta" murmushi Razika tayi tace "bacci nakeji".

Fitowa daga dakin Du'a tayi tana murmushi tana tattaba wayanta dan Aneesa ce kebata dariya tana kawomata karan Mariya waita sace mata zobenta, typing yakuri tayi sanan ta ijiye wayan

kan dinning tawuce tana tafiyan nan ahankali takarasa gaban fridge din dake dinning din tabude dan kishi takeji sosai, wani karamin bottle water mai sanyi taciro tana kallon goran, maida kofan fridge din tayi tarufe kafin ahankali tashiga bude marfin goran sanan takafa ahankali abaki tawani lumshe ido tanasha.

"you know cold water is not good for the body" kaman daga sama taji murya kaman na Sharif akanta, dawani irin sauri tabude idanunta tareda juyowa, yana zaune kan dogon kujera shi kadai a falon yana sanye da 3quater na sojoji da farin t-shirt yana rike da system dake kan cinyanshi, dudda taga ba kallonta yakeba amman saida taji wani irin kunya dasauri ta ijiye ruwan sunnar da kanta kasa tayi amugun kunyace tace "Ya Sharif ina yini" batare daya kalleta ba still yana aikin dayakeyi ne yace "hope u good" gyadamai kai tayi ahankali tama rasa mezata ce tace "uhmm kaga Grandma dina? Tana sama bari nakira maka ita" tai maganan tana fitowa daga dinning tai stairs dasaurinta harda dan gudun ta, wani irin turgudewa tayi kafanta ya lankwashe dayasa tasaki wani irin wawan ihu. "wayyo Allah na kafata" tashi Sharif yayi daga kan kujera dasauri yawaigo daidai lokacin Grandma datagama wayan datakeyi tafito kenan taji ihun ta tazo stairs din dagudu tace "subhanallahi maiya faru? Muga kafan" Hajiya tafadi dasauri tana karban kafan da Du'a takasa ijiyewa kasa tsabagen azaba tana dan kuka mara sauti dan yamugun mata zafi, cikeda tausayinta Hajiya tace "sannu ijiye kafan nagani" gyadamata kai tayi tana kokarin ajiye kafan akasa wani irin ihu tayi saikuma tafashe da kuka sosai wanan karan mai kara tace "dazafi Grandma" cikin dan fushi Hajiya tace " kinsan wajen nan bene ne akan wani dalili zaki dinga gudu akai eh" cikin kuka sosai tana kokarin kama hannun Hajiya dake liliyamata kafan tace "zan kiraki ne naga Yaya Sharif yazo" cikin fada Hajiya tace "Sharif da tuntuni muke tare muna hiranmu har tuwo yaci, sama nazo nayi waya, koma bansan yazo ba gidan nan ba Bakin Sharif bane har sama zai iya zuwa wajena, Sharif zo dan Allah kadubamin kafarta kotasami targade ne, kosu Razika basu kadai ba duk wanda zaizo gidan nan hanashi gudu nake akan bene dan hatsari ne da bene yanzu jibi", karasowa wajen Sharif yayi dawani irin sauri takai hannunta ta share hawayen daya bata fuskanta, Hajiya data matsa gefe tace "au uban kukan dayagamaji kinayi dan yazo nanne zaki wani goge hawaye" turo baki tayi ta dauke kai, Hajiya tace "kaji Sharif dubamin kafan kagani" ahankali yakai yatsunshi biyu yadaura kan kafar datai ja sabida turgudewan yanabin dogayen feet dinta da kallo yace "does it hurt" yadan dagakai yana kallon fuskanta, hadiye zafin tayi tagirgiza mai kai alamun a'a hakan yasa Hajiya tace "kafan dakika gamawa kuka ne kike cewa baya zafi"? Murmushi yadanyi yace "buguwace kawai tashafa man zafi zai daina mata zafi" yay maganan yana sauka kasa abinshi, hararanta Hajiya tayi tace "wuce kije kishafa robb akai Allah kika karamin gudu agidan nan saina saba miki Du'a, kidena guje guje kinji" gyadamata kai tayi ashagwabe tace "tom" "wuce kitafi dakin ki, wani aiki Sharif ketayani yi" gyadamata kai tayi tawuce ta tafi tana tafiya ahankali Hajiya tabita da kallo saida taga tabude daki tashiga sanan tasauko tace "Allah kyauta" karasowa tayi tazauna kusada Sharif tace "wai shi gogan bazaizo yagaidani bane" dariya Sharif yayi yana abinda yakeyi yace "finally kinyi admitting kinyi kewan Asad" hannu tadaga kaman zata dakeshi ya kyalkyace da dariya yace "wlh aiki sosai ne aikin nan dayakeyi shi kanshi yagaji kinsan Asad ya tsani takura shida yasaba saidai yatakurama mutane shi baiso atakuramai Allah Allah yake gobe tayi yagama, da sassafe fa yake fita kullum" murmushi Hajiya tayi tace "Allah sarki Asad, kana ganinshi haka akwai kwazo da zuciya" murmushi Sharif yayi yace "nidai idan yazo kicemai

wlh yafito da mata yay aure inba hakaba dudda ina kanninshi aure abuna ni zanyi na barshi" yay maganan yana batarai, wani irin baki Hajiya tasaki tana kallonshi tace "ohhh jama'a yauni naga takaina, kaiwai mara kunyan inane Sharif, yoo dan kaniyan kama duka duka da wata nawa ya girmeka wata uku ne fa tsakaninku haka Amminku tagayamini, Asad nada wata uku aduniya aka haifoka" dan dariya Sharif yayi yaturo baki cikeda rashin kunya yace "nidai gaskiya nafadi muku aiko Ammi nagayamata ni wlh aure nakeso kuma shi Asad banga alamun ya shirya aure ba Hajiya wlh yaron nan kaman aljani shi yama tsani mata, basa gabanshi the only matan dayakema murmushi yayi hira yay wasa dasu aduka fadin duniyan nan guda biyu ne daga ke sai Ammi, kinsan ko Anty Turai kanwar Abban mu bayama murmushi cewa ma yake he hates her, to ina zan tsaya jiran irin wanan saiyay aure zanyi ai namutu tuzuru hakanan Hajiya wlh a'a" wanan karan hannu Hajiya takai ta dakamai duka abaya dayasa yakusan sakin laptop din yace "aashhh" dauke laptop din tayi tace " naga alama kwana biyu ban jibgeka ba saisa bakada kunya, mugama aikin dakakemin Allah sa ba shirme kakeba dan naga hankalinka baikai" tai maganan tana saka glasses a idanunta tana kanne idanu danta karanta report din daya rubuta mata, karban system din yayi yace "ni dai tsaya na karanta miki natafi gida nai waya da budurwa ta kuma saina gayamata kece duk kika cinye mata time" dariya tayi tace "kagaya mata hala tamadan soka sabida yanda ba'acin kudinka at least ni Kakar ka ina moreka" dariya yayi sosai sanan ya shiga karantamata.....
wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

Free Page
EPISODE 2️⃣4️⃣
yauma kaman kullum suka tashi suna breakfast malamin su yazo ta tafi wajen nata su Razika ma haka, as usual by 1 yatafi, daki takoma ta kunna TV tunani kala kala aranta, wanan sanarwan nan na iya tasake saurara rasa abinda zatayi yasa tabude kofa tafice daga dakin, dakin Hajiya tabude tashiga dake meeting a zoom na retired lawyers, ita kebada report din ga glasses akan idanunta, kallon Du'a dake kallonta tayi hakan yasa Du'a tashigo wani book dake kusada ita tadauka rubutu tamata sanan tabata kallon rubutun Hajiya tayi ta gyadamata kai tareda daukan purse dinta ta zaro 10k tabata, karba tayi tayi cikeda jin dadi tafito daga dakin sanan tasauko kasa da sauri tana murna tai wajen Razika dake dakinsu tace "Grandma tace kirakani saloon jeki shirya nima bari na shirya" gyadamai kai Razika tayi tace "kinbar wayan ki a dinning tun jiya" murmushi tayi tace "zan dauka nasan Su Aneesa ne bari naje na shirya" sama tayi, shiryawa tayi cikin wani black abaya mai kyan gaske, sanan tazauna tai rolling veils dinta dayay

kyau shima ta feffesa turare tafito rikeda handbag, a falo tasami Razika tace "yauwa kin shirya muje to" gyadamata kai Razika tayi suka fice, driver Hajiya ya kwashe su zuwa wani saloon daba na ranan nan ba dantace dagaske bazata wanan ba, tsife mata kalaban akayi sanan aka wanke mata kan sai murmushi take ta kosa agama, gamawa akayi aka mata blowing hair din yabushe tass sanan matan tace "Hajiya wani style za'a miki" dasauri Razika tace "asake mata kalba amman yan kanana kanana this time" dasauri Du'a tace "a'a ayi manya manya" dasauri Razika tace "please amiki kanana Du'a ai tanada sauri" dagakai Du'a tayi takalli matan tace "idan kikai kanana zaki gama kafin 4" kasa magana da kyau matan tayi sabida idanun da Du'a ta zubamata yarinya kaman ita tai kanta. "eh bakice komiba zaki gamamin kafin 4" kasa magana matan tayi sai kawai gyadamata kai datayi murmushi sosai Razika tayi tace "kingani na gayamiki za'a gama, afara to amata mai kyau mai style" fara mata kalaban matan tayi tana mamakin yawan gashin Du'a dakeda tsayi, tsayin shikecin lokaci ma ba asalin kitson ba, wajajen 3 Du'a takalli uban tulin gashinta da ba'ayi ba tace "3 yayi sai yanzu mukai rabi" kallon fuskanta matan tayi ganin Du'a tayi kaman zatai kuka yasa dasauri tace "yakuri gashinki nada tsayi sosai ne gashi robber hair, I am going as fast as I can, zan gama dawuri" gyadamata kai kawai Du'a tayi matan tacigaba da kitson da saurinta, tanaji tana gani 4 yayi ana kan kalaban ba'a gama gamaba sosai taji hawaye yazo mata amman ta daure tahana kanta wuraren 5 matan tagama, tashi tayi tsaye da sauri tana parking kitson da ribbon dinta tadau gyalen ta ta tafa wanan karan batama tsaya rolling ba duka kudin da Hajiya tabata tabama matar sanan takalli Razika tace "muje" tashi Razika tayi suka fito tace "wai ina kike sauri zakije ba gida zamuba" girgixa mata kai tayi suka shiga mota, tace "dan Allah transcorp  hotel zaka kaimu" sanan tajuya takalli Razika tace "program liyafa akeyi na matasa kan fara sana'a tun karfe hudu aka fara" gyadamata kai kawai Razika tayi dan batasan wani program bane ba akeyi ba but yanda taga Du'a tasan it must be something very important to her.

Tunda suka shiga hotel din gabanta ke faduwa sosai parking yayi hakan yasa suka bude suka fito suna kallon kofan dazai sadasu to asalin cikin hotel din da wani security guard dake sanye da uniform ke tsaye yana kallonsu, kallon Du'a dataga ta tsaya sakakau Razika tayi yanda take kalle kalle tace "a ina akeyin abun" dan zaro idanu Du'a tayi irin na asalin wanda doesn't have any idea akan abu tayi tace "nima bansani ba" ganin haka yasa  Razika tadan matso kusada ita murya chan ciki tace "to ki tambayi  wanan security daman gashinan yanata kallonki" dan zaro idanu tayi saikuma tajuya takalli mutumin dake kallonsu har lokacin kafin Du'a tai magana yace "are you here for the program"? Gyadamai kai Du'a tayi batare datai magana ba, yace "to ku shiga hall din ma 8th floor" gyadamai kai tasakeyi sanan tawuce tafara tafiya tana kama hannun Razika suka shiga ciki tare, tunda taji 8th floor yasa tasan akwai elevator hakan yasa sukai hanyar stairs suka farabin bene, da sauri sauri gudu gudu take hawa stairs din, sosai sukai nisa dafa bango Razika tayi tana nishi sosai tace "wayyo Allah na kafana, Du'a nagaji wlh" kaman zata fashe da kuka tace "nima wlh nagaji kinga ankusan gamawa dan Allah muje" tashi Razika tayi tana nishi suka cigaba dabin stairs din ita karan kanta Du'a daurewa tayi kaman kaman kafafunta zasu tsinke, ahaka suka kai floor din tundaga tsayin corridor wajen sukaga mutane sunyi layi hadaddun yammata da maza anyi layi har zuwa hall din da cikin hall din da ake asalin

abun, ganin anbisu da kallo yasa Du'a tabi Razika da kallo saikuma takoma tabayan Razika tana sussunar dakai kaman mara gaskiya dan wani iri takeji idan ana kallonta, murya chan kasa kaman mai whispering tace "Razika tambaya mana inane hall din me akeyi anan" dan Jim Razika tayi saikuma ta kalli wata mata dake tsaye alayi tana sanye da hijabi tace "dan Allah inane hall din" hall din dake gabansu matan ta nuna mata tace "ga hall dinan" ahankali Razika cikeda tausasa murya sabida karta gaji da ita tace "angama ne me kukeyi alayi dayawa haka"? File din dake hannunta matan ta nunama Razika tace "anriga angama liyafan, layin nan kuma na masu son irin su email dinshi ne sanan muna using opportunity din muna submitting CV dinmu akwai possibility na zaiyi recruitment koma baiyiba tunda gwamnati sunsan da zamanshi zaya iya sama mana aiki kingane, long layi ne about 100 people naciki duk sunata bashi kuma ya karba" gyadamata kai Razika tayi tace " nagode sosai, sanan tadan matsa baya still Du'a na labe abayanta tace "kinji ko, ina zamu iya jiran this plenty mutane dasunkai 200, Hajiya tasan kinzo nan" girgixa mata kai tayi alamun a'a, hakan yasa Razika tace "to gaskiya ki wuce mutane tunda anriga angama bazamu kafin akawo kanmu goman dare tayi" gyadamata kai Du'a tayi asanyaye Razika tace "muje" juyawa tayi ahankali suka fara tafiya saikuma ta tsaya Razika takalleta tace "menene?" ahankali tace "I want to say thank u" bata jira amsan Razika ba tawuce wajen da saurinta tai gaban hall din tana sussunnar dakai batai wata wataba kawai ta danna kanta ta kutsa tacikin mutanen dake layi tashiga hall din, tana shiga yan waje sukahau ihu chaaa barinma matan wasu suka biyota ciki ganin haka yasa tawani irin kwasa da gudu dan hall din nada makeken girma sunachan kan stage, dagudu itama Razika tashigo tana kwala mata kira. "Du'a, Du'a, Du'a ina zaki".....

Chak ya tsayar da rubutun dayake ma wata a littafin data bashi, yau yana sanye cikin wani gray suit dayafi na kullum mai kyau, yana zaune yadaura kafa daya kan daya agaban wani hadadden table, both sides dinshi bodyguards ne tsaye rike da gun, sai wasu manyan mutane dake kan stage din suma a zazzaune da suit, tsayar da rubutun chak yayi batare daya dago kanshi ba jin ana ihu da hayaniya a hall din amman suna daya kunnenshi ya iya karba Du'a!

Dawani irin gudu Du'a takaraso gaban hall din daidai inda mutum zai fara hawa yan kirgaggun stairs din dazai sadaka to stage din wanda anan line din yafara duk wanda yazo kanshi xaihau stage ne yaje yasauko, wani irin tsayawa Du'a tayi tana nishi sama sama kaman kirjinta zai fashe sabida gudun datayi tana kallonshi ganin yes yes tabbas shine, daidai lokacin matan dasuka biyota suka karaso cikeda fada sukace. "ke waye dazaki baromu alayi ki gudo ki shigo ciki" juyawa tayi tasake kallonshi cikin muryanta mai shegen zagin nan da dadi dake rawa kuma sabida tsabagen tsoro dakuma gudun datayi tana kallonshi still tace "thank u" duk binta akai da kallo ganin yanda take kallonshi tacemai thank you, wani mutum dakebinta da kallo ne dakekan stage din yace "Pretty lady ki koma kibi layi idan akazo kanki then you now tell him thank u, as it is so many people sun cemai thank you yours is not first kinga he is busy" yanuna mata Asad dayama cigaba da attending to mutane kaman ma baisan something is going on ba, gyadama mutumin kaitayi hawaye na neman zubomata amman ta daure tana kallonshi ahankali tace "thank you for saving my life" daya daga cikin matayen dasuka biyota ne tawani finciketa tace

"dalla malama kizo kifita" dasauri Razika takama hannun matan tace "kisaketa dalla kema ai tafiya zamuyi, muje Du'a" kasa daga kafa daga wajen Du'a tayi tana tsaye kaman an dasata tana kallonshi, muryanta wanan karan narawa sosai hawaye yacika idanunta sosai tace "thank you for saving my life" fincikanta matan tasakeyi hakan yasa Razika tace "malama dalla kisaketa, Du'a let's go" kin motsi Du'a tayi kaman ba ita akeja ba, nan hall din yadau hayaniya, ahankali ya sallami guy din dake gabanshi sanan yajuyo da kanshi ahankali yadaura fararen idanunshi akan na Du'a da akeja taki tafiya tana kallonshi, faduwa gabanta yayi yanda yanda ya kalleta, wani irin yatsine fuska yayi sanan yadauke kanshi daga kanta yajuya yakalli security dake gefen damanshi batare daya kalleta ba yana jiran next person dake kan line yanuna Du'a da yatsanshi a wulakanci yace "fitarmin da yarinyar nan daga hall dinan please and throw her outside this premises".

wanna talk to me no problem just click on this link wa.me/+2347012181461

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

Chat me up directly by clicking on this link wa.me/+2347012181461

✍️ M SHAKUR

Free page

EPISODE 2️⃣5️⃣

amman da jikinshi yahanata fadin bakinshi yakai saitin kunnenta yace "easy Pretty it won't be nice kifadi awajen nan bayan kinyi kyan nan all eyes na kanki" tashi tayi daga jikinshi tayida sauri tanadan murmushin yake tacigaba da manna ma Aneesa kudin data kosa su kare dan tagaji da manna su bata kara yarda ta kalli inda taga Asad ba, daidai lokacin Dad dayaci manyan kaya tareda Ammi suka shigo filin hakan yasa Sharif yaja hannunta gefe da sauri ta kalleshi murmushi yamata yana sakin hannunta yace "lemme dance for the pretty gurl oh yes yimin manni" rawa yahau mata yanabin wakan he looks so cute and funny dayasa tama hau dariya, Mariya ce ta taba Rahima tana nunamata da baki kalli Sharif da Du'a , murmushi tayi bayan ta kallesu tacigaba da rawa abinta,  manni Dad da Ammi sukahau yima Anty Turai, sanan Dad tajuyo zaifarama Aneesa dake taredasu Rahima manni idanunshi suka sauka kan Du'a dake dariya sosai tanama Sharif manni dake mata rawa harda dan tafinta, kallo daya yamata yaganeta dan image dinta yakasa goguwa a memory shi, Sharif dake rawane yalura da kallon da Dad kema Du'a dan yanda yake kallon Du'a ma yasa yakasama Aneesa mannin, dasauri yace "muje ki gaida Dad dinmu Du'a" juyawa takalli Dad dayake nunamata dake kallonta ko kadan bataganeshi ba to ranan ma wani kallonshi tayine, ahankali tace "ina yini" kasa amsa gaisuwan ma Dad yayi sai kallonta dayakeyi hakan yasa Aneesa dasauri tamatso takai bakinta saitin kunnenshi tace "Dad she's my best friend danake gayamaka Du'a jikan Hajiya ce, Dad tanada kyau ko" wani irin washe baki Dad yayi yana kallon Du'a from head to toe yace "sosai ma, I like what I see" yay maganan yanadan cizan lebe, sanan yace "dance for me fine girl namiki manni" yay maganan yana fara mata manni yana wani irin kallonta dayasa Sharif yace "tabar wayanta achan muje ki dauka" baijira amsan taba yaja hannunta suka fitadaga filin suna tafiya Sharif nagaba tana biyedashi abaya Dad  nawani irin binta da kallo kaman wuyanshi zaicire ganin hips masha Allah dominkam Allah yamata ass, curvy and bumpy.

Inda suke dazu suka koma Sharif yajamata kujera ta zauna sanan yazauna kusada ita wani abu namai wato aranshi, daurewa yayi yadanne ya matso kusada ita sosai ahankali yana kallonta yace "Du'a" kallonshi itama tayi tace "uhm" ajiyan zuciya yasauke yasaukar da idanunshi kan fararen hannunta sanan gently yamika hannayenshi biyu yakarbi hannunta yarike dasauri takalleshi, dan murmushi yayi batare daya kalletaba yana kallon hannun yace "sorry nasan na rike hannunki kuma ba kyau I just wanna tell u something ne" yaydan shiru sanan ahankali yace "tun ina dan yaro nakanyi mafarki na auri mace irinki" yaydan shiru sanan ahankali yace "inason mace mai natsuwa da aji, ni namiji ne dako kadan wayan nan wayayyun matan yan gari da sauransu basa burgeni hasalima nafison mace wacce batasan komiba wacce nice zan shayarda ita dadi nakoyamata komi, mai natsuwa mai kyau kamila mai cute smile, ranan dana fara ganinki I saw that kind of lady in you, I love you so m....." tsayarda maganan yayi jin fuskarta akan hannunshi, dasauri yakalleta bacci tayi.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

Not edited
sorry banyi editing this page.

EPISODE4️⃣1️⃣
Zaiyi magana saiga Rahima ta taho wajen tana murmushi tana kallon Sharif irin kallon nan na nasan komi daure fuska yayi tana karasowa gabanshi yace "me" dariya tayi tace "babu naga tayi bacci ne shine zan tadata muje chan dakinmu ta kwanta tunda kasa ce ita" hararanta yayi yace "come amman kibita ahankali please wlh duk kun wahalar da yarinyar nan ita batasaba da gantali irin nakuba" tabe baki Rahima tayi tace "cute Baby alert wlh harna hango d'anda zaku haifa" tai maganan tana tapping fuskar Du'a tana kiran sunanta Du'a, Du'a, bude idanu kadan tayi hakan yasa Rahima tace "tashi muje ciki nima fitsari nakeji" mikewa tsaye tayi dasauri duk cikin bacci tana sosa ido, wayanta Rahima tadauka tace "muje" gaba Rahima tayi hakan yasa Du'a tabiyota abaya ahankali tana tafiya kadan kadan danga bacci gakuma takalmi Sharif yabita da kallo baccin dayagani a idanunta yasa baice mata komi ba, bude kofa sukayi suka shiga falo sama sukayi suna kaiwa dakinsu Rahima kawai fadawa gado tayi ko lafiyayyen 1min batayiba bacci yasakeyin awon gabada ita, itakuma Rahima tawuce bayi fitsari tayi sanan tafito tana kallon yanda Du'a ke bacci ko takalmi ma batacireba tace "Allah sarki Du'a aikam kingaji wanan bacci haka, fitinan Aneesa kadaima yaci kimai baccin nan yau kwana nawa tahana mutanen gidan nan sukuni da shegen birthday dinan" tai maganan tana daura hannu akan switch takashe wutan dakin tawuce tafita sanan tafito ganin Sharif yakoma filin rawa yasa tace "yagama soyewa yakoma rawa kuma" murmushi tayi tawuce wajen itama duk abinda ke faruwa a idanun Abba, ahankali yazame jikinshi yasudade yawuce flat dinsu batare dakowa yalurada shi ba.

Sama yayi dasauri kirjinshi na beating fast fast, direct dakinsu Rahima yayi yabude kofa ahankali kaman barawo, ganin dakin da duhu yasa ahankali yakai hannunshi kan switch din wutan dakin, kunna wutan dakin yayi dakin yay wani haske bau, ganin Du'a kan gado tana bacci yasa da sauri yawani irin waiga baya yana kallon falon saman su jin shiru babu wanda yakenan acikin gidan yasa yamaida kofan yarufe ahankali sanan yasake waigowa, tundaga kan kafafunta dabata cire silver hill dinta ba yake kallo dasukamai bala'in kyau zuwa kafafunta dasuke abude sabida daman rigan bai kaimata har kasaba gashi yanda ta kwanta yasa yadan kwashe gefe sai faran kafanta  ya bayyana harzuwa wajajen bayan gwuiwanta, wani irin lashe miyau bakinshi yayi jikinshi har tsuma yake yace "wanan wace irin danyar yarinya ce haka, yarinya kaman hurun ini, Ya ilahi jibi fata saikace da jinin dawisu take wanka kullum wayyo Allah na gabana" yay maganan yana takawa zuwa gefen gadon yana wani irin kallon fuskanta da gaban riganta dayasa yanayin kwanciyan ta kirjinta yadan fito, wanan karan harwani zazzago harshe waje yayi kaman dan kare yana kallonta baisan lokacin daya mika hannunshi zai

tabatataba yaji anbude kofan dakin dawani irin sauri yakoma baya gabanshi nafaduwa sosai yakalli kofan Asad yagani da headphone makale akanshi hada ido sukayi da mahaifin nashi, saikuma ahankali yajuya yafice dawani irin sauri yace "shitttt nima maiya kaini, na kwafsa wlh" yay maganan dasauri yajuya yafita, ganin Asad zaune kan kujeran falon sama yana daddanna wayanshi yasa yay wajen yasami gefenshi yazauna yana sauke ijiyan zuciya yace "Asad wacece wanchan yarinyar wai nashiga dakinsu Rahima naduba yama sunanshi gorona dan nemanshi nake naganta kwance tana bacci wacece ita" batare daya kalli Baban nashiba yace "I don't know her" dan murmushi yay yace "kai daman dababu ruwanka da yan gidan nan wama zaka sani" yay maganan yana murmushi yana kallonshi ganin Asad ba kulashi zaiyi ba yasa yatashi yay dakinshi daidai Mariya nahayowa falon saman da gudunta, hada ido dasukai da Asad dake mata wani mugun kallo yasata rage gudun murya chan kasa tace "sorry Ya Asad I'm about to pee on my panties ya matse ni" dauke kanshi yayi yace "when u go inside wake that girl ta tafi gidansu" gyadamai kai tayi batare data iya magana ba dan fitsarin ya matseta tawuce tashiga dakinsu tana fitowa tashiga tada Du'a da kyar ta iya tabude idanunta takalli Mariya, Mariya tace "sannu da aiki Du'a wanan ne birthday ko to tashi kutafi gida dare yayi, fara zuwa ki wanke fuskanki" ajiyan zuciya ta sauke cikin bacci sanan ta tashi ahankali zaune takai kusan 2nin ahaka Mariya tace "kefw nake jira" tashi tayida kyar tashiga bayinsu fuskanta ta wanka fuska sanan tafito tana hamma, wayanta da Mariya tadauka tabata tace "muje" tana gaba Mariya na biyeda ita abaya tana sosa idanu tabude kofa tafito, hada idanu tayi da Asad dayasa taji ta turgude tai baya zata fadi dawani irin sauri Mariya tariketa tace "subhanallahi ke Du'a wai haka kikeda bacci karki fadi kiji ciwo fa" tai maganan tana dan turata sabida ta tashi tsaye da kyau, tashi tayi tasauke kanta kasa tawuce tai stairs batare datasake bari sun hada idanu ba.

Har gate dinsu Mariya tarakata sanan tadawo ahankali tabude kofa tashiga falonsu tana tafiya babu kowa falo tariga tasan su Razika sunyi bacci stairs tayi tahau tun kafin takai karshen stairs din takejin muryan Grandma nafada, mamaki abin yabata to dasu Razika take fada, but hardly kaga Grandma nama su Razika fada dan bama su cikamata laifi ba, tun tanajin hayaniya fadanta bata jin maganganun datake tana kaiwa falon sama tasomajin maganganun da kyau. "Muhammad nagayamaka ka kira kanwarka ka shaida mata wlh inhar tazabi mijinta kanni mahaifiyarta dana haifota duniya na shirya na yafe Zainab, tasha min laifi I ignore nahakura I always term abubuwa da kuskuren datakeyi amatsayin soyayya ce tarufe mata idanu but nalura abin mata tsabagen iskanci ne, kagaya mata maganan Du'a tadawo karta karamin shi inba hakaba wlh wlh wlh saina masifaffen bata mata rai"...... iyanan taji kawai taji gabanta na mugun faduwa, tana ganin tunda tazo gidan nan bata tabajin Grandma nafada tana masifa ba sai yau, Du'a tadawo! Du'a tadawo! komarda ita kano za'a sakeyi, nooo jitayi kanta yawani irin buga yasara dasauri tajuya takoma kasa, kitchen ta shiga tadau ruwa tashiga sha dasauri sauri, wani irin shakewa tayi hakan yasa tasaki cup din kasa tana tari sosai tana bubbuga kirjinta, Grandma ta fitowanta daga daki kenan ranta abace jin tari yasa tasauko dagudu tayo dinning gani Du'a a kitchen ta dafa fridge tana tari sosai idanunta sunyi ja yasa tace "subhanallahi sannu sannu, daga shigowanki sai tari Du'a, halan kishi ki kije sosai, sannu ko" tai maganan tana bubbuga bayanta, tsayawa tarin yayi Grandma tace "sannu, iyye daman haka akasha kyau yanmata ko a nunamin aka wani tafi, ya akayi kika dawo naji ba'a gamaba" asgaeabe tacd bacci nakeji,

fuskanta Grandma tashafa tace "jeki kwanta to kinji, amman ki wanke wanan fentin da aka miki kafin ki kwanta kinji yar albarka, Allah yatashemu Ipy" gyadama Grandma kai tayi tana tafiya sama hawaye ya zubo mata Grandma tabi bayanta da kallo cikeda wani irin so dan sosai Du'a tashiga zuciyanta yanda yarinyar nan ta zama happy girl gashi harya making friends bazata taba bari tKoma kangin datake ciki daba wlh.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE 4️⃣2️⃣

Yau dakanta ta tashi da Asuba sabida batama iya tai baccin kirki ba tunda taji wayan da Grandma keyi, koda Grandma tashigo taganta akan dadduma murmushi tayi tawuce tafita daga dakin, tadade kan dadduma sai wajajen 8 tafito da safe, ahankali tabude kofan dakin Grandma ganinta zaune kan gado yasa tashiga ciki tamaida kofa tarufe tana murmushi takarasa wajenta tace "Grandmaaaaa dina, good morning" hararanta Grandma tayi tace "daga zuwa birthday party sai bacci kai Du'a" dariya tayi sosai batace komiba, Grandma tace "oya sauka kasa kiyi kari saikije ki shirya yau malaminki zaizo" sauka tayi dagakan gadon tace " to" juyawa tayi tafita daga dakin, breakfast tayi tanayi tadawo sama sanan tai wanka tashirya 10 nayi malamin ta yazo, hadda tabashi shi karan kanshi malamin yanda yaga takeda kwazo dakuma kokari yasa saida ya yabamata, karfe 1 suka tashi fitowa tayi tana tafiya tun kafin takai falon takejin hayaniya, da Sallama tabude kofa tashiga Ammi tagani tareda Dad da Grandma duk zaune a falo suna hira, suna ganinta duk suka bitada kallo hakan yasa cikeda kunya tadan duka tace "ina yininku"murmushi duk sukamata Ammi tace "har an tashi Du'a" gyadamata kai tayi ahankali, Ammi tace "to Allah bada sa'a, tai sama abinki ki huta" sama Du'a tayi Dad yabita da kallo yace "yanzu wanan yar Zainab ce Hajiya, lallai Allah mai iko, ni inda acema yar Muhammad ce zan iya na'am da abin duba da shi achan kasashen turawa yake, yarinya gatanan jazur kaman balarabiya" murmushi Grandma tayi tace "wlh yar Zainab ce" dan gyaran murya tayi tace "babu abinda yakai kwanciyan hankali da zaman Ipy da iyali Baban Asad, Ammin Su told me everything, Allah ubangiji yamuku albarka Allah yabarku tare" washe baki yayi yana murmushi yace "Alhamdulillah, yanzu sai yan wajenki Asad da Sharif sunakeso yanzu suyi aure" murmushi sosai Grandma tayi tace "zasuyi" sosai sukasha hira, bini bini Dad idanunshi nakan stairs har addu'a yake Du'a ta sauko koya kara ganinta amman bata sauko ba haka wuraren 4 suka tafi.

Monday!

Wuraren 7:49 nasafe tafito ashirye tana sanye dawani bakin abaya plain black mai flowers bakake, saukowa kasa tayi tana rikeda jakanta a hannun, sahun tafiyanta da Grandma dake cin dumamen tuwo taji yasa dasauri tadago kanta ganin yasa tace "Yammatan nawa ne haka har anfito" wani irin murmushi tayi arayuwa ayanzu jitake batada wanda takeso kaman Grandma tace "Grandma nima zanci dumamen" gyara zama tayi tace "Alhamdulillah zokici zanma iya barmiki idan zaki cinye" dariya tayi tasa clean hand dinta tafaraci tana kallon TV dake aiki, Grandma tace "kibar office dinan yau gobe sai ki fara, sai anjima da yamma za'a kawomin abubuwan ki, banson ki saba dokan Asad ne" dasauri tace "yauwa Ammi namaje wajensu Aneesa" hararanta Grandma tayi cikeda wasa tace "sannu uwar yawo angulu" dariya tahauyi Grandma ta harareta tace "ci abinci kafin na makeki awajen nan" dasauri tacigaba dacin tuwon, Grandma dake kallonta tace "su Aneesa suntafi school yau, kema inaso nakira malamin ki na tambayeshi progress dinki, yanamiki su biology da chemistry da kyau ko tunda kince ke science zakiyi" dasauri tace "eh yanayi ina ganesu amman Grandma maths ne kebani wahala da physics but ina ganewa suma" "duk zaki iya ai AbdulFatah ya iya lesson, zan tambaye shi if u can stand ma waec zan biya miki kiyi this year kome kikeso ki zama Du'a inhar ina raye I will help you achieve it" murmushi tayi ahankali tace "Grandma thank you" "now stop talking ki cinye ingani" Grandma tai maganan tana tashi tai kitchen dan ta wanke hannu.....

Akofar Gidan yay parking hakan yasa ahankali tajuyoda kanta takalleshi kaman yanda shima yake kallonta, ajiyan zuciya tasauke ahankali sanan tabude kofan motar tasa kafa tasauko kana ganinta kaga wacce keda damuwa sosai bude gate din gidan tayi tashiga, security zai tsareta tace "please I don't have time for this, wajen mutane gidan nazo" yanda tai magana yasa yakasa cemata komi tashiga, ahankali tai sallama tabude kofan falon tashiga, Dad ne yana sanye da manyan kaya dan fitowan shi kenan zai fita aiki ganin Asad da yanzu ma yashigo side din yazauna a dinning yana hada coffee yasa yay dinning din, jin sallama da bude kofa yasa atare dukansu biyun suka juyo suka kalli kofan, turus Ammi dake saukowa kasa rikeda hulan Dad tayi ta tsaya, cikeda mugun mamaki tace "Zai.....nab....kece ko gizo idanuna kemin" tai maganan tana saukowa da sauri tai hanyar kofa batai watawata ba ta rungume Mami tace "oyoyo saukan yaushe" tai maganan tana sakinta tajuya takalli Dad da Asad tace "Alhaji don't tell me baka gane Zainab ba Yar Hajiya ce Maman Du'a" dawani irin sauri Asad yadago kai yakalleta, tahowa Dad yayi yana murmushi sosai yace "Zainab ido kanga ido dama bakida zamunci" murmushi tayi na dole saikuma hawaye, hannu tasa tagoge hawayen dasauri zatai magana kuma saita fasheda kuka sosai, dawani irin sauri Ammi tarike mata kafada tace "subhanallahi Zainab menene come, sit" tazaunar da ita kan kujera tana kallonta tace "menene" cikin tsananin damuwa tace "Hajiya nazo wajenku ne sabida nasan Mama zataji maganan ku zata saurareku cemin tayi nazo mata gidama bata yafemin ba, mutanen nan sunaso su karbi yarsu Kakan su ta matsa a dawo da ita gida, nama Mama bayani namata namata taki ta fahimceni, i don't know what to do, Baban Du'a ma na waje" dasauri Dad yace "assha maisa baki shigoda shi ba, je dauko mayafinki Wife mutafi wajen Hajiya" gyadamai kai Ammi tayida sauri tawuce tai stairs tana kallon Asad da kanshi ke kasa kaman baimasan me ake afalon ba, ko 1min batayiba tafito, Dad yace "kutaho to" dagata Ammi sukayi suka fice.

Cikin mutunci sosai Dad da Abba suka gaisa sanan yamusu jagora yace "bismillan ku muje" shiga gidan sukayi Abba na gaba, da Sallama yabude kofar falon yashiga, Grandma na zaune kan kujera tasanya glasses dinta a idanu tana aiki a sysyrwm dinta, jin sallama yasa tajuyo, ganin Mami da Abba tareda Dad da Ammi yasa ta ijiye system dinta agefe tamike tsaye zatai magana dasauri Abba ya tsaya agabanta yace "Hajiya aikin daukeni amatsayin danki ko, sanan kina fadi naji, inason sabida ni ki sauraresu dan Allah Hajiya kinji" Mami Hajiya ta kalla da kanta ke kasa takasa hada ido da ita, sai Abba dashima kanshi ke kasa cikeda girmamawa sanan tadauke kanta takalli Dad tace "Baban Asad kasan ina bala'in ganin mutuncin ka and kaman yanda kafadi nadaukeka amatsayin d'ana dan haka listen to me and obey me, kaga mutanen nan biyu" tanuna Abba da Mami tace "inhar maganan Du'a yakawosu gidan nan ai nariga nafadamata awaya, bazan bayarda yarinyar nan ba, Du'a tagama rayuwan datayi agidansu har abada, na gayamata nakuma gayama yayanta Muhammadu yakara sanarda ita bazan bada yarinyar nan ba bazan bayarba" dasauri Ammi ta tashi ganin Hajiya tadauki zafi sosai tace "Hajiya calm down" cikin fushi sosai tace "don't tell me to calm down, sunason yarinyarne suka azabtar da ita, yarinyar dabaya lissafata cikin yaranshi, sun kulle yarinya, Du'a became so depress, sunyi depriving yarinya of her right, na education, bata iya komi an yaa mace ba, bata iya girki ba, yarinya sun maidata doluwa mara wayau, yarinya yar 15yrs yanzu zata iya saida Du'a, sun cutar da Du'a shine yanzu sukeso su dauketa su maidata gida sabida wacce tace akoreta da farko tace yanzu adawo da ita to wlh wlh kura yay kadan afadan giwa" Ammi karan kanta saita taji tsoro tunda take da Hajiya bata taba ganin bacin ranta da bala'intaba sai yau......

Sosai Du'a kejin hayaniya wanda tunda tazo gidan bata tabajin irinshi ba, tashi tayi dagakan gado gabanta nafaduwa hakanan ahankali tabude kofanta muryan Grandma taji dasauri tafito, jin maganganun da Grandma take duk akanta ne yasa tai hanyar stairs din tana tafiya ahankali, hango Mamin ta da Abban ta, da Ammi da Dad, saiga Grandma a tsaye tana masifa sosai yasa taji jikinta yafara rawa, su Mami sunzo su komarda ita, wani irin kuka ne yazo mata dasauri tasa hannu ta toshe bakinta tahana kukan fitowa, saikuma tajuya da gudu tai dakinta kaman mahaukaciya tana wani irin kuka kaman wacce ke hauka, memory gidansu yahau flashing akanta, rawa jikinta yafara sosai tace "no....no oooo" wani irin bude kofan sip tayi jakan goyonta na makaranta sabo da sum sayo ta fizgo kome tagani turawa take ajakan, gyalen abayan dake jikinta tadaura ta yana akanta sanan ta goya jakan tana kuka sosai, fitowa daga dakin tayi tana kalle kalle saikuma tasake komawa dakinta tai wajen window dakin, bude window tayi tana kallon kasa dan abene take, wani irin fashewa tayi da kuka tana goge idanunta da bayan hannu tace "bazan koma gidan nan ba, bazan koma ba, nooo" kawai tahau kan window kaman wanda aljanu suka shiga, runtse ido tayi kawai tai jumping tundaga saman nan har kasa aiko tafado timmm kan grass carpet din dake wajen wani irin bugewa tayi ahannu da kafa amman bata damuba ta tashi tana kuka sosai tana wani irin dingishi tana tafiya da gudu gudu sauri sauri ko kallon maigadinsu batayiba tabude gate tafice, tana fita tawani irin kwasa dagudu rikewa kafanta yayi hakan yasa tai kara, da kyar ta tashi bamatabi takan kakkabe jikinta ba ta kwasa da mugun gudu tana dingishi, Asad da fitowanshi daga Gate kenan da motanshi zashi office lokacin itama tafito ganin tafadi tasake mikewa tana gudu still tana kuka yasa yatabe baki, saka sit belt dinshi yayi ya danna waka yaja motan yana gudu ahankali.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE 4️⃣3️⃣

kafin yakai gate din estate dinsu harta wuce tayi titi tana gudu sosai, fita yayi daga estate din yana jiran traffic light abashi go ahead yawuce, kaman ance yakalli side din left dinshi, ganin yanda take gudu tana dingishi tana kuka sosai yasa yadanyi jim kaman mai tunani, maganan Ammi ne yafadomai rai datamai ranan nan what if kanwar kace su Rahima da Aneesa, yatsine fuska yayi ya karya kwana yaja motan dawani irin mugun gudu, saura kiris yabugeta akan titin hakan yasa ta tsaya chak ganin mota yasha gabanta tana goge hawayen fuskanta tana kallon motan dayake tinted dan bata iya ganin naciki, saukar da glass din motar yayi yana kallonta fuskanshi babu ko alamun strictly yace "get in" girgixa mai kai tayi jikinta ko'ina narawa saikuma tafashe da mugun kuka sosai akan titi tace "dan Allah dan Allah kabarni natafi, Dan Allah Dan Allah Dan Allah narokeka Ya Asad" tunda take bata taba kiran sunanshi ba sai yau, jin yanda ake bugamai horn akan titi yasa azuciye yabude marfin motan dawani irin gudu tajuya zata tafi sabida dingishin datakeyi yasa taku daya yayi ya dauketa tana ihu ko kallon mutanen dake titi baiyiba yabude baya ya jefata ciki yay locking car, sanan yashiga gaba yaja motan dawani irin mugun gudu.

Wani irin mahaukacin kuka take a motan shi kaman yana yankata, takasa shiru, saida yay tafiya mai nisa sosai sanan yakai wani filin kwalo dake kan titi yay kwana ya shiga dan babu kowa ciki, parking motar yayi awani irin zuciye yabude motan yafito yabude bayan motan hannunshi yasa yawani irin fizgota waje sanan yabugata dajikin motan yasaka mata mugun tsawa. "shut up!" ko tari bata karaba gabaki dayan kukan datake daya kusan taushemai kunne hadiyeshi tayi jikinta na bala'in rawa, rasa yanda zatayi yasa kawai saita zube agabanshi tai kneeling looking so helpless and pitiful da zakaji kaman ma kamata kuka, kaman karaman yarinya harwani jiniyan kuka take cikin muryan bala'in tsoron shi tace "Ya Asad dan Allah kayakuri kataimakeni allow me to run, dan Allah Ya Asad karka bari su komar dani kano, dan Allah karka bari su komardani kano, dan Allah dan Allah dan Allah ya Asad dan Allah karka bari su komarda ni kano, dan Allah kataimakeni" yanda take rokonshi jikinta narawa kanta akasa dan tsoron shi ma yahanata ta kalleshi yasa yabitada kallo saikuma yay shiru still kallonta yake, yakai kusan 1min ahaka bazaka taba iya tantance yanayin shi ba yace "stand up" tashi tayi tana sauke ijiyan zuciyan kuka tana kuka, gaba yabude mata yace "shiga ki zauna" shiga tayi batare datai musu ba ta zauna, maida kofan yayi yarufe sanan yazagaya ta side dinshi yabude yashiga yazauna yadade yana kallon filin kwallon yanajin yanda take rera kuka ahankali tana sauke ijiyan zuciya sanan yajuyo ya kalleta yanda riganta yay budu budu duk kasa sabida faduwan datayi, dauke kanshi yayi yamaida gefe yana kallon filin kwallon yace "maisa bakison komawa gida" kaman

jira take tafashe da kuka tace "Abban mu baya sona, Mum bata sona, su Ya Hawwa da Ya Nana duk basa sona, Kakan mu bata sona,Ya Hamad kadai kesona agidan" murya chan kasa batare daya kalleta ba yace "waye Ya Muhsin waye Ya Hamad, maisa kowa baya sonki" gabaki daya tabashi labarin gidansu dudda in a childish way ne but he understood everything, sosai take kuka tace "Ya Asad dan Allah kataimakeni kaji, dan Allah karka bari su Abba su koma dani kano dan Allah kataimakeni" tafashe dawani irin kuka mai tsuma rai tana daura kanta akan cinyoyinta, yakai kusan 2min kallon football field din dasuke ciki yake sanan yajuyoda kanshi wani makirin murmushi yasaki for the first time sanan yace "kinason in taimaka miki"? Dawani irin sauri tadago kanta da jajayen idanunta takalleshi dasuke cikemda hawaye, gyadamaikai tayi ahankali tana goge hawayen da bayan idanunta, yana kallonta still yace "are you sure kinaso na taimaka miki"? gyadamai kai tasakeyi cikin muryan kuka tace "eh" tabe baki yayi sanan yadauke kanshi daga kallonta yace "idan kinaso na taimaka miki dole ki koma gida and face ur father and ur Mum" girgixamai kai tayi wani sabon kuka yana zuwanmata tace "wlh zaku komar dani gidan nan dan Allah Ya Asad kayakuri kataimakeni karsu tafi dani" dan juyoda kanshi yayi yakalleta, zubamata mayun idanunshi yayi dayasa taji tahadiye kukan datakeyi tana kallonshi cikin wani irin murya yace "do you trust me"? hakanan taji idanunshi na compelling nata dan batasan lokacin data gyadamai kai ba tace "eh" ahankali yana kallonta yace "I will help you, I have a plan but dole ki koma" gyadamai kai tayi badan tasoba, juyawa yayi yasa hannunshi abayan yazaro wani rag, jefa mata ajiki yayi yace "first thing first clean ur body" dasauri tadauki tsumman ta goge jikinta tass dashi, wani kalan earpod taga yadauko dabatasan na mene ba, gani tayi yayi connecting nashi to wayanshi sanan yajuyo ya kalleta yace "saukar da this thing kasa" yanuna mata gyalen kanta baki, kallonshi tayi ganin yamaida hankalinshi kan wayanshi da abin daya rike a hannu yasa gently takai hannunta taja gyalen abayan kasa, yan kananun kalabanta suka wani bayyana, ga kwantaccen suman gaban goshinta, juyowa yayi ahankali yakalleta, murya chan kasa yace "come closer" matsowa tayi kusadashi ahankali hartanajin saukan numfashin shi kan fuskanta, dauke idanunshi yayi dagakan fuskanta yadaura kan fararen kunnuwanta, ahankali yadauko abin guda daya yakai kunnenta yasamata aciki yana kallon yanda takeda gashi har akunne a kwance, murya chan kasa yace "the other ear" juyoda kanta tayi fuskanta yataba kafadanshi ajiyan zuciya tasauke, gently yasaka mata sanan yakoma sit dinshi yazauna hakan yasa itama yakoma tazauna, ahankali yace "I will help you, namiki alkawari baza'a tafi dake ko'ina ba inhar u do what I will tell u, idan kuma bakiyiba u are on the own, I have one condition koda wasa karki sake kafadama wani ko wata cewa nine na taimakeki understood" yay maganan yana kallonta dasauri ta gyadamai alamun eh, yace "duk ranan da kika fadima wani what happen ranan nida nataimakeki ni din still zansa amaidaki Kanon" dasauri ta girgizamai kai, kunna mota yayi yaja yace "zanuje yanzu, I will drop u outside zaki shiga direct wajensu zaki ki gaidasu, daganan I will be telling you kome zaki fada musu sanan kome sukace zan baki amsan abinda zaki fada musu, remember say exactly what I said kingane" dasauri tasake gyadamai  gabanta na mugun faduwa dan gani take kaman wayau yake mata, har gaban gidan sanan yakashe motan yajuya yakalleta yace "gyara gyalen karsu hango abun nan, and don't show them any sign cewa magana ake miki a kunne" sake gyadamai kai yayi, ahankali yace "sauka kitafi" kallon fuskanshi tayi hawaye taji zasu zubomata murya chan kasa tace "Ya Asad dan Allah karka bari su tafidani kano dan Allah kataimaka min" yadade yana kallonta kafin ahankali yace "I will help u Du'a, now go, remember kome nafada

miki repeat my words exactly" gyadamai kai tayi tabude kofan tasauka ahankali tabude gate tashiga gida bayan tabar jakanta a motan shi, saida yaga tashiga gida sanan yaja motar shi zuwa gidansu horn yayi aka budemai yay parking awajen parking lot dinsu sanan yay locking motar yana gyara zama ya kara wayanshi saitin bakinshi yanajin sautin karan bude kofan datayi dakuma hayaniya dake tashi afalon.

Binta kowa na falon yayi da kallo, ahankali Grandma da ranta ke abace tace "me kikayi anan" hawayen daya zubomata ta share tana gyara tsayuwanta tanajin maganan da Asad yayi sanan takalli Grandma tace "nazo wajen Abba da Mami ne inason magana dasu" kowa kallonta yake, barinma Dad dako kyafta ido ba yayi yana kara kallon halitta irin na ubangiji Baba baki Mama baka, y'a balarabiya, zama tayi ahankali agabansu ahankali tace "Abba ina kwana, Good morning Mami" anatse Babanta yace "Du'a ya kike? Maganan me zakimin bazaki iya bari anjima ba idan mugama magana da kakanki" girgizamai kai tayi ahankali sanan takalleshi tace "Abba Grandma batada Ipy sosai, banson sabida ni wani abu yasameta" tsareta da ido Abba yayi sanan ahankali yace "okay to ina jinki menene" shiru tayi kusan 2min takasa magana hakan yasa Abba yace "speak up Du'a, yauzan koma kano" bakinta duk suka gani yafara rawa sosai kaman tana kokarin fighting abinda zata fadi, saikuma ta runtse idanu gam kaman daga sama duk sukaji maganan kaman saukan aradu. "Abba ni aure nakeso!" ba Abba kadaiba da Mami har ita Grandma saida tadan jinkirto daga kujera tana kallon Du'a jin maganan daya futo daga bakinta, tadauki kusan 1min idanunta a runtse sanan tabude idanunta ahankali tadago kanta takalli Abba dake kallonta asanyaye murya chan kasa hawaye na taruwa a fuskanta tace "Abba wlh ni aure nakeso, da inkoma Kano gwara nai aure" tai maganan ahankali dayasa Abba kasa koda motsin kirki hakama Mami dasu Ammi daduk ke falon, ahankali Mami tace "Du'a! Aure kikeso?" Tamata tambayan da mugun mamaki, gyadama Maman nata kai tayi ahankali tace "aure nakeso Mami" Abba da yaji ranshi yasosu sosai da kalamanta yace "Du'a kinsan mekike fadi kuwa? Aure kikeso, wazai aureki? wakikeso to ki aura eh"? Wanan karan shirun datayi yamafi nada sosai lips dinta kerawa takasa fadin maganan dake bakinta hakan yasa Abba da ranshi ke abace yadaka mata tsawa yace "I told you I don't have all day I still have to go back to kano yau, wakike so Du'a!" Yasaka mata tsawa dabatasan lokacin da maganan tafito ba. "Ya Asad!" Tai shiru tana wani irin sauke ijiyan zuciya kaman kirjinta zai fito sanan tace "Ya Asad nakeso Abba!" Wani irin kwalalo idanu Dad yayi, Ammi batasan lokacin dawani irin kayataccen murmushi ya kufce mata a labba ba, surprise look Grandma kemata danyau Du'a takasheta da mamaki, Abba dake kallonta yace "waye Ya Asad" ahankali tanuna Ammi tace "ga Babanshi da Maman shi anan" wanan karan saida Grandma itama tai murmushi bama tagama kai karshen murmushin ba tace "Abba dan Allah ka auramin Ya Asad ina sonshi sosai" wanan karan Abba jiyayi duka karfinshi yakare Du'a humiliated him to the core dabaisan lokacin daya dago kanshi ahankali yakalli Dad ba ahankali Akuma natse yace "waye Asad"? hada idanu Grandma da Ammi sukayi kafin Abba yamayi magana Ammi ta mike zumbur dasauri tace "I think har yanzu baitafi office ba, bari naje gida nakirashi kaganshi Baban Du'a" tafita daga falon dasauri batare data jira amsansu ba Abba da kowa na falon yazubama Du'a idanu.

Gida Ammi ta shiga, ganin Ammi yasa Asad yayi kaman irin zai tada motarnan yafita ne dawani irin sauri ta bubbuga kofan motan tace "Asad wait wait" saukar da glass din motar yayi yace "Ammi what is it am late fa office zani" dasauri tace "Asad wait kashe motan kaji I have something very important to tell you, kashe kashe kafito" yanda yaga jikinta narawa yasa ya kashe yafito yana kallonta yace "is everything okay maiya faru Ammi"? Hannunshi takama tarike duka biyun tace "look at me Asad we don't have much time but we will go into deep details later,Asad kasan nina haifeka ko, nai rainon cikinka na haifoka na tarbiyantan dakai zuwa what u are today nataba tambayanka kabiyani ko kasakamin"? dasauri yace "no Ammi" ahankali tace "tom I need u to do something for me, taimako zakayi kuma duk wanda yataimaka ma wani Allah zai taimaka mishi, at this point wata yarinya her life depend on u wlh Asad, please Asad dina, and just know this bazan taba saka kai abu mara kyau ba so u should trust me" kallonta yake kaman wanda bai gane komiba yace "Ammi maizanyi" danshiru tayi kaman wacce ke shakkan fadamai tace "inaso ka auri Du'a jikan Hajiya" dawani irin sauri ya fizge hannunshi yay baya dasauri sauri yace "no way! Ammi, kinsan mekike fadamin kuwa" cikeda damuwa Ammi tabiyoshi hannunshi tasake rikewa tace "Asad bamu da time ana jirana naso dakaine dan girman Allah that's just the only thing I need u kamin right now, any other thing we will discuss it later, at this point kawai u need to save her ne please Asad dan girman Allah idan kana kaunata ni mahaifiyarka, Asad dan darajan Allah karka zubamana kasa a idanu, As......" Ammi! yawani irin kirata da mamaki, cikeda damuwa tace "Asad lemme kneel for u toh halan sainai hakan zakayi" takai gwuiwanta zatasa akasa, dasauri yarike mata hannu yace "Ammi don't kneel for me" kaman zatai kuka tace "Asad I have to kneel for u inhar hakan zaisa kayarda ka taimaken ka auri yarinyar nan nagayama we will discuss d matter later yanzu kawai ina bukatan ka ceci rayuwanta ne inba hakaba tafiya da ita za'ayi, gwara na duka maka Asad na rokeka" tai kaman zatakai gwuiwanta kasa dawani irin sauri yariketa yace "ohhh ohkay Ammi naji basaikin kneeling ba" dasauri ta tashi takalleshi tace "zaka aureta"? Yatsine fuska yayi yace "yes Ammi for now just to save her kuma sabida ke" wani irin ihu Ammi tayi ta rungume shi tana kissing fuskanshi tanamai addu'a kafin taja hannunshi sutafi.

Sallama Ammi tayi tabude kofa tashiga Asad biyeda ita kanshi akasa yana cikin suit din aiki, kallo daya Abba yamai yagane yaron dan yaga program din dayayi na youth a channels television news, zama Asad yayi kanshi akasa anatse yace "ina yini Abba" ahankali Abba yace "Alhamdulillah kaine Asad"? Gyadamai kai yayi ahankali yace "tell me about ur self Asad" danshiru Asad yayi sanan ahankali yace "sunana Asad Abdullahi Kitse, I am 33yrs old, nai karatu a UK inada 2 degree my first degree is medicine I am a Doctor, sai na biyun business Administration, currently yanzu bana aiki as a Doctor, business nakeyi inada company kaina" yay shiru daidai nan, gyadamai kai Abba yayi sanan yadaga kai yakalli Grandma dake kallonshi yace "kin yarda da tarbiyan Asad Mama" gyadamai kai tayi tace "a hannuna Asad ya girma nasan waye Asad, na aminta da tarbiyan yaron nan dari bisa dari" gyadakai Abba yayi babu ko alamun wasa tattare dashi yakalli Asad yace "zaka auri y'ata Du'a Asad"? shiru Asad yayi, ahankali Mami tataba Abba, kabarda hannunta yayi batare daya kalleta ba still yana kallon Asad

yace "zaka auri y'ata Asad"? kaman Asad bazaice komiba har lokacin kanshi akasa ahankali yace "eh zan aureta Abba" gyadakai Abba yayi yakalli agogon dake daure a hannunshi yaja daya saura, dagakai yayi yakalli Dad dakenan azaune kaman ruwa yacishi yace "bismillah mutashi mutafi masallaci, Asad bismillah" tashi Dad yayi, Asad ma yatashi duksu Grandma na kallonsu suka fita daga gidan, suna zaune nan shiru afalo aka tada sallan azahar akayi sai sukaji sanarwa ana adakata jama'a akwai daurin auren da makocinmu Sanata Abdullahi Kitse yakeson ku shaida, kafin kaceme kawai su Grandma sukaji ana an daura aure tsakanin Asad Abdullahi Kitse da Du'a Muhammad akan sadaki dubu dari.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE 4️⃣4️⃣

Ko minti biyu basu karaba sai gasu sun shigo gidan da Sallama, Amsasu Grandma tayi suka shigo, kan Asad akasa kowa yanemi waje yazauna, Abba yadade ahaka sanan yay gyaran murya yace "Du'a" dago kanta tayi ahankali takalleshi, anatse yace "zonan gabana" gyadamai kai tayi ahankali jikinta duk yay sanyi sanan ta rarrafa zuwa gabanshi ta lankwashe kafa, hannunta yakama ahankali yarike yana kallonta yace "Du'a you always feel am unjust towards you, and kinsan wani abu u are right Du'a" Yaydan shiru sanan yace "koma yaya kike u are my daughter and hakkinki ne nakira sunanta cikin yarana so" yadan sakin mata murmushi for the first time tunda yashigo gidan yace "I hope this time around I am just dan namiki abinda kikeso, kince kinason aure kuma amatsayina na mahaifinki na aura miki wanda kikeso wanda Kakarki tayaba da tarbiyanshi bama ita kadai ba ko a masallacin anguwan yanzun nan mutane dayawa sun yaba halin Asad din hakan yakara samin natsuwa hankalina ya kwanta danhaka" yay maganan yana zare hannunshi daya daga rikon dayama hannayenta yatura hannun a aljihu yaciro wrap na sababbin 1k guda daya yadaura akan hannunta yace "ga sadakin kinan Du'a naira dubu dari, Allah ubangiji yamiki albarka" batasan mesa na hakanan taji kuka yazo mata kodan sabida wanan ne karo na farko da Abba kemata magana mai tsayi haka oho amman dai jitayi kuka yazo mata, dagakai Abba yayi yakalli Asad yace "come Son" wani irin murmushi Ammi tayi, ahankali Asad kanshi nakasa yataho gaban Abba shima, hannunshi Abba yakama sanan yadauki na Du'a daya rike yasa asaman nashi yace "ga Y'ata Du'a nan nabaka amananta, ka riketa tsakani da Allah karka cutarmin da ita, ka kulada cinta, shanta, suturanta da lafiyanta dan yanzu duka sun tashi daga kaina ko kan Kakanta sun koma kanka Asad, zuciyata ta aminta dakai dan haka nabar muku ita, yanzun Du'a matarka ce halak malak sai yanda kace sai yanda kace ayi za'ayi dan haka, idan kunso kuyi  biki ko taro duk ba matsala takace Allah ubangiji yamuku albarka, zan koma gida zan sanarda Kakanki tachan cewa na aurar dake zan sanarda yan uwanki, kibi mijinki kimai biyayya Du'a, Allah yamuku albarka" yay maganan yana zare hannunshi dagakan nasu yanadan murmushi sanan yakalli Mami da

idanunta sukai jajir yace "tashi mukama hanyan tafiya" sanan yatashi yakalli Dad dakawai binsu yakeda ido dankomi yafaru akan idanunshi kaman mafarki ne yabashi hannu yace "surukina sai munyi waya, Allah ya tabbatar mana da alkhairinsa" dasauri Dad yatashi yana kakalo murmushi yabashi hannu da fara'a yace "Ameen Ameen, zamuyi waya muje namaka rakiya" gyadamai kai Abba yayi yakalli Grandma dake zaune awajen ahankali cikeda girmamawa yace "kiyakuri Mama dakomi, zamu tafi" dan murmushi tamai tace "babu komi baban Hamad agaidamini da yara dan Allah barinma mijina Hamad" murmushi yayi shida Abba suka wuce suka fice, dakin yarage saura Mami data kasa tashi da Ammi dakuma Grandma dake kallonta, tashi Ammi tayi tadaga Mami ta rungumeta bakinta tadaura akan kunnen Mami tace "I know what u are thinking right now Zainab karki manta nima uwace, but zanmiki wanan alkawarin inhar inada rai Du'a bazata taba wulakanta na, zan kulada ita Asad ma zai kulada ita amana, namiki alkawarin nan Du'a tariga tai miji bazan miki karya ba she is in a good hands I assure u that" wani irin ajiyan zuciya Mami tasauke dan har kasan ranta taji dadin kalaman Ammi kankameta tayi tace "thank u Anty Zainab" sakinta Ammi tayi tace "yima mahaifiyarki sallama" gyadamata kai tayi sanan takarasa wajen Grandma ahankali ta tsugunna, dauke kai Grandma tayi hakan yasa gently tace "Mama kiyakuri kiyafemin kinji dan Allah" juyowa tayi takalli yarta ta ga mamakinta saitaga tasakin mata murmushi takai hannunta kan fuskanta tace "komi yawuce, Du'a tayi aure tana kuma kusa dani danhaka komi yawuce, tashi kitafi tafiyan ku nada nisa" tashi tayi ahankali Sana tajuya zata fice hartakai kofa tadan waigo tasaci kallon Du'a hada idanu sukayi hakan yasa tai sauri tafice Ammi dake murmushi tabita abaya dasauri, Du'a batasan lokacin data cire hannunta dake cikin na Asad ba tawani irin tashi cikeda murna tai kan Grandma tafada jikinta tana wuntsula kafa Grandma basu tafi dani ba wayyooo Allah na wlh dadi nakeji yayyy, tawani irin kankame Grandma da mamaki yagama kasheta tana murna, tashi Asad yayi ta gefen ido yakalleta sanan yay hanyar kofa batare daya kalli Grandma ba yace "bari naje office Grandma" baima jira respond dinta ba yafita daga falon wani irin makirin murmushi yasaki tareda biting lips dinshi ahankali yace "killing two birds with one stone feels good, ranshi fess kaman fresh madara....

Saida Abba da Mami suka wuce amotansu sanan Dad yajuya yakalli  Ammi yace "what have you done dayasa Asad yace yes to this marriage dan nasan Asad ba son yarinyar nan yakeba, mekikayi Zainab" wani irin murmushi Ammi tayi da zuciyanta daya tace "rokonshi nayi, Alhaji Du'a is a very good girl, ga tarbiya gata so calm, bata bude idanu ba, kuma I am sure ko Asad bayasonta now he will grow to love her trust me and zasuyi making a very nice and healthy family, I just made the best decision for him tr........""Malama kimin shiru" Dad yadaka mata tsawa cikeda fushi yace "what kind of nonsense is all this eh? kinzaci aure abin wasane dazaki lallaba yaronki ya auri yarinyar da batama taba burgeshi ba" ahankali Ammi tace "to inda bai aureta da yanzu sun tafi da yarinyar data kara shiga depression haba Alhaji this girl is so innocent da kallonta kadai zaisa mutum yaji bakison anything that will hurt her, Asad save this girl and muna nan dakai zaisota" cikin kunsan rai Dad yace "just stop with this nonsense idan Asad yashigo gidan nan zan tambayeshi dakaina idan bayasonta this night zansa yarubuta saki yabama yarinyar mutane and free her tunkafin wani abu ya shiga tsakanin su" Cikeda lallashi

Ammi takama hannunshi tace "listen Alhaji badanniba dan Allah na yarda idan Asad bayasonta yasaketa but ba da zafi zafi hakaba mutanen nan zasuzo su tafi da ita, adan bari all this heat yalafa tukunna, inhar yasaketa yanzu zasuzo sutafi da ita kano ne that is inma basu maidata kauyen da Mamanshi ke zama ba so please kabar komi ya lafa, dansuma am sure yasami Mamartashi da sauran yan uwanshi kan yama yarinyar aure wani sabon bala'i ne zai barke, amman kaga yanzu da auren nan Asad keda iko da ita kome zasuyi suyi bazasu iya taba tafiya da ita ba kaji" shiru Dad yayi yana kallon Ammi yakuma yarda da maganan ta dan yanzu suna tafiya da yarinyar he stand no chance so dole ya yanke decision din dat is in his interest, kallon Ammin yayi yace "naji bazan sashi yasaketa ba just for now sha sai komi yalafa, my poor boy uwarka tasaka a poor kona" dariya daga Ammi harshi sukayi suna shiga gidansu Ammi tace "he will come around", Dad yace "muje nafadima Turai da kaina nakira Dadda shima nafadamai kafin suji agari" dasauri Ammi tace "wlh amman mubari sai anjima idan ana dinner lokacin kowa na nan, yanzu zokatafi office" gyadamata kai yayi baima shiga cikin gidan ba yashiga mota direban shi yajashi sukatafi Ammi tawuce ciki ranta fess one thing is koma yayane bazata taba bari auren nan ya lalace ba saima tafara tunanin hanyoyin da she will make it work, abubuwan dazaisa danta yaso Du'a sosai.

Gidansu yashigo ranshi fess yaja motanshi yatafi office abinshi.

Saida Asad yafita Grandma taji karan bude gate da fitanshi sanan ta daddage ta dakama Du'a dakekan jikinta duka acinya tace "tashi dan gidanku kidubeni nan" tashi zaune tayi ahankali tana turobaki, Grandma tace "ba asama na barki ba da yaushe kika fita danaga kin shigo ta kofa" turo baki tayi tace "ta window" shiru Grandma tayi tana kallonta anyway bama ta tambayan nan takeba wanan ne most important one ahankali tace "Du'a yaushe kika fara son Asad" sosai take kallon Grandma lips dinta harrawa yake tanaso tafadi mata gaskiya but tana tuna uban kashaidin da Asad yamata, tashi tayi takai hannayenta kan fuskanta tace "ni kunya nakeji" tai stairs da sauri tanadan dingishi, tafi Grandma tayi tace "jama'a yau naga yarinya, agaban kowa tagama cewa tanason yaro, yanzu ni dana tasata agaba ina mata tambayan shine take cemin tanajin kunya ai shikenan" tai maganan tana murmushi wlh bazatai karyaba har cikin ranta taji dadi, tun ranan da Hamad yakawo Du'a data daura idanunta akanta aranta taji zataso tahada Asad da Du'a aure, sai gashi Allah yatayata kome zai faru yafaru she will make sure that this marriage work, kwalama Razika da Shemau kira tayi dasauri suka fito, cikeda fara'a Grandma tace "kuzo inaso na aikeku kasuwa direbana na kaiku ku sayomin sweet da goro, an daurama Du'a aure da Asad dan wajen Ammi yanzun nan mahaifinta a masallaci kutayani murna" gani kawai Grandma tayi sunhau tsalle, Razika tace "Ammi ni duk idan yazo gidan nan dama nakanji inama ace Du'a budurwanshi ne wlh naji dadi" dariya Grandma tayi tace "nima haka, ungo kudin nan kuga kuje ku sayomin narabama jama'an Annabi suci su shaida su sama auren jikata albarka insha Allah mutu karaba, wuce kutafi" karban kudin sukayi, Grandma tadau wayanta takira danta tasanar dashi sanan tashiga kiraye kiraye tana sanarda jama'a.

💫 KYAWUNA JARABTA TA 💫

✍️ M SHAKUR

EPISODE4️⃣5️⃣

Wuraren Magrib suka shigo gidan, motan Sharif ne agaba na Asad biyedashi, suna parking suka fito agurguje sukai alwala anan pampon tsakar gida sanan suka fita zuwa masallaci salla sukayi suna idarwa Sharif yaga sai musabaha akeyi da Asad ana cemai Allah ya sanya alheri Allah ya sanya albarka, tabe baki yayi yace wanan hala yasayama masallacin wani abune, gaba yayi dan yunwa yakeji, Asad din yabiyoshi daga baya, suka shiga gida Sharif yace "muje muci abinci please I am starving" hararan Sharif din yayi hakan Yasa Sharif yaja hannunshi yace "common d more kana gudunma Anty Turai d more tanamaka iskanci idan ta ganka muje jor" janshi falon yayi kowama zaune a dinning harda Dad ganinsu yasa Dad yace "daman ku muke jira let's eat" karasowa sukayi ahankali yace "evening everyone" sanan yaja kujera yazauna Anty Turai ta ballamai harara amman ko kallonta baiyiba, ahankali sukecin abincin jikake tsit babu mai magana ma Aneesa sai satan kallon Asad din take dataga yamata kyau, saida aka gamacin abincin sanan Dad yadau tissue yashare bakinshi yace "nobody should leave the table akwai abinda zan gayamuku listen up" duk gyara zama sukayi suna kallon Dad din banda Asad da yaciro wayanshi yana daddannawa, gyaran murya Dad yayi yace "I believe dukan ku nan kunsan Du'a, Du'a yarinya ce that has been through a whole lot.........nan yabasu labarin Du'a har zuwa dalilin zuwan ta Abuja everyone was shock barinma Sharif dayaga he's a bit closer to him and bata taba gayamai rayuwanta ba, sanan Dad yacigaba yace "yau mahaifinta da mahaifiyarta sunzo........ nan yabasu labarin komi harzuwa inda Du'a tace Asad takeso har aka daura aure har kawowa yanzu" yanda gaban Sharif ke fadi haka na Aneesa kefadi danasu Rahima dan sunsan yanda Sharif keson Du'a, haka kuma sunsan yanda Aneesa keson Asad dudda bata taba fadamusu da bakinta ba, kasa hakura Sharif yayi yajuya yakalli Asad dake daddanna waya abinshi kamanma baisan mesukeyi ba yace "kai kanason ta ne Asad" girgixa mai kai yayi yana tabe baki, cikin yanayin wulakancin nan da halin basarwa irin nashi yace "Ammi made me do it" dukansu juyawa sukayi suna kallon Ammi, dasauri Ammi tabude baki zatai magana Dad yace "yes Ammi ku tasa yay haka but I am in support of hakan datayi inba hakaba tafiya da ita zasuyi maybe ma amaidata kauye, so for now abar maganan aurensu ahaka harzuwa komi yay sanyi ya lafa, auren is not like irin eh aure aure is just to save the girl ass, dazaran komi yalafa Asad zai iya rubuta mata takarda and free the girl idan tasami miji ta auri duk wanda takeso" ahankali da Anty Turai ranta yake a mugun bace tadan saci kallon yarta dake gabda kuka amman daurewa kawai take jitayi ta harzuka sosai tace "maganan banza maganan wopi, wani irin banzan abu kukasa danku yayi eh? Ina ruwanku dawata Du'a ba dangin iya bare na Kaka haduwan Abuja, yar uwanmu ce ko danginmu ne dazakusa yaro ya aureta just to save her, ba kauyeba ko wuta sukakai yarinyar me ruwan mu ba yarsu bace inma sun kasheta ai su suka haifi kayansu, ni dama tun ranan dana fara ganin yarinyar naji bana sonta, nidai wlh inhar da raina banyi accepting auren nan ba so I as much am concern Asad is still very single in my eyes kuma zamu nemamai mata......" tsareta Dad yayi yace "to menene

abin tada jijiyoyin wuya anan Turai eh? Kedai wlh baki raina abin fada, shi yaron kinga yanaso ne"? Cikin fushi tace "wani irin tambaya Yaya kakemin haka? Asad fa namiji ne eh? Inhar yarinya nada nono da duwawu mezai hana kar Asad yasota nan gaba? Anfa riga an daura aure yarinya tazama tashi halak malak, namiji anbashi mumnunan yarinya dabayaso amatsayin mata yadurama yarinya ciki balle kuma anbama Asad mai kama da mayun nan dako yan uwan ta tsoronta suke, ai wlh Asad ya shiga kenan, ni wlh ku masifan batamin rai and nagayamuku I will never ever accept that girl, Yaya sabida rashin mutunci da rashin ganin amfani na ma ace ina gidan nan fa babu inda naje, ni kadaice kanwarka yar uwarka aduniyan nan amman kuje kuyi abu dagakai sai munafukar matarka baku sanar dani ba san......" Tashi Sharif yayi fuuuu yawuce yafita, Turai tabishi da kallo, ahankali Asad dake daddanna wayanshi yatashi yabishi yafice shima, tashi Aneesa tai dagudu tai sama su Rahima da Mariya suka bita sama itakuma Anty Turai tashiga surfafama Dad da Ammi bala'in ta inda take shiga batanan take fitaba Abba yay shiru kaman ruwa yacinyeshi dan he's even confused, ba'a taba trusting namiji da mace shi karan kanshi bazai iya kirga mata munana da bayasonsu yan office dinsu dayaci ba, baya sonsu ko kadan amman saida yacisu balle kuma mai kyau, what if Asad sleep with this girl, what if yama yarinyar nan ciki ga yarinyar da shegen kyau ya zaiyi kenan?.....

